[30/04, 5:37 PM] UMMU  AFAN 🌹: 🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
Bissimillahir Rahmanir Rahim

Ya Allah kamar yadda nafara wannan  novel lafiya kasa nagama lafiya

Wannan novel hakkin ummu afan ne mallakarta ne  kuma banyarda wata ta juyashi zuwa nata book dinba

Dedicated this page to
GORGEOUS WRITERS FORUM😘😘

🌟GORGEOUS WRITERS FORUM🌟

🌟G.W.F🌟

HOME OF GORGEOUS, INTELLIGENT AND EXPERT WRITERS,
WE ARE THE BEST AMONG THE REST

🎗AKWAI LOKACI🎗

🎗 PAGE   1   to  5🎗

Alhaji abubakar dankoli shahararan Dan kasuwa ne Wanda yashahara gida da wajen kasan nan

Allahji abubakar d'an asalin garin Kaduna ne dake zaune a anguwar tudun wada

Ficeccene a duniya duk inda kuke tunani sunan shi yaje

Alhaji abubakar shikadai ne agurin mahaifiyarshi  kuma amma agurin mahaifinsa su goma sha hudune

Mahaifiyarshi amina itace amarya agurin mahaifinsa kuma ita kadai Allah yaba d'a namiji

wannan dalili yasa kishiyoyinta suke mugun matsa mata

Bama iya kishiyoyi ba harda 'yan uwan alhaji abubakar duk ba mai sonta kasancewar Allah yawa Dan uwansu arziki
Kofaduwa yayi yamutu suna da kaso mai tsoka acikin dukiyar tunda bashida da namiji

Sai kuma gashi kwatsam ya auro matarshi ta hudu kuma karamar yarinya tahaihu da namiji

Shikuma alhaji shuaib dankoli yayi murnar samun magaji da yayi

Ranar suna yaci sunan Abubakar

Tunda aka haifi abubakar mahaifiyarsa batada ishashan lafiya

Uwargidanta hajiya suwaiba da maibinta suka je gurin wani hatsabibin boka shine yabasu magani sukasa mata a abinci ranar sunan abubakar

Haka tayi ta fama da ciwo
Abubakar na da shekara daya aduniya Allah yayi wa mahaifiyarsa amina rasuwa

Rikonshi yakoma hanun uwargida hajiya suwaiba

Hajiya suwaiba yaranta biyar mata

Babbar yarta rukaiya sai kannata hudu
Rukayya tadau komai na bakin halin mahaifiyarta

Dan haka kawai itama tadauki tsanar duniyar nan ta daura akan abubakar

Gashi duk yadda zasuyi abubakar yabar duniya sunyi amma Allah yace basu isaba

Cikin tsanani da kunci abubakar ya rayu agidan mahaifinsa

'Yan uwan Alhaji shuaib ma sunfi nuna mishi tsana karara

Bayan shekaru 30 abubakar anzama saurayi kuma mai jini ajika
Mai Neman nakamshi duk da yawan dukiyar mahaifinsa hakan baisa ya nade hannu ba

Yayi karatu sosai inda yakai matsayin babban a karatunsa

Bayanwata biyar da kammala karatun professor abubakar ne

Mahaifinsa ya mishi maganar aure yace ba yanzu ba sai yasamu matar da ta dace dashi

Hajiya suwaiba uwargidan allahji shuaib tasameshi da zancen Yakama ta ya matsawa abubakar akan yayi aure Dan duk abokanshi yanzu suna da matayensu

Alhaji shuaib yace mata tunda yace abashi lokaci abashi mana suwaiba

Ran hajiya suwaiba yabaci tace wallahi alhaji kana bata yaron nan  dayawa yanzu auren ne sai yagada ma zaiyi

Tashi yayi yabata guri Dan baicika San surutuba

Hajiya suwaiba taje tasamu kishiyarta maibinta tafada mata yadda sukayi da allahji akan abubakar

Hajiya larai tace aikema dai wasa kika tsaya
Mai zai hana muje musami baffa kisan shima mafa ba kaunar yaron nan abubakar yake

Sai muji shawarar dazai yanke

Hajiya suwaiba ta amince da shawarar hajiya larai

Sukayi gidan baffa  sunci sa akuwa suka sameshi agida

Nan yazauna bayan sungaisa sukace fada mishi abinda ketafedasu

Yace aikin banza shi shaaibun ne yake daure masa gindin Dan na lura da hakan

amma badamuwa zanyi maganinsu
Zan hada shida hafsat  kunga kenan kawar dashi aduniya bazai mana wuya ba

Cikin jindadi sukace hakan ma yayi  baffa Dan wallahi muddin yaron nan yana gidan nan fa bawani morar dukiyar Dan uwanku zakuyi

Dan komai nashi abubakar yakesawa akai yanzu kamai na kadarorin alhaji abubakar ne jagoransu

Baffa yace nima abin yana damuna

Komai yazo karshe ita wannan yarin hafsa zata gama mana dashi

Nan dai su hajiya suwaiba murna yakamasu

Sukayi sallama sukatafi gida

Bayan kwana biyu baffa yasamu kaninshi alhaji shuaib da maganar hada yaransu auren zumunci

Alhaji shuaib yace abashi lokaci yayi magana da abubakar tukun

Baffa yace lalle ma shuaibu Ashe maganar da mutane suke fada akanka dagaske ne nawan wai yaronka yafi karfinka

Alhaji shuaib yace yaya kenan
Wannan kuma wani maganane na mutane Wanda idan mutum yanajin irin wannan jita jitar bazaiyi abinkashi ba

Baffa yace kwarai kuwa shuaibu dole kanunamin ban isa da kai ba balle danka

Duk abunda kefaruwa akunnen abubakar
Yashiga cikin falon yadurkusa harkasa yace wa babanshi abbu na amince

a aura min wace baffan yakeso abbu dalilina bazanso kasaba wa 'yan uwan kaba Allah yasa haka shine mafi alkari

Alhaji shuaib yace Allah yamaka all albarka  abubakar Allah yarabaka da sharrin duniya da na lahira Allah kuma yakareka daga sharrin mutum da aljan

Abubakar yace ameen abbu
Baffa yace kagani ba Dan naka ma yafika hangen nesa idan bamu hadasu zumunci tun yanzu sai bayan ranmu zasuyi

Alhaji shuaib yace tunda ya amince ai shikenan

acikin yaran nawa
Wacece za ahadsun

Baffa ya wage baki yace hafsatu mana
Alhaji shuaib yace Allah yasanya alkari

Sukace amin

Baffa yace saika shirya kaje kufahimci juna ko abubakar

Abubakar yace insha Allah baffa zanyi kokari naga nasamu lokaci naje

Baffa yace yauwa hakan ma yayi kyau
Yace nizanwuce
Abbu yace tun yanzu yaya

Baffa yace tunda nayi abinda yakawoni zama ai  banawa bane
Abbu yace hakane  kagaida gida yace gida zaiji

Bayan tafiyar baffa abbu yakalli abubakar yace nidai hankali na baikwanta da wannan auren ba abubakar

Abubakar yayi murmushi yace karka damu abbu kasa albarka kawai aciki

Hajiya suwaiba da kishiyarta hajiya larai sunji dadin wannan Abu koba komai idan abubakar yamutu  suna da kaso maitsoka cikin dukiyar alhaji shuaib

Hafsa yarinyace ga baffa kuma itace babbar yarshi

Hafsat kyakkyawace ajin farko Dan danginsu sungaji kyau ne Dan shima Abubakar ba bayaba gurin kyau

Hafsat tana da zafi Dan ita bata son raini ko kannata ba kasafai tafiye  sake musu fuska ba Dan karsu rainata

Ko a school ba mai taka ta barshi  sai dai kuma tana da wani hali Wanda ko agidansu ba asanta

nadashi wato tausayi da son 'yan uwanta

Kwatata bata nunawa dan tasan halin iyayen nata

Lokacin da zancen hadasu aure da Abubakar yazo kunnen ta hafsat tayi murna sosai

amma sai ta bar abinda acinkinta
Ba Wanda ya fahimceta

******
Bayan auren abubakar da hafsat tun abubakar baya kulata irin kyautatawar da take mishi yasa yafara sakin jikinsa da ita

Soyayya sosai suke inda kasan auren soyayya sukayi

Bayan shekara daya da aurensu

Ranar asabar hafsat tana zaune kusa da abubakar tasa mishi ido kawai tana kallonshi yace yadai madam

Tace wallahi dama sonake kabarni naje gida na wuni yau kaga nafi wata banjeba

Abubakar yace shikenan bukatar tace shikenan

Da kanshi yashirya hafsa ma ta shirya suka shiga mota yajasu sai gidansu su hafsat

Suna zuwa yasauketa yabata kudi masu yawa yace tashiga shi sai yazo daukarta zaishiga

Tace Allah yadawo da kai lafiya
Yace ameen matar kirki tayi murmushi tashiga gidansu

Kannanta na murna ga adda hafsat ga adda hafsat tayi murna ita ma da ganinsu

Taci sa akuwa YAU suna da babbar bakuwa wato rukayya babbar yarinyar hajiya suwaiba

Wato yayar abubakar kenan

Nan akagaisa Rukayya tace anya hafsat kina amfani da maganin da akebaki kizubawa abubakar a abinci

Maman hafsat dinta ce nima dai abin yadameni wallahi ace duk wata sai munkashe makudan kudi akan sa munkarbo maganin

amma sai muji sajinkanya kuwa kina yin yadda akesaki kuwa

Hafsat ta zumburo baki tace inayi mana kawai dai shifa yana da addua sosai ajinkinshi Dan infada muku gaskiya ma baicika bacci ba saboda makiyansa

Rukayya tace a lalle wato mune ma makiyansa ko

Ashe bakida kunya hafsat

Hafsat tace kai nifa barin fito muku a mutum ina son mijina

Kuma koda banasonshi bazan taba kashe mutum ba balle ma Dan uwana kuma mijina

Salati sukasa tare da tafa hanu suna salati cikin tsananin kaduwa da maganar hafsat dasukayi

Hafsat batayi aune aune ba taji saukar bugu kota inta

Bakowa bane yake dukanta illa mahaifinta baffa yace ai wanna yarinya da haihuwarki gwamma barinki

Ashe bakya son cigaban mu kinje soyayya ya rufe miki ido ko

Maman ta tace to wallahi ko kiyi abinda mukace ko na tsine miki

Cikin tsananin tashin hankali hafsat tace mama babu biyayya ga aikata sabo

Barin taba aikata abinda kukeso ba sai dai kuhada dani da shi kukashe gaba daya

Nan ma baffa da maman ta suka rufu mata da duka dakyar rukayya takarbeta

aikuwa tana samun anbarta tadauki Jakarta da gudu tabar gidan takal manta a hanu

Tayi bakin titi ta tari keke nafef

Sai gidanta tana shiga tayi dakinta tayi kuka mai isarta kafin

Ta bakanta hakuri takudiri aniyar koza a kasheta bazata barisuyi galaba akan abubakar ba

Takira abubakar tafada mishi ya wuco gida kawai tadawo

Yana zuwa yasameta ba kaman yadda suka rabu ba

Yace meyasameki madam tace bani da lafiya ne shiyasa ma baffa yace na dawo gida

Yace ashsha maza tashi muje asibiti
Tace a a basainaje asibiti ma jikinda sauki yace shidai baiyarda ba

Bata son mishi gardama sosai

Cikin ikon Allah kuwa kitoci sukayi mata tambayoyi

Tayi ta bada na karya
Daga karshe dai suka mata pregnancy test aikuwa aka sameta da ciki na sati hudu

Itakam ma bata sani ba Dan bata laulayi komai

Cikin farinciki abubakar yayi wa Allah godiya

Bayan sundawo gida ne abubakar yatafi hargidansu yafada wa abbu mahaifinsa cewan hafsat na da ciki

Abbu ma yayi murna sosai daga karshe yayi fatan alkairi

Labarin cikin hafsat yabaza ko ina duk dangi asan da cikin dake jikin hafsat

Hajiya suwaiba da kishiyar ce cikin tashin hankali suke tattaunawa

Hajiya suwaiba tace amma larai kinsan baffa ya mugun raina mana wayo

Hajiya larai tace nima nayi tunanin haka kinga  gashi yarinyar zata haihu idan ta haihu musamman akasamu namji fa shikenan kashin mu ya bushe

Shikuwa baffa jika za ahaifar mai kinga koba komai za anfana tanan

Nan dai suma suka hau kulla kullansu

Bayan wata tara hafsat tahaifi danta kyakkyawa namiji fari Sol dashi kaman atsaga jini yafito

Yaro sonkowa kin Wanda yarasa

Ranar suna yaro yaci sunan ABDUL HAKEEM

ana kiransa da HAKEEM

Hakeem yataso cikin soyayyar iyayensa ga wayo ga farinjini

Tako inta Hakeem ya hadu

Mujezuwa taku ummu afan ce

Sai mun hadu a next page

Comments & share 📝📖
[30/04, 5:40 PM] UMMU  AFAN 🌹: 🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN 🎗

DEDICATED THIS PAGE  TO UMMY KHALEEL

🌟GORGEOUS WRITERS FORUM🌟

🌟G.W.F🌟

HOME OF GORGEOUS ,INTELLIGETAND EXPERT WRITERS
WE ARE THE BEST AMONG THE REST

🌟AKWAI LOKACI🌟

PAGE 6 to 10

Please masu karatu karku rikice shuaib shine baban alhaji abubakar

******

BAYAN SHEKARA ASHIRIN
Hakeem yaro Dan kwalisa Wanda yagaji kyau tako ta ina kama daga kan uwa uba dangi da dai sauransu

Duk wani kulla kulla yafaru acikin shekaru ashirin nan
amma Allah bai ba wa makiyan alhaji abubakar nasaran cin galaba akanshi

Tare da gudumawar uwargida ran gida hajiya hafsat
Kwatata taki bada hanyar da za a cutar mata da miji ko danta

Dan yanzu mahaifinta wato baffa ya saduda tunda yaga samu tunda an Haifa mishi jika namiji

Hajiya suwaiba tare da hajiya larai sune basu yarda ba su sai sunga bayan alhaji abubakar da iyalanshi

Yayar alhaji abubakar wato hajiya rukayya itama fa tana nan akan bakanta

Naganin kanin nata yabar duniya da iyalansa

amma hakan ya gagara .

Hajiya hafsat zaune makeken falonta tana duba wani littafin ahalarine

Sai taji sallamar dan nata Hakeem
Tadaga kai ta kalleshi tace Dan albarka yace na am abin alfaharina ki tashi lafiya ,

Hajiya hafsat tace lafiya qalau Dan albarka daman kainake jira kamin dauri akan inda nake jiya

Hakeem yayi murmushi yace da fatan dai d'alibartawa zata kawo hadda
Idan bata kawo hadda ba yau ba dori

Mummyn shi tayi murmushi tace tunda kaga yau baka kirani ba kaima nakejira aikasan nawuce gun

Hakeem yayi murmushi yace a a fa mummy bagirin girin ba tayi mai fa

Mummy tace mai sosai makuwa

Yace muje zuwa inajinki d'alibata
Nan mummy hafsat tafara karatun da ya Dora mata najiya tiryan tirya.

Tana gamawa yace allahuakbar yaufa gaskiya daliba tayi kokari

Nan yaci gaba da Dora mata

Duk abinda suke daddynshi abubakar yana kallonsu cike da sha awa

Dan Allah ya daura mishi son iyalanshi da

Akullum ya kallesu yana godewa wa Allah daya bashi family kaman Wanda yake dashi a yanzu

Yana alfahari da hafsat

Saukowa yayi falon tare da sallama Hakeem yaje ya Rungume dad din nasa

Dan kullum haka suke gaisuwa kaman wasu larabawa

Baban yace Allah yamaka albarka Hakeem

Mummy tace ameen daddyn Hakeem

Nikam ina da tambaya daddyn Hakeem yace inajinki mummyn Hakeem inajinki yi tambayarki

Tace kullum saika tasawa Hakeem albarka Dan wani lokacin sainaji jikina yana sanyi saikace mai bankwana

Alhaji abubakar tayi murmushi manya yace hafsat kenan a duk lokacin da kalli Hakeem inajinsane harcikin raina kullum son d'ana karuwa yake acikin zuciya

Sai nakeganin ba Kalmar da dace dashi sai aduk lokacin da na kalleshi nasamishi albarka

Daddy yace tukun nama badai kishi kike bako
Mummy hafsat tayi murmushi tace kishim ma ai sainayi daddyn Hakeem kafin na haifi Hakeem duk ni kama irin wannan abubawar amma tunda aka haifeshi karage

Komai naka Hakeem

Hakeem yayi dariya yace wato ma d'aliba kishi kike dani ko zamuzo karatu zan fanshe ai

Daddyn Hakeem yayi dariya yace gaskiya kam yakamata kadau mataki

Mummy hafsat tace inkuwa hakane Nima saina dau maki

Nima Baku abinci d'an kadan
Kasan danka da ci kaman gara

Gashi bayacin abincin kowa sai na mummyn shi

Haka dai sukayi ta hira cikin nishadi

Hakeem tun yana shekara shabiyar yagama secondary school

Kuma ashekarar mahaifi sa yakaishi Saudi Arabian karatu ,

Duk shekara Hakeem yake da wowa gida Hutu.

Wannan shekarar ma yadawo ne  har yanasa ran komawa nan da sati daya

Islamic law ne acan saudiya

Karatu yake sosai bakama kafar yaro wancen da wowar dayayi ne yayi service dinshi a Kano
Kafin yakoma Dan hado degree dinsa nabiyu wato   masters

Yanzu yake da shekara ashirin aduniya cas

Hajiya rukayya  yayar alhaji abubakar suna zauna da mahaifiyarta

Tazo gida tace  nikam hajiya maizai hana muhada su Hakeem da laila aure

Kinga dai laila kam kanwar lasa bace  zata iya komai akasata

Hajiya suwaiba tace amma kinsan baza a wa Hakeem aure yanzu bako
Duka duka fa shekararsa ashirin

Kuma  kakansa ya yarda ko babanshi ya yarda kinsanshifa da taurin rai

Dakyar  ya yarda aka aura wa abubakar hafsat

amma Kinga yadda tazama bata jin maganar kowa

Hajiya rukayya tadubi uwartata tace hajiya  tunda kekika rike abubakar ,

Ki aika akira miki shi kinsan shi da biyayya  har kuka kisamishi akan lalle kina son a hada auren laila da Hakeem inyatashi komawa karatu   yatafi da matarshi ,

Kinga idan kika gama kama kafar abubakar na Abba ba maiwuya bane saboda Abba yana son abubakar Kuma yana jin maganar shi ,

Hajiya suwaiba tace naji dadin wannan shawarar taki rukayya
Allah yamiki albarka 'ya mai kishin uwarta ,

Nan hajiya rukayya tace wa uwarta zata wuce gida dan taje tasamu laila tafara gaya mata abinda suke shirin yi .

Alhaji abubakar yana office dinsa na kasuwancinsa dan tunda yayi karatun shima har zama professor Sai yazabi da yayi kasuwanci

Kuma alhamdullila komai yasamu asanshi gida da wajen kasan nan

Yana zaune bayan sun gama meeting yaga kiran matar baban nashi wato hajiya suwaiba
Ta shaida mishi tana son ganinshi
Cikin girmamawa yace insha Allah yanzu zaizo

Wacece Laila
Laila 'ya ce agurin hajiya rukayya yayar alhaji abubakar

Laila ta taso cikin gata ga tabara bairin wacce batayinsa

Laila duk wani halin rashin mutumci takwashe tsaf na uwarta da kakanta hajiya suwaiba

Shekara daya ne a tsakaninsu da Hakeem amma saboda son zuciya irin nasu hajiya suwaiba da 'yarta suke kokarin hadasu aure.

Lokacin da hajiya rukayya tasamu 'yartata da zancen auren Hakeem bakaramin murna tayi saboda Hakeem tun bai kai koina ba billionaire ne

Dan komai na mahaifinsa nasane kowa yashaida hakan so ake kawai
Yagama makaranta adanqa mushi komai a hanunshi shiyasa takesonshi

Dan kudin shi Kuma laila tana ganin akan kudi zata iya komai ciki kuwa harda kissa

Dan haka taba uwarta rukayya goyan baya Dari bisa Dari

Hajiya rukayya tasan dama bazata samu matsala da 'yartata ba sanin halinta datayi"

****

Hajiya suwaiba ta zauna da alhaji abubakar tace tana son taroki wani alfarma agunshi Allah yasa zai iya mata alhaji abubakar yayi murmushi yace haba hajiya kema uwatace Ba alfarma a tsakanin mu Sai umarni ,

Umarni kawai Zaki bani na aiwatar

Cike da jin dadi  hajiya suwaiba tawage baki tace Allah yamaka albarka abubakar

Yace ameen hajiya
Tace daman 'yar uwarkace tace maizai hana kuhada yaranku aure wato Hakeem da laila kaga za adada karfafa zumunci atsakanin mu ko yajagani

Cikin tsananin mamaki   Alhaji abubakar ya kalli hajiya jin abinda tace

Yace hajiya aure fa kikace duka duka Hakeem din gudawa nawa yake yanzu fa yake ashirin hajiya  gwamma ita lailar ta kai amma shifa namiji ne hajiya ai dasauranshi

Hajiya suwaiba tace inbanda abunka baka so muga 'ya'yan jikokinmune ai gwamma tun kan kasa ya rufe mana ido muga munbar baya ana zumunci a tsakani

Tace amma daman shawarane ba umarni dan nasan ban isa nabaka umarni ba  tunda bani na haifeka ba saita fasheda kuka

Cikin tashin hankali Alhaji abubakar yace kiyi hakuri kidaina kuka na amince da bukatarki

Allah yasa haka ne mafi alkairi agaremu baki daya
Tace Allah yamaka albarka abubakar wallahi yadda kake min biyayya ko 'ya'yan Dana Haifa basa min haka

Allah yajikan Amina mahaifiyarka ya haskaka kabarinta

Abubakar yace ameen

Nizan wuce hajiya tace to yaushe zaka samu baban naka da maganar yace badamuwa gobe zandawo

Ya wuce cike da jin tausayin dan nashi a wannan shekarun zai hada damuwar mata akansa ""

Bayan yakoma gida ya huta
Ya ce hajiya ina Hakeem tace aitunda kuka dawo daga isha banganshiba baishigo ba alhaji yace OK namanta

Yana ganawa da wasu committee na gidan marayu

Nisuka zo gani nace yaji abinda suke bukata Sai yafada min

Mummy hafsat tace Allah sarki gaskiya daddyn Hakeem kana kokari Allah yakara budi

Kafin daddy yace wani Abu Hakeem yayi sallama yashigo bayan ya zauna yafada mishi yadda sukayi da committee din marayun

Sai dadddy yace dama inason zamuyi wata magana mudiga uku

Duk suka bada Hankalinsu ga abinda daddy zaice

Nan yafede musu biri har wutsiya

aikuwa Hakeem cikin tashin Hankali yace aure kuma daddy at this age of mine
No impossible Daddy

Mummy hafsat tace kwantar da Hankalinka babu Wanda ya isa maka aure a wannan shekarun

Wallahi basu isaba su samu a damuwa ba
Indai ni hafsat inaraye inkuna nasamu goyon bayan mahaifinka
Ta nuna daddyn da han nunta """

Muje zuwa fans' 😘

Naji dadin comments dinku a first page dina ina alfahari da Ku masoya 🎗️akwai lokaci 🎗️

Please your comments is needed naji comments dinku
[30/04, 5:42 PM] UMMU AFAN 🌹: 🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️
🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️🎗️
BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗️HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN 🎗️

I DEDICATE THIS PAGE TO AKWAI LOKACI FANS'

MUCH LOVE TO YOUR COMMENTS😘😘😘😘😘😘😘

🌟GORGEOUS WRITERS FORUM🌟
🌟 G.W.F🌟

HOME OF GORGEOUS, INTELLIGENT AND EXPERTS WRITERS WE ARE THE BEST AMONG REST.

🎗️AKWAI LOKACI 🎗️

PAGE 11 to 15

Alhaji abubakar yanisa yace abin duk baikaiga haka ba hafsat

Nasanki da biyayya da jin magana ina son kubani goyon bayan akan wannan abun da hajiya takeso

Zata ga kaman dan ba ita ta haifeni bane yasa na kibin umarninta

Hajiya hafsat tace amma alhaji HAKEEM guda nawa yake da za ace wai za amishi aure yanzu

Gaskiya dai nasan wannan auren
Bana Allah da annabi bane auren manufa ne kawai dan sucinmma wani burinsu na daban

Alhaji abubakar yace ina son kidinga kyakkyawar zato akan mutum kuma kisa wa abin albarka a matsayinki na uwa

Kuma ai Hakeem namiji ne ko awani lokaci zai iya kara aure a lokacin dayake bukatar hakan

Wannan kawai kutai maka kubani goyan baya nasamu ladar zumunci

Hajiya hafsat tace amma dai kasan yaya rukayya ba sonka take bako
Tayi hakane dan kawai tasamu hanya ta cucemu

Daddy yace a musu kyakkyawar zato

Shidai Hakeem tunda yasaukar da kansa kasa baisake dagowa ba

Dan yadda yakejin zuciyarsa kaman zata bugs

Hajiya hafsat tace kuma ma arasa yarinyar da za ahadashi da ita Sai wannan Mara kunyar yarinyar da ita kanta yaya rukayyar ma bata barta ba

Alhaji abubakar yace shina mijine ai zai gayrata
Yadda yakeso ta zama

Hakeem dai yace Sai dasafenku

Daddyn yace harzaka bacci son

Hakeem yace a daddy
Ya kalli mummynshi yace  mummy Sai da safe

Tace Allah yatashemu dan albarka

Daddy yace bakace min komai ba zakatafi bacci

Hakeem yace duk abinda kayi dai dai ne kawai daddy bazaka taba umartata akan Abu nakasa yima ba koda kuwa ni banasonshi

Ya wuce yatafi zuwa dakinsa

Alhaji abubakar yace masha Allah
Allah yayi gaskiya kabi iyayenka kaima za a bika

Kinga abinda nayi wa mahaifina nima nawa d'an yadawomun dashi ,

Hajiya hafsat tace hakane daddyn Hakeem gaskiya Allah yabamu d'a nagari fatanmu kawai shine

Allah yarabashi da sharrin makiya .

amma wallahi wannan aure na Hakeem bai kwanta minba kokadan

Haka dai sukayi ta tattaunawa tsakaninsu .

HAKEEM bayan yakoma dakinshi yashiga duniyar tunani yace tabas gaskiyar mummyn shine auren manufa zasuyi ,

Dan yadade da gane 'yan uwan mahaifinsa basa kaunarshi koka dan ,

Inba haka zasuce wai za a hadashi aure da yarinyar da bata da mutunci batada tarbiya ,

Nifa idan asona nane sai nan da shekara goma sha nayi aure ,

Dan sai tsaya na zaba matar da ta dace da rayuwata ,

amma idan tasake tashiga rayuwa ta a yanzu zan nuna mata waye ABBULHAKEEM

zata San koni waye duk wani shige da ficen dangin mahafin nasa yasani sarai

Dan haka yadauki aniyar yiwa mahaifinsa biyayya

Sai zai nuna musu shidin namijine wato dangin mahaifinsa kenan

Haka dai Hakeem yayi ta sake da warwara

Washagari da safe bayan Hakeem yagama break fast ne yadauki phone dinshi yakira Ahmad Abokinsa yace kana inane ahamad yace ganin agida

Hakeem yace OK ganin nan shigowa gidan """"

Ahmad abokin Hakeem kud da kud dan tare sukayu primary da secondary school

Kuma tare sukatafi makaranta a Saudi Arabian tare suke dawowa Hutu ,

Hakeem da Ahmad basa boye wa juna sirrinsu kokadan

Komai nasu tare sukeyi dalilin hakan yasa iyayensu sanin juna har ake zumunci sosai ""

HAKEEM yayi parking a harabar gidansu  Ahmad

Kai tsaye ya wuce part din Ahmad yana shiga yafada kan kujerar falon Ahmad din

Ahmad yace ya man yanaga duk kayi wani iri meyake faruwa ne

Hakeem yaja dogon numfashi yace kaidai bari  man wallahi so ake a hada min zafi agida

Ahmad yace zafi kuma kaman yaya
Ahmad yakwashe komai yafada wa Ahmad

Ahmad yayi dariya sosai yace to ai kai Allah ya kashe yabaka tunkana very young dinka zaka angonce ni wallahi banga  abinda damuwa Ba

Tunda Ahmad yafara magana Hakeem yake kallonshi dan yabashi haushi sosai

Yace wato dariya ma nabaka ko
Ahmad yace dariya kabani mana kaida za ama auren gata

Ahmad yace amma fa ina tausayawa yarinyar saboda by the time din kake cikin samartakarka by then itakuma bayadda takaraji fa dan tazama baba

Hakeem yace kai man har ka mata lissafi kasan  ko yar ten years za abani

Ahmad yace ai nasan baza a tabaka yarinyar da bata wuce goma Ba

Kaga kuwa may be 16 to 17 years haka
Kagakuwa ai kafin nan da wani lokaci tazama mama

Hakeem yace duk ma baka zogunba
Todai yarinyar shekara daya nabata a duniya

Ahmad yace cab wallahi hartabani tausayayi dan nasan bayadda za ayi kazauna da ita kadai a lokacin da samartaka yazo maka

Hakeem yace kaji dan rainin hankali yanzun wanene idan ba saurayin Ba

Ahmad yayi dariya yace sau dai baka kai rayi dinba

Hakeem yadauki trowing pillow ya jefeshi dashi

Yace kaiko nazo nafada maka damuwa ta memakon  kakwantar min da hankali sai kuma bige da da yimin shiririta ko

Ahmad yace to naji abikona yanzu dai kasan  muhimmancin bin umarnin iyayeko dan haka kawai kabi maganar daddy insha Allah komai zaizo dasauki

Ya da amaryar zamuwuce ne Hakeem ya yatsina fuska yace Allah yasauwake natafi da ita akanme

Ahmad yace ya hakuri maida wukar

Yanzu dai katashi mushiga cikin gida kugaisa dasu mummy

Sai muwuce sallar azahar ko dan naga time yayi .

Alhaji abubakar yasamu mahaifinsa alhaji shuaib akan maganar dasukayi da hajiya suwaiba

aikuwa alhaji shuaib yace baisan San zance Ba
Yace waini abubakar sai yaushe za abarka kayi abun kankane

Kai an baka mata batareda son rankaba ka karba sakamokon biyayyar da kayi Allah yasa kadace da mata tagari

Sai kuma yanzu andawo kan danka
Wanda shi ko auren ma bai isaba ance za abashi mata

Hajiya suwaiba tafito daga dakinta tana cewa haba alhaji ai nagani yaran nan fa duk jikokinkane daga ita lailar  har Abdulhakeem din

Idan akayi wannan aure sai munfi kowa farinciki

Kaga ai tuwona maina kenan

Alhaji shuaib yace yanzu Nagano kekika kitsa komai suwaiba

Hajiya suwaiba tace a nice alhaji ganinayi da abubakar da rukayya ai duk 'ya'yanane
To ina laifi dan nace suhada yaransu aure tunda sauran numfashin mu muga hakan

Alhaji shuaib zaiyi magana abubakar yace dan Allah Abba maganar yawuce kawai ka amince kawai da bukatarta

Alhaji shuaib yanisa yace  yanzu Abdulhakeem din ya amince

Abubakar yace namishi magana tunjiya kuma ya amince

Alhaji shuaib yace banyardaba  katuromin shi idan bayason auren ba maiyi mashi dole ..

Bayan kwana biyu Hakeem yayi shiri tsaf ya wuce gidan kaman nasa alhaji shuaib

Yana shiga falon gidan yasamu kakan nasa yana zaune yana kallon sunna TV

Sai yace a a tsoho mairan karfe an kura wa TV ido kaman kanagani da gaske

Alhaji shuaib yace aikuwa dai idona yafinaka naka karfi dan tar nakeganin ka

Hakeem yayi  dariya yace  fadi gaskiya dai kakus

Alhaji shuaib yace yanzu dai Ba wannan
Maganar da kuka yi da mahaifin ka nakeson naji ka amince ne ko baka aminceba idan baka amintaba Ba zanbada goyon baya amaka doleba amma idan ka amince shikenan Allah yasa albarka

Hakeem yayi shiru dan dai kawai yariga yayi wa mahaifinsa alkawarin amincewa ne

Nan yace na amince kakus
Alhaji shuaib yace Allah yasaka albarka

Sannan kuma ina maka albishir da cewan duk lokacin da zuciyarka yabaka kanason auren zabinka kana da dama yin hakan

Dan wannan aure ne kawai na hadi nasu na daban

Harcikin ran Hakeem yaji dadin maganar tsohon yayi wata dariya Allah yakara maka Nisan kwana  kakus dina na kaina kaga irin wacce zanzabo a matsayin mata

Kakan yace Ameen dan albarka Allah yasa muna raye muga wannan rana

Hajiya suwaiba tashiigo taji duk abinda suke fada

Cike da isa tace wa alhaji  shuaib aidai kabari ayi wannan din kafin afara zancen wata

Hakeem ganin shigowar hajiya suwaiba yasa yadaure fuska yakoma Hakeem dinsa

Danshi Sam jinin bai hadu da matar kakan nashi Ba

Ganin haka yasa yace sai anjima kakus zan dawo muyi hira na musamman

Batareda yakalli inda hajiya suwaiba take ba

Yace ina wuni hajiya
Baijira amsawarta Ba yayi hanyar waje

Tabishi da harara tace inan daku ai
Zamu hadu a karo na biyu ne

Laila da mahaifiyarta sunan suna ta murnar samun nasara
Dan ansa sati nan sati daya saboda komawar Hakeem school

Mummyn Hakeem kam batayi wani gayya Ba dan  ita wannan auren ba aure  bane agurinta

Duk lokacin da yakawo matar da zai aura alokacin ne zata yi nata bikin

Zata nunawa dunniya sai a lokacin dan yayi aure

Next page

Your comments is needed fan's😘😘😘😘
Much love to your comments🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
[30/04, 5:46 PM] UMMU  AFAN 🌹: BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN 🎗

I DEDICATE THIS PAGE TO MY LOVELY MOM
MUCH LOVE TO YOU MOM
NO ONE LIKE YOU IN THIS WORLD❤❤❤

🌟GORGEOUS WRITERS FORUM 🌟

🌟G.W.F🌟

HOME OF GORGEOUS, INTELLIGENT AND EXPERTS WRITERS WE ARE THE BEST AMONG THE REST

🎗AKWAI LOKACI 🎗

🎗PAGE 16 to 20🎗

Hajiya suwaiba da hajiya rukayya kadai suke kidansu kuma suke rawar su

Abin yana basu haushi ganin Ba Wanda yake shiri akan bikin
Sai dai dayake suna ganin dazarar anyi auren shikenan

Zuriar alhaji abubakar sundawo hanunsu dan sai yadda suka juyasu

amarya laila ta gayya ci kawayenta sosai dan halartar bikinta

Maman amarya hajiya rukayya ce tazaunar da ita tace wai ke yau saura kwana biyu biki amma baki tambayi shi Hakeem din kudin dazakiyi hidima dasu Ba

Laila tace hmm mama kenan to ina managanshi ballantana har na tambayeshi kudi

Hajiya rukayya tace lalle ma yaron nan ya raina wa mutane hankali amma zai shigo hanunmu ne ai

Yanzu abinda nakeso dake kitashi kidauki kawarki daya tarakaki zuwa gidan su Hakeem din Kikarbo kudin dazakiyi Hidima dasu

Laila tace wannan ma shawara ne mamana yanzu kuwa zan tafi

Haka laila tadauki biky daya daga cikin kawarta taraka zuwa gidan su Hakeem

Laila shiga tayi cikin wasu Riga da wondo parkistan Wanda siririn gyalenta tayafashi akan gashin dokinta dayazubo mata har gadon bayanta

Ga farce da akasa musu duk ita da kawar tata kana ganinsu kasan dai Ba tarbiyya

Laila tana parking cikin gidan su Hakeem tashiga direct zuwa falon gidan
Tana shiga ta tarar da hajiya hafsat mom din Hakeem zaune kan two sitter tana kallon tasharta na MBC 4

Mummy hafsat kawai ganin mutane tayi tsakiyar falo batare da sunyi sallama ba
Tadaga kai takallesu suka hada ido da laila

Laila cikin rashin gaskiya tace mummy ina wuni wallahi banganki bane nazo gurin Abdul Hakeem ne

Mummy hafsat tamusu wani kallon takaici tace  Ku wasu irin marasa tarbiyar yarane dazaku shigo gida  Ba sallama ko haka aka koya muku agidajenku

Cikin in ina laila tace sorry mom please ina  Hakeem yake muna sauri lokaci na kurewa

Cikin tsanin mamaki mummy hafsat take kallonsu laila da suke tsaye kikam kaman andasasu suna karkada jiki

Mummy hafsat tace nikuke wa rashin kunya laila ankuwa fada miki halina
To kikoma kitambayi uwarki wacece ni idan ita ta turoki kimin rashin ni ina dai dai da lokacinku

Kuma kije kifada wa uwarki dan tana yar mijina hakan bazai bata dama  hakan bazai bata damar saku kuzo harcikin gida kuna min dibar albarka Ba
Ita tasan wacece ni niba kanwar lasa bace

aikuwa daga Laila har biky kawarta sun tsorata da yanayin mummy hafsat

Mummy hafsat tace kubace min daga gida yanzun nan insake ganin kafarki agidan nan kiga abinda zaifaru

Da gudu suka fice agidan kuwa harsuna tun tube

Suna zuwa parking space
Zasu shiga mota sai ga motar abdulhakeem  aikuwa Laila washe baki tayi tace biky Gashi nan fa biky tace waw wannan

Zazzafar motar shice

Laila tace kadan ma kika gani indai Hakeem ne kinga zomuje musameshi karyashiga

Hakeem kuwa shida Ahmad ne
Ahmad yace wa Hakeem ya kaman kunyi baki Hakeem yace maikagani

Ahmad yanuna mashi su wurinsu laila
Hakeem yakai idonshi gurin
aikuwa yana ganin sun nufosu yadaure fuska

Ahmad yace kai harda bakin ma zaka nunawa halinka ko
Hakeem dai baice komai

Laila suka karaso gurin su Hakeem din
Sai Ahmad yadan durkusa yace anty ina wuni

Cikin tashin hankali Laila tace wace ce antyn taka
Ahmad yakalleta cikin rashin mahimta danshi yadauka yayar Hakeem ce dangin su

Danshi baitaba sanin laila Ba tunda Hakeem bazuwa yakeba

Abin yaba wa Hakeem dariya amma yaci fuska sosai dan kar laila taga hakorinsa da sunan dariya

Yarufe motarshi ya kalli Ahmad yace mujeko

Laila ta tari gabanshi tace haba Abdul kasanfa  gurinka nazo ko

Hakeem yakalleta ya watsamata wani mummunar kallo yace gurina kikazo namiki me

Abin yaba Laila haushi dan ya tsinkata agaban babbar kawarta

Ta daure tace naga har yanzu baka zo gida munyi maganaba kuma baka kuma tambayeni abinda nake bukata na game da harkar bikinba shine mama tace nazo nakarbi kudin dazan yi hidima dasu

Sai a lokacin Hakeem yayi wani killer smile yace lalle kuwa bazakiyiba
Kikoma gurin wacce ta hada abin sai tabaki
Nikam kwandala ta bazaiyi ciwo akanki Ba

Nan ya wuce ta Ahmad yabi bayansa suka shiga cikin gida

aikuwa da gudu Laila tafada mota
Dan tunda take Ba a taba wulakantata irin wannan Ba

Kawarta biky tayi ta rarrashinta kasa driving tayi biky ce tayi

Hakeem da Ahmad suna shiga falon mummy
Suka ganta zaune kan kujera
Hakeem yasaki murmushi yace mummy na yadai naga kaman antaba minke

Ahmad yanemi guri yazauna yace mummy an wuni lafiya

Cikin fara a mummy hafsat tace lafiya qalau Ahmad ya su hajiyartaka
Ahmad yace lafiya qalau tace zata zo anjima

Mummy hafsat tace aikuwa kaman tasan inason ganinta Allah yakawo ta lafiya

Hakeem yace mummy shine wato kinga Ahmad ina miki magana kina wani basarwa ko

Mummy tayi murmushi tace ai matarka ce taba tamin rai shiyasa

Hakeem yadaure fuska yace daliba zakifara ko

Mummy tayi murmushi takalli Ahmad tace Ahmad katayini da abokinka dan Allah matarshi tazo ta bata min rai dan Allah basai na huce akanshi Ba

Ahmad yayi dariya yace kinyi dai dai mummy

Tace a to kaima kafada dai

Hakeem ya harari Ahmad ya kalli mummy yace daliba bazaki daina kiran wannan Mara kunyar yarinyar da mata ta bako

Mummy hafsat tace toya zamuyi komunki ko munso sai anyi

Nan tabasu labarin yadda sukayi da su Laila dasuka shigo
Hakeem yatashi ya suri key din motarshi  yayi hanyar fita

Mummy hafsat tace dagata dan albarka ina zaka yace mummy kibarni naje naci ubanta  har

tana da gost da zata zo gidan nan tasaki magana haka

Mummy hafsat tace kalesu nima din ai sunsan wacece ni zata je tafada wa uwarta

Zasu sake sabon shiri mu basusan shirinmu yafi nasu  dan muda Allah muka dogara

Hakeem yace wai mummy maiyasa daddy yakasa gane mutanen basa kaunarshi Ba sonshi suke ba fa

Mummy hafsat tace nima abun yana damuna wallahi hakurin mahaifinka yayi yawa wallahi

amma bakomai duk mai hakuri wataran yana tareda riba

Mummy tace kutashi kushiga kuci abinci

Suka tashi zuwa part din  HAKEEM

Suna shiga dariyar dayake cin Ahmad yafito dashi

Yayi sosai Hakeem yace wai kai kuma wakake wa dariya

Ahmad yace wallhi matarka da nacewa anty

Hakeem yace karkasake cewa matana kace kawai matar kaddara

Ahmad yace narki gaskiya man na tausaya ma wannan yarinyar wallahi kokadan wallahi bakuyi marching ba kokadan

Da zanbata shawara data nemi mijinta a wani wajen tabarka

Hakeem yayi dariya yace akai man shine wannan dariya haka amma nima naso nayi dariyar
Dan bakaramin dariya abin yabani ba
Kawai dai banson rainine yasa na make kawai

Ahmad yace oh baruwana fa randa zaka angonce ina ina Dan haka nayishiru Allah yabada zaman lafiya

Tsaki Hakeem yayi yace katashi muje muci lunch idan kuma baka gama surutun ba to

Nan dai sukayi hira amma Rabin hirar tsokanane Ahmad yakewa Hakeem

***

Bayan komawar su Laila gida tana kuka tana bawa mamanta labarin abinda mummyn Hakeem da Hakeem din suka mata

Ran hajiya rukayya yabaci
Tadauki waya takira  uwarta hajiya suwaiba ta fada mata komai abinda Laila tafada mata

Nan itama hajiya suwaiba ranta yabaci tace bakomai ai sunkusa shigowa hanunmu

Tayi hidimarta da kudinta kawai zata fanshe ai

Hajiya ruakayy tace amma hajiya kinsan wallahi bakudi a hanu na sosai

Hajiya suwaiba tace kwantar da hankalinkki
Kituro min ita jikallen sai nabata wasu kudi

Nan hajiya rukayya tayi godiya ga mahaifiyarta kafin takashe wayar takalli 'yartata dake kukan wulakancin da akamata

Tace kidaina kuka kitashi  kitafi gidan  hajiyata zata baki kudi konawane sai kufara hidimarku na kawaye

Nan Laila ta washe baki tace kai Allah yabarmin kakallena yanzu ita zata bani kudin

Hajiya rukayya tace kwarai kuwa aiba abida bazatayi miki ba kece fa jikarta tafarko

Nan dai Laila suka tashi suka tafi karbo kudin """

Ranar daurin aure dasafe  hajiya suwaiba takira alhaji abubakar tace mishi yau daurin aure amma haryanzu basuga  kayan lefe ba

Alhaji abubakar yace ai mun sha afa ne hajiya kaman nawane za a hada lefen dashi

anzo inda takeso tace million biyu sun isa

Alhaji abubakar yayi signing a cheque yabata tace yauwa Allah yayi albarka

Alhaji abubakar yace Ameen hajiya

Nan yatashi yashige wajen mahaiginsa alhaji shuaib

Yanashiga yasameshi yagama shirin daurin auren ne ma

Yace a a abubakar kaine tafe kohar kafito gurin daurin auren ne

Alhaji abubakar yayi murmurshi yace
ai hajiya ce takirani akan maganar kayan lefen Daba akawo ba

Alhaji shuaib yayi dariya yace wargi ma guri yakesamu

Tamin magana nace tawa angon magana shine taki kai dayake sunga kana da hakuri shine suka bita kanka ko

Alhaji abubakar murmushi kawai yayi baice komai ba

Alhaji shuaib yace yadda yaron nan yake yana burgeni suna mugun shakkarsa

Dan ina mata maganar ta tambayi Abdul Hakeem dakanta bakaga yadda ta yiba

Alhaji abubakar yace ai yaron nan nima yana bani mamaki wlh gashi karamin yaro amma koyanzu nasake mishi komai zai riqe sosai

Alhaji  shuaib yace  ai Allah ne yama sakayyar biyayyarka gareni da wannan d'anaka ABDULHAKEEM

Zakayi alfahari da haihuwar Abdul Hakeem saboda kaima nayi alfahari da haihuwarka Allah yajikan mahaifiyarka amina

Alhaji abubakar yace ameen Abba

Nan sukayita hirarsu har lokacin daurin aure yayi suka fita zuwa gurin daurin auren

Hajiya suwaiba ta kira yarta hajiya rukayya tafada mata yadda sukayi da alhaji abubakar

Wani irin ihu hajiya rukayya tayi tacikin waya tace million biyu fa kika ce hajiya

Hajiya suwaiba tace  to meza afasa

Hajiya rukayya tace aikin ki nakyau hajiya ta

Kinga munfara bambara tun yanzu ko

Hajiya suwaiba ta ce kidai bari yarinya dai Allah yakashe yabata

****

Bayan andaura auren  Abdul Hakeem da Laila usman

Daddyn Hakeem ya dawo  gida bayan yazauna
Mummy hafsat takawo mishi abinshi yaci sannan yabata labarin yadda sukayi akan kudin lefe

Mummy hafsat tayi murmushi tace a lalle sun wankeka

Yanzu zasuga kaman shirinsu yafara aiki kenan

Murmushi Daddyn Hakeem yayi yace Hafsat  mata agurin abubakar  maman Abdul Hakeem

Rigimar ki yana bandariya kefa baki yarda dawannan auren bako

Mummy hafsat tayi murmushi tace ai Dana baiyi aureba

Dan banmasan anyiba wallahi kawai dai za aiya kiran aurn da kaddara

Daddyn Hakeem yayi murmushi yace zanso kimishi fatan dacewa kamar yadda nadace dake
Dan ko zabin kaina nayi ba lalle nayi dacen danayi akankiba hafsat

Next page

Your comments is needed fan's 💋💋💋

📖📖📝📝📝
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
[30/04, 5:48 PM] UMMU  AFAN 🌹: BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN 🎗

DEDICATED THIS PAGE TO LOVELY SON AFAN
❤❤❤❤❤❤❤

🌟GORGEOUS WRITERS FORUM🌟

🌟G.W.F🌟

HOME OF GORGEOUS INTELLIGENT AND EXPERTS WRITERS WE ARE THE AMONG THE REST

🌟A KAWAI LOKACI🌟

🌟PAGE 21 to 25 🌟

Ankai amarya Dan kararen part dinta dake gidan su Hakeem .

Mummy hafsat kam a ranar ma gidansu taje wa wuni
Saboda batason damuwa """"

HAKEEM suna zaune shida Ahmad

Ahmad yace kai kasan karfe nawa yanzu katashi muje narakaka dakin amarya fa .

Cikin halin ko inkula Hakeem yace lalle kuwa su amarya manya bari ma kagani

Ya kashe phone din shi ya gyara kwanciyarsa akan bed din Ahmad .

Ahmad yace banganeba mekake nufi badai anan zaka kwana ba

Hakeem yayi banza dashi yayi baccinsa Ahmad yace OK halin ya motsa ko

ai wannan amarya taja wa kanta data waye. Hakeem da bata kanta wahala ba wajen auranka ba

Nan shima yakwanta abinshi Dan yasan duk yadda zaikai  ga magiya Hakeem bazai tashi ba .

Amarya Laila tana ta zuba ido taga ango yashigo shiru kakeji malam yaci shirwa  kawayenta ma sun gaji suntafine

Idonta biyu har wajen karfe uku ba ango
Tadauki waya takira Maman ta Maman tace yadai laila naga kiranki yanzu

Kingane dai yadda akace kiyi anfani da maganin ko karfa kiyi wani abin da zaisa yaki kusantarki kinsan maganin na yau ne kawai

Duk hanyar da zakibi yakusance ki
Kiyi shi karmuyi asara makudan kudaden da muka narkar wajen karboshi

Laila tace yanzu dai dakin tsaya na fada miki abinda zanfada miki

Hajiya rukayya tace inajinki meyafaru

Laila tace haryanzu fa bai shigo gidan ba ma

Cikin tashin hankali hajiya rukayya tace munshiga uku
Yanzu soyake muyi asarar makudan kudaden nan

Ki kirashi a waya mana
Laila tace ina naga numbarsa

Hajiya rukayya tace shikenan munyi asarar kudinmu

Dan malam yace maganin kwana daya yakeyi idan yakusanceki zai zaima rakumi da akala bazaiji maganar kowa ba sai abinda kikace mishi

Kuma zai tsani iyayensa

To gashi Hakan su bai comma ruwaba

Har kuka sai da hajiya rukayya tayi Dan maganin nan naira million daya haka suka caske wa malam

Gashi yanzu wannan Dan ban zan yaron yaja musu asara

Daga laila har uwarta basuyi bacci ba

*********

Washagari  da misalin karfe goma  Hakeem yafito daga wanka daga bathroom din Ahmad

Yashirya cikin wasu kananun kaya sun balain mishi kyau ya fesa turare

Kafin nan yakalli Ahmad da yariga  yashirya Dan yariga Hakeem tashi tunda suka dawo daga sallar asuba shi Hakeem sai yanzu yatashi

Hakeem ya kalleshi yace  yace muje mukarya zanje naga dalibata fa

Ahmad yace to ango muje dining din ko
Suka wuce zuwa dining area na Ahmad

Sukayi break fast
Kafin suka dauki hanyar zuwa gidan su Hakeem

Suna hanya kafin sukai gidan su Hakeem sai daddyn Ahmad yakirashi akan yazo zai aikeshi

Ahmad yace man sauke ni kawai nakoma gida idan na dawo daga aikan dad zan shigo mugaisa da amarya

Hakeem bai kalleshi yajuya da motar yamaida Ahmad gida kafin shikuma yakoma gida yanazuwa yayi parking a gurin parking dinsu """"

Laila tana jin shigowar mota tabude labulen window din ta
ai kuwa taga shine
Harfitowarsa tagani

Yamata kyau kuwa Dan Hakeem mai kyau ne bakarya
Da badan son kudin dayamusu yawaba ai Hakeem miji ne na nuna wa sa a

Hakeem ya kulle motarsa yayi part din mummy
Yanashiga yaga bata falo ya haura  bedroom dinta

aikuwa tana can tana ninkin kayan ta tana jerawa a sif

Yashigo yace assalamualaikum mummy na

Cikin murmushi mummy tace Dan mummy yakake

Dafatan dai katashi lafiya ko

Hakeem yace lafiya qalau daliba kawo kiga ni koma kawai kizauna muyi hira

Mummy hafsat ta nemi gefen bed din ta tazauna

Tsaf Hakeem yagyara wa  mummy kayan ta yasake gyara mata bedroom din kafin yace mummy kinci abinci kuwa

Mummy tayi dariya tace kaima dai tsokanata kake yaushe zankai har wannan time ban ci abinciba ""

Hakeem yayi dariya yace acici
nasan ai dama agurinki na dauko ci

Mummy tayi dariya tace a a nikarka min sharri

Mummy tace ba wannan ba ma
Dama inason magana dakai

Hakeem yadawo da hankalinsa kanta

Tace Dan albarka jiya ba agida ka kwanaba hakane

Hakeem yace hakane mummy a gidansu Ahmad na kwana

Mummy tace ai baka kyauta ba
Tunda anriga andaura dole zamu rungumi kaddara
Yanzu dai Laila tariga zama matarka

Dan haka ina umartarka da karka wulankanta aure

Aure ba abin wasabane duk kuma wani sharrinsu zai koma kansune da izinin Allah bazasu taba tasiri akanmu ba

Hakeem yace ai mummy ki kwatar da Hankalinki adduoi na tsarin jiki ba Wanda bamayi agidan nan dai
Dan haka ba abinda zasu iya mana

Mummy tace Allah yasa Dan albarka acigaba da kula da addua Dan ina tsoron sharrin mutane
""""""

Bayan sun gama magana yace Mum zanje wajen Daddy a office Dan kinsan jibi mukeson dagawa fa Hutu yakare zamuje mutattauna

Mummy tace kadage dai sai katafi ajibinko

To da amaryar zakatafi Hakeem yace Allah yasauwake tayi zamanta ba inda zantafi da ita

Mummy tace bazan maka doleba amma ka tabbatar komai kabari a kafin tafi

Hakeem yace insha Allah mummy

Yace barinje gurin daddyn

Mummy hafsat tace a a kafara shiga kaduba yar mutane tukun ko
Koba komai fa yar uwarkace

Yace to mummy sai na dawo
Tana jin dadin inda Dan nata baya mata musu

Hakeem yashiga part din shi
Direct bedroom din shi yawuce
Yaje yadauko wani file kafin yasake fitowa

Laila kuwa basan shigowarshi ba fitanshi tagani
aikuwa kafin yakarasa fita tasha gabanshi

Yace lafiya kuwa zaki sha gabana haka

Laila cikin yanga tace Haba Abdul ya kake min wasu Abu kaman ba mijina kuma Dan uwana ba

Dan Allah kadawo muzauna kona minti biyar ne .

Hakeem ya watsa mata wani kallo Wanda dakanta tabashi hanya yawuce abinshi zuwa office din dad dinsa

Hankalin Laila yatashi tace anya kuwa wannan
Mutum """

********
Da daddare bayan daddy da Hakeem sundawo sunci abinci can wajen karfe goma
Mummy tace Dan albarka tashi katafi kabar Laila ita kadai

Badan yasoba yamusu sai safe ya wuce part dinsa ,
Yana shiga falon Laila ta na kashe wayarta dasukaga gama da gawarta

Ko kallo bata isheshiba ya wuce abinsa zuwa  bedroom dinsa

Yanashiga wanka yafada

Yana fitowa sukayi ido hudu da Laila cikin wasu arnar kayan bacci wato sleeping dress kenan

Kallo daya yamata yakau da kanshi
Danshi idan ya raina kasuwa ko sauto baya mata

Ya goge jikinsa yashafa mayukansa masu kamshi kafin yasaka night Wear din shi

Ya kwanta tare da kashe wutar dakin  """"""

ai kuwa Laila tafashe da kuka
Tun abin na bashi haushi har yagaji yace dalla malama kitashi kifita min  adaki

Cikin kuka tace Haba Abdul yanzu wannan shine zumuncin da iyayenmu suka hada muyi kenan

Hakeem yayi wani uban tsaki kafin yajuya ya kwanta abinshi

Can tace ai idan kai baka bukatata ni ina bukatarka

Bai kamata kahanani hakkina da Allah yarataya a wuyarka ba """"""

Tabbas yasan hakane kuma mummynshi ma ta mashi tuni akan haka
Koba komai gwamma yafita a hakkinta

Yajuya yace mata damuwarki kenan yasa aka miki aure ko
Kafin tayi magana ya bajadda ita akan bed din

Yacire sleeping dress din nata yayi wurgi da shi bako romance

Sai dai adduar da akeyi lokacin da miji zai sadu da iyalinsa

ai kuwa dai Laila tafada musu

Tagane shayi ruwane

Yanagama abin da zaiyi ya tureta ya kwanta abinshi

Ita kuwa Laila tana cikin farin ciki Dan ita yadda taji din ne kuma bazata iya hakuriba """"""

Kullum zata kawo kan nata indai zai biya mata bukatarta kafin ta shekashi lahira taci dukiya

Nan itama ta kwanta bacci ya dauketa cike da  farincikin kasancewarsu da Hakeem a Daren nan .

Washagari Hakeem kota kanta baiyiba yana gama shirinsa cikin wata yadi mai tsadar gaske iri daya ma sukayi da Ahmad

Yadin ash colour ne sai yasa bakin takalmi da hula Wanda akekira da senator

Duk Wanda yakalli Hakeem sai yasake kallonsa Dan ya hadu iya haduwa

Yana fitowa Laila ta tareshi tace abdul ga break fast dinka fa mai aiki tagama ,

Wani matsiyacin kallo yamata yace kinga nayi miki kama da mai cin abincin masu aiki """

Ban guri nawuce ni
Tabishi da kallo tace aikuwa sai dai idan bazaka ci abinci agidan nan ba Dan ko kwai ban iya soyawa tayi dadi batare da ya kone ba """

Hakeem suna break fast daddy yace mishi
Shi Ahmad din yashirya kuwa Dan naga kaman kai ka matsa kutafi

Hakeem yayi dariya yace bahaka bane dad kasan fa I want to be come professor like you kaga yakamata indage ko dad

Daddyn Hakeem yace hakane but please son take care of your self sosai kaji ko banda harka da mutanen banza """

Mummy tayi murmushi tace kai daddyn Hakeem duk komawarshi school saikayi mishi wannan nasihar yanzu fa babban mutum ne tunda ya ajiye iyali

Daddy yayi murmushi yace wai haka son
Shidai Hakeem baice komaiba

Daddy yace nifa wallhi ina mantawa yarinyar nan tana cikin gidan nan
Ya bara kace tazo akarya da itaba .

Hakeem yace daddy ai tana da mai aikinta har tagama komai sunci abincinsu

Daddy yace duk da hakadai ai itama yar gida ce

Mummy tace kasan alamarin yara sai a hankali
Kawai kabarsu  nan dai mummy ta canja magana

Tace jirgin safe zakubi ko

Abdul Hakeem yace da asuba makuwa mummy tace aikuwa kaman nasani nagama hada ma komai

Mummy Allah yasa kinmin wanna cake din naki medadi

Tace ai duk abinda kasan  ina maka ba abin da na rage

Cikin jin dadi Hakeem yace that's my mom Allah yabar minku iyayena

Daddy da mummy sukace ameen Allah yamaka albarka

Yauma da daddare sai da Laila takai kanta gurin Hakeem

Tun karfe uku yatashi yagama shirinsa tsaf bai Dade da gamawa ba Ahmad ya kira yace man kataho tafa nigani a air port ma

Hakeem yace OK gani nan
Yadauki cheque ya rubuta dubu Dari biyar yasama Laila akan bed
Da kuma short note

Yafita daddy da mummy shi kawai suke jira suka rakashi

Next page
Your comment is needed fan's

📖📖💋📝📝📝
[30/04, 5:49 PM] UMMU  AFAN 🌹: 📖📖💋📝📝📝
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
BISSIMILLAHI RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN🎗

DEDICATE THIS PAGE TO MY ONE AND ONLY HUSBAND
ABU AFAN (DOCTOR SULEIMAN)❤💋

🌟GORGEOUS WRITERS  FORUM🌟

🌟G.W.F🌟

HOME OF GORGEOUS INTELLIGENT AND EXPAERT WRITER'S WE ARE THE BEST AMONG THE REST

🌟AKWAI  LOKACI🌟

🌟PAGE  26 to 30 🌟

Laila ta tayi taga ba Hakeem
Sai ta tashi tashiga tayi wanka tana fitowa idonta yakai kan takardar da ya ajiye mata

Tadauka ta duba taga cheque ne na kudi """"

Nan da tawashe baki tace kai tun yanzu bata gama rufe baki ba taga wani guntun takarda .

Tadauka taduba
Cewa yayi Nina wuce ga kudi nan

Idan kina bukatar wani Abu zaki iya samun mummy

Laila na gama karantawa ta wurgi da takardar tace kutuman uba Ashe tafiya yayi yabarni anan ,

Nida nake ta burin tafiya Saudi
Ashe ma badani zaitafiba """

Tadauki wayarta takira hajiya rukayya
Tanadawa Laila tafashe da kuka

Hajiya rukayya tace Lafiya kike kuka Laila cikin kukan Laila tace mama kinsan
Abdul Hakeem yakoma Saudi yau """

Maman tace yakoma fa kika ce
Lalle ma yaron nan wato badake zai wuce ba kenan """"

Laila tace ai niban Masan yatafi ba rubuta min yayi
amma yabarmin dubu dari biyar yace kuma idan ina bukatar wani Abu na sami mummynshi ,

Hajiya rukayya tace aikuwa sun ja wa Kansu
Nan da jibi kice kina bukatar kudi
Kinga sai musamu mufara shiri kafin yadawo ,

Laila tace to mama wallahi amma naji haushin rashin tafiya dani din nan dayayi ,

Hajiya rukayya tace kwantar da hankalinki zai dawo ne ai zai shigo hanunmu daga shi har iyayensa .

Yanzu zanzo gidan naki nakarbi kudin na ajiye su a wajena

ai gwamma ma da yatafi abinsa kinga matara kafin yashigo hanu mu kawar dashi banza""""

******
Bayan kwana biyu Laila taje gidansu daga nan itada mahaifiyarta suka wuce gidan hajiya suwaiba wato kakan Laila kenan ,

Suna isa hajiya suwaiba takira hajiya larai kishiyar suka shige can dakin hajiya suwaiba Laila ta kwantar da kanta  akan cinyar kakarta

Nan hajiya rukayya tafada musu komai  abin da Hakeem ya ma Laila

Hajiya suwaiba tashafa kan rukayya tace hakuri kinji jikalle zai shigo hanun mu ne kinji ko ,

Dazaran yashigo hanun mu sai yadda kikayi dashi kinji ko
Cikin jin dadi Laila tace Allah yasa haka kakalle na

Dakuwa kinga gata Dan sai na canja  maki gida kekadai basai da wannan tsohon ba

Hajiya rukayya tace a lalle ma uban nawa ko

Hajiya larai tace Dana dashi aka ware

Hajiya suwaiba tace a dinta ji anwarekun

Nan dai suka ta kulla tsiya

Sai can wajen karfe goma na dare kafin Laila ta tashi tayi hanyar gida
Dan dama ita tasaba da driving din dare ,

tana shiga maigadi yabude mata gate din yana gaisheta ko ta amsa mai .

Tana parking sai daddyn Hakeem yafito yace Laila daga ina a wannan Daren haka
Laila tace daddy daga gidansu alhaji nake a can na wuni .

Daddy yagane wani alhaji take nufi wato alhajinsa,
Yace kin tabbata tace a daddy kakira ma katambaya

Yace a a shikenan karkisake kai dare a waje haka kinji ko tace naji Daddy

Yace maza wuce dakin kin dare yayi
Namishi saida safe

Tana shiga falonta tayi wurgi da gyalenta tace nifa bana son sa ido haka kawai mutum yafita amma ana gadinsa

*****
Bayan wata biyu Laila ce kwace cikin lallausar kujerun falon Hakeem tana kallo
Sai tafara jin tashin zuciya

Ta tashi tayi hanyar bathroom tafara amai sosai take amai kaman zata fitar da kayan cikin ta

Kanwarta suby wacce taci sunan hajiya suwaiba ce tazo
Tana ta sallama amma shiru
Dan tunda Hakeem ya tafi suby tadawo gidan gurin yarta ,

Itama dai duk halin nasu dayane da yaruwarta

Taje siyo wa Laila balangune a bakin titi

Taduba bedroom din Laila bata ganta ba  tace anty Laila da karfi

Can ta duba bathroom din falon Hakeem aikuwa nan taganta tayi sharaf ,

aikuwa suby ta rude ganin yar uwar tata a kasa jiki ba karfi tadauki waya takira uwarsu hajiya rukayya tafada mata tace gatanan zuwa

Can dai taga karfa Laila ta mutu Dan haka sai ta
Tashi tayi hanyar part din mom din Hakeem

Mummy hafsat tana kitchen Dan daura abincin rana sai taga suby kaman anjifota

Tace lafiya kuwa suwaiba  zakishigo ba sallama
Suwaiba tace kiyi hakuri mummy anty laila ce balafiya ,

Mummy hafsat tace meyasameta tace wallahi bansaniba nima naje aika kafin nadawo nasameta a haka

Mummyn Hakeem tace wace muje naganta
Wannan shine farkon shigowar mummy hafsat part din Dan nata

Kusan atare suka iso da Maman su Lalai hajiya rukayya

Mummy  hafsat tace a  a yaya ashekema kinzo

Hajiya rukayya tace a gani nan ai

Mummy hafsat tace bara na dauko mota akaita asibiti ko

Hajiya rukayya tace duk yadda kikayi

Mummy hafsat tace afito da ita mutafi ko

Hajiya rukayya ta kalli mummy hafsat wato ita bazata kamata afita da ita ba sai dai tabasu command

Hajiya rukayya da suby suka kama Laila zuwa mota

Mummy hafsat ita taja motar zuwa hospital

Bayan gwaje gwajen da aka wa Laila likita yagano tana da cikin wata biyu

aikuwa hajiya rukayya da suby dama ita kanta Lailar  murna suka hauyi sosai ko kunyar mummy hafsat basaji

Itadai mummy hafsat tunda doctor yace Laila cikine da ita

Bata ce komai ba tausayi kawai danta yabata hada zuria da irin hajiya suwaiba

Nan dai tana ta tunanin zuci

Hajiya rukayya tace hafsat bakice komai ba zamuyi jika mummy hafsat tayi murmushi kawai tace Allah yaraba lafiya

Yanzu dai bari na sami doctor nabiya komai sai muzo muwuce gida

Hajiya rukayya tace ai inaganin zan wuce da ita gida kawai idan tasamu lafiya sai ta koma dakinta

Mummy hafsat tace badamuwa hakan ma yayi zama Ku iya  bari saita haihu sata dawo

Hajiya rukayya maganar mummy  hafsat yamata zafi sosai  wato subasa ma bukatar zaman Lailar agidan kenan

Hajiya rukayya tace tokuma idan mijinta yadawo fa

Mummy hafsat tayi dariya tace ai daga har ta haihu son bazai sami damar zuwa ba

Hajiya rukayya tace duk karatun ne zaisa yaki dawowa gida

ai yanzu idan kika kirashi kikafada mishi zai iya samin lokaci yazo yaga matarahi kafin yakoma ko

Mummy hafsat tace sai dai nabaku numbar nashi   ita lailar saita kira tafada mishi

Cike da jin haushi hajiya rukayya tace ai ashikenan takira tafada mishi da kanta

Mummy hafsat tace dayafi dai bara na biya kudin nazo mutafi ko

Hajiya rukayya tace a a kibarshi kawai driver na zaizo yanzu yamaida mu gida

Mummy hafsat tace to Allah yabata lafiya ni na wuce

Laila tayi saurin cewa mummy baki bani numbar abdulhakeem dinba

Mummy tace OK kawa wayar taki na samiki

Laila Tamika wa mummy hafsat wayar
Nan tasamata numbar HAKEEM

Laila tace thanks mom

Mummy Hakeem tawuce abinta

aikuwa tana fita hajiya rukayya tace zanyi maganinkine

Muza ayi wa wulakanci duk abin mutaum dai
Ciki dai sai an haife shi tsaf

Ta kalli Laila tace kekuma harda wani godiya Dan anbaki numbar mijinki

Suby tayi dariya tace kai mama kaman Bakisan halin anty Laila ba
Tasan metakeyi fa

Laila tayi dariya tace Haba mama anfada miki Dan Allah nayi godiyar caf

Nan dai sukayi gidan hajiya suwaiba suka shaida mata abin farin

aikuwa harda gud'a hajiya suwaiba tayi Dan murna tace kaman muzuba ruwa a kasa musha Dan dadi

Hajiya rukayya tace kinga  yanzu saimuyi addua ta haifi namiji Dan mukasa mutsare gidan

aikuwa hajiya suwaiba tace ai namijin ne ma zata Haifa kuzuba ido kugani

ai tunada wuri zamuje gurin malamin nan yabamu taimako

Haka dai sukulla wannan su kulla wancan

*****

Mummy hafsat bayan daddy ya dawo gida  ta shaida mishi  abin dake faruwa

Daddyn Hakeem yace kai amma naji dadi Allah yaraba lafiya

Kice son dina yagirma fa
Harda da d'a

Mummy dai bata ce komai ba
Yace ai sai a tura musu kudin dazai ishesu kula da ita abin da kecikinta

Mummy hafsat tayi murmushi tace hakane

Nan daddy  yakira yayarshi wato hajiya rukayya  maman laila

Tana ganin kiran daddyn Hakeem tasan sunwarke Dan tasan zai jikasu da kudi

Nan da nan tadaga wayar daddyn Hakeem yafara gaisheta kafin yace yaji abin farinciki Allah yaraba lafiya

Sannan kuma inason kuturo da account number dazanturo muku da abinda zatayi anfani dashi aikuwa farinciki Yakama hajiya rukayya tace yanzu kuwa zanturo
angode fa Allah yakara arziki

Tunda yake bai taba jinta tamishi godiya ba sai yau yace bakomai
Mudai fatanmu dai Allah yarabasu lafiya

Ameen hajiya rukayya tace takashe wayar nan da nan taba wa suby wayar tace ta tura wa daddyn Hakeem account number din Laila

aikuwa suby bata Dade da turawaba sukaji alert din dubu Dari takwas  cas

aikuwa murna awajen su kaman me

Hajiya rukayya tace wanna ma ai kadanne ne

Dan nasan nan da wani lokaci zai kara mana

Nan dai Laila ta dauki wayarta takira Hakeem sai da yayi ta  ringing kafin yadauki
Tare da sallama cikin kwarewa da harshen larabci Dan bazaka kadauka bahaushebane

Can yace dawa nake magana please

Cikin sauri Laila tace Laila ce
Hakeem yace inajinki ya akayi

Nan tafada mishi what's kina da ciki
Laila tace a mummynka cema takaini asibiti

Hakeem yaja numfashi yace Allah yasauke ki lafiya daga haka baikara cewa komai ba yakashe wayarsa

Laila tabi wayar da kallo ta kalli mahaifiyarta  tace mama kodai shima baya farinciki da cikin ne

Suby tace kai bahaka bane kinsan halin ya Abdul yanzu hakama murna ne yasa yakashe wayar

Hajiya rukayya tace komai dai menene shine dai uban d'a

Da su so da karsu so duk uwa ubansu daya can ta matse musu

*****

Hakeem bayan ya kashe wayar ya kalli Ahmad dake fire musu doya
Dan basa cin abincin waje

Yace man kasan meye kuwa
Ahmad yace saika fada

Hakeem yace wai Laila cikine da ita  har na wata biyu

Cike da farinciki Ahmad ya ajiye wukar yadaga hanu sama
Yace Allah mungode maka
Wai mune zamu baba

Hakeem ya watsa mishi harara
Yace dadina da kai Ahmad yarinta wallahi

Ahmad yace nayarda yarinta nedan gaskiya  kam yanzu fa ka girmeni tunda gashi kana shirin ajiye baby

Hakeem yace please man muyi maganar arziki mana
Nifa harga Allah banso samun da daga jikin lailaba
amma tunda Allah yabani Allah ya albarkaci abinda za a Haifa

Ahmad yace adduar kenan kawai
Allah yashige mana gaba
Nan Hakeem yace ameen

*******
Bayan wata bakwai
Abubuwa da dama sunfaru

Su hajiya dai an tatsi Daddy Dan abin kadan zasuce a turo kudi

**
Yau laraba Laila  ta tashi da nakuda
Sukayi da ita hospital
Nan da nan aka shiga da ita labour room

Mummy hafsat itama ana fada mata tazo asibitin daddy ne yasauketa  kafin yawuce office bayan kaman awa hudu da shigarta

Ta haifo yarinyarta maikama da ita sak

Aka gyarasu itada babyn kafin akazo sanardasu mummy

ana ce ta haihu sukayi cikin dakin dasauri banda  mummy hafsat
Tace wa likitar me akasamu likita taçe mace

Mummy Hafsat tace Allah yaraya

Takira daddy tafada mishi
Yace gashinan zuwa

Su hajiya kuwa ganin Allah baicika musu burinsuba yasa sukacika tam kaman zasu fashe

amma ganin yadda daddy yake farinciki da samunjika yasa suka kwantar da hankalinsu kadan

Nan daddy yakira Hakeem yafada mishi  Hakeem yace Allah yaraya Daddy yace Ameen Ameen

Yakamata kasamu lokaci  kazo  kaga yarinyar da ita Lailar ko

Hakeem yace ai daddy bayanzu Dan karatu yafara zafi sosai sai dai mumsami time zanshigo

Daddy yace Allah yamuku albarka inashi Ahmad din
Hakeem yace yashiga wanka

Nan sukayi sallama da daddy

Ranar suna yarinya taci sunan maman daddy  wato amina

Mahaifiyar daddyn Hakeem kenan marigayiya

Alhaji  shuaib yasaka sunan da kanshi ba ma daddynba

Haka  Laila tacigaba da rainon yarta Amina

********"********

Tofa
Yanzu akafara kubiyo ummu afan

Your comment is needed fans😘😘😘😘😘

📝📝📖📖
[30/04, 5:51 PM] UMMU AFAN 🌹: 📝📖📖
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN🎗

DEDICATE THIS PAGE TO MY ONE AND ONLY HUSBAND ABU AFAN (DOCTOR SULAIMAN)❤💋

🌟GORGEOUS WRITERS FORUM🌟

🌟G.W.F🌟

HOME OF GORGEOUS INTELLIGENT AND EXPERT WE ARE THE BEST AMONG THE REST

🌟AkWAI LOKACI 🌟

🌟PAGE 31 to 35🌟

Laila kwance take tana danna wayarta

Yayinda  hajiya rukayya takeba wa Amina cerelack

Hajiya rukayya tace kinga  wasa wasa fa watan meenat shadaya amma amma haryanzu mahaifinta baizoba

Suby tace wai Ku meye kuka damu sai yadawo ne bakusan idan yadawo Baku basamun abinda kuke samu yanzu ba  """"

Laila tace nimadai haka nagani
Nifa wallahi tunda acikamin jaka da abinda nakeso yashekara  goma ma baizoba ba abinda yadameni

Hajiya rukayya tace duk kurinta ne yake damunku inba yarinta ba ai wallahi idan yashigo hanu zamufi yadda muke yanzu

Dan sai abinda tace zaibata komai ta tambaya zaiyi jiki na bari

amma hakan bazaiyu ba sai
Yaci abinci da maganin har na wajen wata daya inji malam

To ta yaya hakan zaifaru idan bata jawo shi jikinta ba

Laila tace kuma fa hakane mama yanzu manene shawararki  mama

Hajiya rukayya tace yauwa anzo gun danakeson azo

Kinga yanzu abinda zakiyi ke Laila kisamu Daddyn Hakeem kice kizakibi mijinki can saudin

Nasan shi da hangen nesa bazaiso shiga hakkin waniba

Idan kikaje can duk wani Abu na biyayyya ki kirkiro kiringa mishi inda zamusamu yasaki jiki dake sosai inda har zaki bashi abinci kuma yaci

Laila tace to mama yanzu dai zanshirya na tafi gidan mummy hafsat
Zanfada wa daddy komai

Hajiya rukayya tace  yauwa yar gari  tashi maza kishirya kiyi kama  hanya

Suby tace anty Laila zanrakaki
Lailatace shirya muje

Hajiya rukayya tace kuje kawai kubar min yarinyar

Laila tace dama bazamu jeda itaba

****

Laila sukayi sallama a falon mummyn hafsat tana zaune tace a a

Laila kune atafe

Laila tace a mummy Allah yasa daddy na nan
Munzo gurinshi ne

Mummy hafsat idan da sabo tasaba da zuwa Neman daddy agunsu Laila

Mummy tace yanan yanzu zaishigo ya fita sallah ne

Nan su Laila suka zauna zaman jiran daddy

aikuwa daddy shigowa suka gaisa
Yace Lafiya kuwa Laila kokuna bukatar wani abunne

Laila tafada mashi damuwarta nason bin mijinta

Daddy yace wannan ba wani abinda damuwa bane

Kishirya kawai kije kiyi passport agama komai kafin jibi sai kitafi

Laila tace To daddy Allah yakara girma yace Ameen
Ina amaryar tawa

Suby tace tana wajen hajiya

Yace to ace angonta na gaisheta

Nan suka wa mummy sallama suka fita

Daddy ya kalli mummy yace Lafiya kuwa mummyn Hakeem

Mummy tace wallahi alhaji mutanen kotata ban yarda dasuba
Mezaisa tabishi har can yabari mana ai komai daran dadewa zadawo

yanzu haka uwartace ta kitsa mata komai

Daddy yayi murmushi yace insha Allah ba abinda zaisamu Hakeem
Kokin manta Dan naki
Ma abocin riko da addini ne
Dakuma yawaita adduoin tsarin jiki

Mummy tayi murmushi tace hakane daddyn Hakeem
Gaskiya Hakeem kam akwai addua
Sai dai muce Allah yadada tsare mana shi

Daddy yace Ameen

Washagari daddy yagama wa Laila komai nashirin tafiya
Wanda jibi jirginsu zaitashi

Zuwa Saudi

Hajiya rukayya da hajiya suwaiba ne suka sata gaba kan yadda zata yi anfani da magun gunan dasuka karbo daga gurin malam

Komai Laila ta haddace Dan hartafara hango kanta cikin daula

Washagari jirginsu Laila yadaga zuwa Saudi
Inda tabar meenat 'yarta agurin mahaifiyarta hajiya rukayya

Daddy yadauki waya yakira Abdul Hakeem cikin ladabi Abdul yagaida mahaifin nasa
Daddy yace kashirya kaje airport kadauki matarka
Tana hanya

Cikin mamaki Abdul Hakeem yace Laila kuma daddy
Meyasa zata biyoni har nan

Gaskiya takoma gida kawai Daddy

Daddy yace Haba Dan albarka aure fa ba abin wasa bane

Na kusan shekara bakanan
Ta nemi data zo tagan ka ai baza a hanata bako

Hakeem yace amma daddy
Daddy yace karkace komai ka je airport kadauketa kawai kaji ko

Yace naji daddy Allah yakara Lafiya daddy yace Ameen
Allah yamuku albarka Hakeem yace ameen daddy

Suna gama waya da daddy yace ya Allah

Ahmad yace Lafiya kuwa Man  naganka haka
Hakeem yasauke ajiyar zuciya yafada wa Ahmad komai

Ahmad yayi murmushi yace kace nakoma dayan  part tunda amarya zata zo

Hakeem dai baice komai ba
Yazauna akan kujera

Karfe hudu dai dai yaje yadauko Laila

Tana ta rawar kai shikuwa Hakeem tunda tagaisheshi ya amsa bakaracewa komai

Wannan shine mafarin zaman Laila a saudiya

Dan bata koma ba

*******
Bayan shekara goma shabiyar
PROFESSOR ABDUL HAKEEM ABUBAKAR

Dan shekara talatindashida aduniya
Cikakken saurayine Wanda ya amsa sunan

THE YOUNG PROFESSOR

ko ina haka akeranshi gida da wajen kasan nan

Yayi suna sosai aduniya saboda kudi da kuma ilimin da Allah yabashi

Har yanzu yanazama a sauddiya ne a inda yake koyarwa a jamiar Saudi Arabian

Dashi da babban abokinshi professor Ahmad

Wanda a yanzu suke shirye shirye komawa kasarsu  Nigeria

Laila anzama manyan mata koda wasa bazaka kaga Hakeem kace shine mijinta ba

Ba alamun dacewa a tsakaninsu

HAKEEM bashida rowa koka kadan kudi masu sunan kudi yana cika
Laila dasu
Dan yanzu taza business wuman sosai suke kasuwanci da kanwarta Suby

Idan ta saro kaya a Saudi sai ta tura wa Suby Nigeria

Su duk aganin su Hakeem magani ne yake aiki akansa
Wanda abin bahaka bane   dai niyya kawai yayi yake mata abinda yake mata

Amina kuwa agurin  hajiya rukayya take sun shaku sosai Dan yarinya dai tayi mugun gado

Shiyasa basa shiri da kakarta mummyn Hakeem Dan tana mata wa azin tabi a hankali kartayi mugun gado

Yanzu haka ma basa Kaduna suna can kano nan hajiya rukayya takoma Dan mijinta yayi ritaya sai ya koma garinshi kano

Shiyasa hajiya rukayya tadauki jikarta meenat suka koma can
Yanzu meenat ta Dade a kano

Tana zuwa Hutu Saudi gurin iyayenta

Wannan kenan

KANO

Malam sualaiman  yana zaune a wata unguwar talakwa ne dake nan kano

Yana da mata daya da rana biyu

Yaya shamsu shine babba zaikai shekara 36 aduniya

alokacin da umma ta haifi yaya shamsu sai da yashekara ashirin cas

Kafin tasamu cikin asmaullahil husna
Wato asmau kenan

Inda akecemata husnah

Husnah ta taso cikin gata da tattalin uwa Dana uba da kuma Dan uwa rabinjiki wato yaya shamsu

Tunda aka haifi husnah shamsu ne me dawainiya  da ita kasancewar yadade baisamu kani ko kanwa ba

A yanzu haka husna tasamu scholarship a wani makarantar masu kudi a inda take s s two  a halin yanzu

Husna  tana da hankali da nutsuwa ga kuma  uwa uba kyau da needed

da Allah ya horemata

Husna yar kimanin shekara shabiyar aduniya

Sun hadu da Amina Abdul Hakeem abubakar

A school lokacin da husna ta samu scholarship tashigo itama Amina alokacin tashigo makarantar

Amina taso husna Dan Abu guda biyu ne na farko iliminta  farinjininta  da kuma kyau

Dakyar husnah ta amince wa Amina suka zama kawaye sosai duk inda kaji ance husnah to za ace amina

Muje zuwa 😘 anfra fa

Fan's kubiyo ummu AFAN

Kawai

Your comments is needed
[30/04, 5:53 PM] UMMU  AFAN 🌹: BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗️HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN

🌟GORGEOUS WRITERS FORUM🌟

🌟G.WF.🌟

HOME OF GORGEOUS INTELLIGENT AND EXPERT WRITERS WE ARE THE BEST AMONG THE REST

🎗️DEDICATED THIS PAGE TO MY ENTIRE FAMILIES🎗️

🎗️AKWAI  LOKACI 🎗️

🎗️PAGE  36 to 40🎗️

HUSNA nata saurine saboda tayi latti yau Monday yau ne za a Nada zabin prefect a school dinsu

Ummu tace husnah naga kina ta sauri yau Lafiya kuwa

Husnah tayi murmushi har dimple dinta suka lotsa tace wallahi ummu yau za a nad'a sabbin prefect a school ne shiyasa mukeson muje muga wadda za a ba

Yaya shamsu yace kokuma kije a nad'a kuba
Husnah tace aini bandani yaya Dan an min

Interview ma naki bada amsa a hall din

Duk Dan kar abani damuwar nan

Yaya shamsu yace ai duk yadda kikayi sunsani tunda sunsan dalibarsu
Kokinyi shiru sunsan bawai baki sani  bane

Tunda dama sunsan bakyaso
Bakince min saki dole akayi kiyi interview din ba

Husnah tace wallahi wani malaminmu ne copper yace lalle sai nayi interview

Kuma duk abinda suka tambayeni Nace I don't no
Komai I don't no kawai

Yaya shamsu yayi dariya yace kedai jekidawo kiban labarin wadda akazaba

Husnah tace to shikenan yaya
Tajuya ta kalli ummanta tace ummu sai na dawo

Ummu tace Allah yadawo dake Lafiya tace ameen umma na

Har takai bakin kofa yaya shamsu yace husnah kiyi hakuri kinji bakudi ajikina yanzu nakeson zuwa nayi buga buga naga abinda za a samo acigidan

amma namiki alkawari idan nafita nasamu wani abin zana biyo har school dinku

Inbaki Abu mai dadi

Husnah tayi murmushi tace karka damu yaya na wallahi bani da damuwar komai Dan bancika son cin komai a school ba ma

ai kana kokari yayana Allah yakawo maka aiki maitsoka nasan zamu huta sosai

Yace ameen yar kanwata jeki karkiyi latti

Tafita abinta tana murmushi

Umma ta sauke ajiyar zuciya tace wa yaya shamsu

Kasan wani Abu kuwa shamsu deen yaya shamsu yace a a umma  saikin fada

Tace wato akullum na kalleku kaida kanwar ka ina wa Allah godiya daya mallakamin 'ya'ya nagari

Dan ba abinda zance wa Allah sai godiya kawai

amma duk inda ake neman 'ya'ya nagari nasamu
Abba dayake shirin fitowa daga dakinsa yace munsamu dai  zakice zainaba

Tunda Allah yasa shamsu yakawo kwari fa shiyake dawainiyya damu agidan

Shine komai na kanwarsa shine namu aiba abinda zamuce sai muce shima Allah yabashi mai mishi

Umma tace Ameen malam

Malam sulaima yace babban damuwata shine inga kasamu aiki kayi aure  Dan shine cikar mutuncin mutum

Umma tace hakane ai baki yayi tunda yana da wacce yakeso khadija yarinyar kirki taki kowa saishi take jira
Ko a yanzu aka tura za ayi komai tunda iyayen ma sun komai

Malam sule yaja numfashi yace hakane kam to Allah yabamu yadda zamuyi

Ya kalli shamsu da tunda suka fara zancen auranshi yashiga duniyar tunani

Dan yana matukar son budurwarshi khadijat wacce akekira da kubra kitama tana son yaya shamsu sosai Dan

Shekarar ta daya kenan  dagama secondary school
Manema sunzo Neman aurenta taki ita sai shamsu
Haka iyayen suka hakura suke zaman jiran shamsu yakawo sadaki a daura aure

Malam sule yakalli shamsu yace karka damu akwai Allah

Shamsu yace barinje Abba sai na dawo ya ma umma ma sallama ya wuce zuwa Neman abinda zasuci

YAYA SHAMSU daga secondary bai kara gaba ba saboda rashin kudi daya musu katutu shida mahaifansa

Dan haka kawai ya hakura yake Dan buga bugansa dahaka kuma har Allah yasa aka haifi kanwarsa husna saiya yaci burin Husna zatayi karatu tunda shi Allah baisa zaiyi mezurfiba

Sai kuma gashi Allah yafara cikawa shamsu burinsa inda husnah taci scholarship

**
Husnah tana isa school tasamu anfara assembly
Ta tsaya daga bayan 'yan mate dinsu suna sauraron jawabi daga bakin principal dinsu

Can sai vice principal yace yace zamufara kiran  new prefect dinmu daya bayan daya

Principal tace a fara da head girl ko

Sai copper bash yace am sorry ma
Gwamma afara da sauran kafin head girl
Zaifi Jan ra ayin su

Principal tace OK afara kira kawai

Nan akafara kiransu ana samusu hula da kuma belt
Dansu prefect din hula suke sawa green gabadayansu na head girl ce kawai ya   banbanta Dan nata read cap take sawa

Can taji ance social prefect AMINA HAKEEM ABUBBAKAR

Nan aka dau tafi raf raf raf ana murna

Can sai vice principal yayi gyaran murya yace  yanzu zamu Kira me gayya me aiki  wato our head girl

Nan aka kira sunan ASMAU SULAIMAN SHAMSU

cikin gigicewa  Husnah tadago kanta aikuwa tana dogowa sukayi ido hudu da  Copper bashir

Ya kashe mata ido daya

Cikin tashin hankali Husnah ta daga  kafa dakyar tana zuwa ta hau kan stage

Principal ta rungume Husnah tare da
 Da samata hulan head girl dinta read cap

Ta daura mata belt dinta read shima
aikuwa daga students har malaman dake wajen  aka dautafi  Dan sunburge kowa ga read cap din yawa  Husnah kyau sosai kaman Dan ita akayi hulan

Nan dai aka rantsar dasu Husnah a matsayin new prefect

***

Copper Bash ya tsare Husnah alokacin dazata wuce gida  itada meenat

Copper bash yace asmau
Ya naga kina ta shan kamshi ne Yau

Meenat tafashe da dariya
Tace uncle ai Husnah fa batasan za abata prefect  ba ballantana Head girl

Copper bash yayi murmushi yace ai kuwa ta yaudari kanta

To inba a bata ba waza aba wa
Meenat tace aifa dai kam

Husnah dai tana jin su batace komaiba

Nan driver din meenat yazo daukarta

Husnah kuma dama da kafa take zuwa take komawa

Meenat tace Dan Allah Husnah kizo musaukeki a gidan  kinga sai naga gidanku ko

Husnah tayi murmushi dimple dinta suka lotsa

Copper bash ya tsaya kawai yana kallon Husnah komai nata cikin aji takeyinsa    da nutsuwa shiyasa takeda farinjini a school din

Husnah tace wallahi meenat idan ya shamsu ya ganni a mota zai min fada sosai .

Meenat tace kedai kawai   bakyason kibimu sai kiyi tayiwa yaya shamsu sharri

Copper bash yace kinga kuyi sauri kutafi gida kar anemeku kuntsaya surutu

Meenat tace to shikenan sai mun hadu goben  idan munzo ko

Husnah tace to meenat  Allah yakaimu kigaida gidan
Nan sukayi sallama

Copper bash yace wa Husnah muje nakaiki gida da kaina

Tunda kinki kawarki takaiki

Husnah  tace Dan Allah uncle kayi hakuri wallahi yayana yaganni da kai zaimin fada

Copper bash yace mezaisa yamiki fada baki kai a rakakin bane ko yaya

Husnah tayi shiru  tace kayi hakuri Dan Allah

Yace wato har yanzu Husnah kinkasa yarda da sonda nake miki ko

Kibani dama nasan gidanku da iyayenki  wallahi dagaske nake auranki zanyi Asmau

Husnah tace Dan Allah malam kayi hakuri kar yaya yasan da wannan maganar

Dan ya hanani kula koda kawace ballantana

Maganar soyayya  tun yanzu

Da kyar yabani dama kawance da Àmina Hakeem ma

Copper bash yace OK na fahinceki
Ba wai nidinne bakyaso ba umarnin yayanki kikebi ko

Husnah ta rufe ido tana murmushi tayi hanyar fita daga gate din school din

Copper bash yayi murmushi tunda ya gano yafara shiga zuciyar Husnah

Zaisan hanyar da zaibi Dan yasan iyayenta da yayanta shamsu

Bashir Dan wani hamshakin maikudi ne sosai acikin garin kano

Bautar kasa wato NYSC yakaishi school dinsu Husnah
Tunda yadora idonshi kan Husna yaji yakamu da son ta

amma takibashi daman hakan

Next page
[05/05, 11:05 AM] UMMU AFAN 🌹:
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN 🎗

🌹🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹🌹

🌹F.C.T.W.A🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITERS OF THE NATION🌹

🎗️DEDICATE THIS PAGE TO UMMY 😍 KINA KOKARI WAJEN GANIN NOVELS DINA SUNA KARBUWA A KOWANI GROUP ALLAH YABAR KAUNA 😘😘😘😘😘

🎗️AKWAI LOKACI🎗️

🎗️PAGE 41 to 45 🎗️

ABDUL HAKEEM THE YOUNG PROFESSOR

kwannansu biyu da dawowa daga saudiya dashi da madam laila

HAKEEM yana shirin zuwa sashen iyayensa ne don yagaishesu

Yafito daga wanka ne yashirya cikin wani farisol din jallabiya ya faffesa turarruka masu kamshi Dan akwaishi da son kamshi sosai

Har yagama shiransa zaifita Laila bata tashiba

Ya kalleta kawai ya girgiza kai yayi gaba abinsa zuwa part din su mummynshi

Yanashiga yasamesu akan dining da mummy da daddy

Daddy yace Dan halal kaki anbato yanzu nace baka shigo break fast ba mummyn ka tace ai tasan kana hanya

HAKEEM yayi murmushi cike da kaunar iyayensa

Yace ai mummy tafadi gaskiya Dan bazan taba karyawa a wani waje ba matukar muna tare da mummy

Mummy tace yauwa son fada mishi dai

Nan mummy tayi serving din HAKEEM abinci yafara ci

Bayan sungama break fast ne mummy zata kwashe kwanukan Hakeem yace haba daliba yazakimin haka kuma

Kezaki kwashe kayan zuwa kitchen nikuma meye anfani na

Mummy hafsat tace nabari tashi ka kawashe

Daddy dai dariya yake musu yakoma kujerar falo yazauna

Hakeem bayan yagama kwashe kwanukan zuwa kitchen saiya dawo falo Dan hira da iyayen nasa

Daddy yace wai acikin makarantu biyu dasuke bukatarka wanne kazaba kayi lecturing din agun

HAKEEM yayi murmushi yace ai daddy daga ni har Ahmad munzabi muje BUK kano

Daddy yace Allah yasa haka shine alkairi

Mummy hafsat tace amin

Daddy yace kace kuna tare da amaryata kenan

Mummy hafsat tayi murmushi tace MEENAT ko rigima

Yakama ta ma suturota tazo tagaida iyayenta ai

Daddy yace karkice komai tunda basuyi hakan ba shi saiyaje yaganta

Kafin Hakeem yayi magana wayar daddy yadau kara

Daddy yadaga sai sukaga daddy yace subuhanallla a wani asubiti

Mummy da Hakeem suka maida kallonsu kan daddy

Bayan daddy yakashe wayar ne suka tambayeshi abinda kefaruwa

Yace Abba na aka kai hospital

HAkeem yace subuhanalla muje kawai daddy

Mummy hafsat tace nima bazaku barniba muje tare

Suka he asibitin Hakeem ne me driving dinsu

Suna isa suka sami alhaji shuaib bayadda yakara ji

Dan yanajin jiki sosai

Alhaji shuaib yarike hanun Dan nashi wato daddy
Yace Allah yamaka albarka abubakar da kai da zuriarka

Ba abin da zance dakai sai Allah yàmaka sakayya da gidan aljanna duk inda akeneman yaro nagari ka kai abubakar

Ya kamo hanun Hakeem yace jikallena ga mahaifinka nan nabar maka amanarshi duniya da lahira

Kabishi kamar yadda yabini

Ya kalli mummy hafsat yace kema Hafsatu Allah shizai biyaki akan yadda kika nuna kaunarki ga abubakar

Duk yadda aka kai cutar dashi kinki bada damar hakan

Allah yamiki albarka

Tunda alhaji shuaib yafara magana suke kuka musamman daddyn Hakeem

Da mummy

ABDUL HAKEEM ne kawai ya daure amma shima idonshi yayi ja sosai

Can dai likitoci sukace sufita zasu samishi
Oxygen Dan numfashinsa yafara kasa

Alhaji abubakar ne kawai akabari a dakin

Can wajen La asar 'yan kano suka iso asibitin

Kuma harda meenat

Hajiya rukayya itama a rikice tazo jincewa jikin mahaifin nasu ya tashi

amma anhanata shiga taganshi

Hakan kuma ya bata mata rai sosai

Amina kuwa tana ganin daddynta Hakeem tare da mummynshi takarasa wajensu cike da murnar ganin uban nata

Bayan tagaida Hakeem ne take tambayarsa dad ina mummyna yace tana gida yanzu zata zo itama

Amina ta kalli mummy hafsat tace wato ma bazaki kimin magana ba ko

Mummy hafsat tace kaga jaira kinga babanki bakima San ina wajenba zaki ce ban miki maganaba

Sannu uwata mummy hafsat takarasa maganar tana tsokanarta

Amina tace ai wallahi duk abin kidai saina auri mijinki sai naga yadda zakiyi

Mummy hafsat tayi murmushi tace kishigo mana kigani da tabarya zan koraki ai nan mummy Hafsat tana jikinta ajiki sukata Dan hirarsu amma cikin jimamin rashin lafiyar alhaji shuaib

Ahmad yakaraso hospital din shima cikin jimami

Hakeem na ganin Ahmad yace Man ka karaso kenan

Ahmad yace ai kana kirana nace wa mummy zanzo hospital namata bayani

Itama zasu zo tanason gama abincine sai ta taho dashi

Hakeem yace Allah yakawota Lafiya

Ahmad yace barinje na gaida su mummy suka karasa harwajensu mummy

Yagaishesu yamusu ya maijiki

Amina tace daddy Ahmad ina wuni yace Lafiya qalau daughter ya mummyn ki

Tace banganta ba mu yanzu mukazo daga kano

Kafin Ahmad yayi magana daddyn Hakeem yafito daga dakin yana goge hawaye

Hakeem da Ahmad suka  karasa dasauri Hakeem yace daddy yajikin alhajin

Daddy abubakar yace Hakeem Allah ya yi wa mahaifina rusuwa
Alhaji yatafi yabarni Hakeem

Yanzu bani dakowa dama bansan mahaifiyata ba shikadaine min aduniya

Shima yatafi

Duk matan dake gun sukasa kuka

******

Bayan arbain din alhaji shuaib

ABDUL HAKEEM  da aminin sa suka fara lecturing  B U K

Dan karakaran gidaje makaranta tabasu a matsayinsu na professional akan aikin su

Yanzu Haka suna shirye shiryen auran Ahmad kuma a kano zaitare da matarsa

Itakuma Laila tayi tayi yabarta tadawo kano yaki

Sai dai yazo masu Hutu yakoma

Yanzu haka bikin Ahmad saura sati biyu cas a daura auren Ahmad

*****

Yaya shamsu zaune akan kujera yar tsugune  umma kuma na hada zobo Dan duku gidan suna azumin Monday da alhamis

Itakuma Husnah tana kan hada musu abincin buda baki a kitchen

Kanin kubra budurwar yaya shamsu ne yayi sallma yashigo ya tire

Ya gaisheda umma kafin ya ajiye abincin yace yaya shamsu gashi anty kubra

Kafin shamsu yayi magana umma

Tadauko naira hamsin tace zoka karba ko kace mata angode Allah yasaka da alkairi

Yaron yaki karbar kudin umma yaya shamsu yace haba kanina  karba mana ai ba roka kayiba

Yakarba yayi godiya zaifita kenan
Husnah ta tace sani kace wa anty kubra gobe zanzo kitso
Sani kanin kubra yace to zanfada mata

Umma tace kajita kaman wani kitson takeso
Yanzu zatace maka zata kitso taje tadawo da kalba

Husnah tayi murmushi tace umma wallahi banason kitso nafison dai amin kalban kawai

Tagama kwashe komai ta ajiye musu akan taburma

Jelouf din taliya ta musu Wanda ya shamsu yakawo dazu yace a dafa yasan tana son taliya sosai

Umma tace wallahi yarinyar nan kubra akwai kokari
Bata gajiya da aiko maka da abinci duk Monday da alhamis

Husnah tace gaskiya kam wallahi anty kubra Nada kirki

Yaya shamsu Allah yabaka kudi wannan sallar dai kasamu kamata kayan sallah

Umma tace amin gaskiya kam ta cancan hakan

Shamsu yaja numfashi yace kuma wallahi umma kubra bata jin dadin gidansu

Indai ba abbanta yana gidaba

Kishiyar mamanta tana matsa mata sosai
Yanzu fa wai akwai Wanda yamata magana yanson kubra shine tadage sai kubra ta amince da auran wani baniba

Dan taki amincewa shine take bata wahala
Kuma abbanta yace bazai mata auren doleba
Sai Wanda takeso zaibata

Shine tayi bakin jini agidan

Umma tace Allah sarki marainiyar Allah

Allah yabaka abinda zaka  auro yarinyar nan karabata da gidan nan

Shamsu yace amin umma
Husnah ma tace amin

Yaya shamsu yace barinje sallar magriba indawo muyi buda baki

Shamsu yana  fita Husnah tace wallahi ummu yaya shamsu yana bani tausayi

Dan wallahi shima yana son kubra sosai

Umma tace bakomai AKWA LOKACI

watarana sai labari Husnah tace Allah yanuna mana lokacin amin ummu tace

Suma tashi sukayi Dan gabatar da sallah

**
Bayan kwana biyu wani abokin shamsu  yabashi
Shawarar mezaihana yakai takardunsa Neman aiki B U K  koda masinja aka bashi zai rage zafi ai

Shamsu yace gaskiya naji dadin shawarar nan daka bani kabiru
Allah yabar zumunci

Kabiru yace bakomai ai   zaman  taren kenan

Kaga ni a secondary school nake masinja amma alhamdulilla ina samu

Ya shamsu yace hakane yanzu zanyi wanka nakai kuwa

Bayan ya shamsu yashirya zuwa kai application dinsa

Saiya wa umma sallama Yakama hanya

Bayan yakai akace za anemeshi idan yasamu idan kuma baisamuba zaiji shiru

Yabasu number dinsa

Yatafi gida yana ta aduar  samun nasara

Idan Allah yasa yasamu aikin nan zaiyi kokarin  raba kubra da gidansu  tazo suyita maneji yasan  kubra zatayi hakuri da abinda zaibata umma kuma bata da matsala zasu zauna Lafiya

*****

Professor Abdul Hakeem zaune a office dinsa yana duba wasu takardu sai wata mata tashigo tagisheshi

Tace wai itace sabuwar sakatariyarsa

Abdul Hakeem yace OK zaki iya tafiya  sai na nemeki

Tafita
Tana fita Hakeem yakira management din makarantar

Suna ganin wayar office dinsa
Aka je dasauri Dan yanakirane

Manager nashiga yagaishe da professor Hakeem

Hakeem yace ina buka tar a canza min secretary  ma ana bayason mace

Namiji yakeso akawo mishi

Manager yace angama sir

Hakeem yabashi izinin tafiya

Sukaje suka zauna meeting

Nan akayi shawarar daukar SHAMSUNDEEN SULAIMAN  a matsayin secretary na THE YOUNG PROFESSOR ABDUL HAKEEM

Yaya shamsu yana kofar gidansu kubra yaje zance
Sai yaga kira da bakuwar number

Yayi picking call din

aikuwa kubra taga yana ta fara a yana godiya
Bayan ya kashe wayar ne

Ya kalli kubra yace kiyimana murna munsami aiki kinga kenan burinmu yakusa cikako

Cikin tsananin farinciki kubra tace alhamdulillahi
Gobe zafara azumina kenan

Da mamaki shamsu ya kalli  kubra yace azumin mekuma zakiyi

Kubra tayi murmushi tace aina wa Allah alkawarin cewa duk randa kasamu aiki sainayi azumi uku cas

Shamsu yace aikuwa bazakiyi kekadaiba tare zamuyi

Nan dai yamata sallama ya wuce gida Dan yasanar wa umma

**
Umma tayi farinciki sosai  haka ma mahaifinsa

Husnah kuwa tsalle taringa yi tana murnar ankusa kawo musu anty kubra gidansu

Mahaifinsa yace gobe zaka fara zuwa kenan
Yaya shamsu yace a daga gobe sukace wai karfe takwas zandinga zuwa

Sainaje ma zasubani dokokinsu

Nan iyayen sukayi ta albarka

Washagari yaya shamsu yashirya zuwa wajen aiki

Bayan yayi sallama da su umma

Ya wuce gidansu kubra itama tamishi adawo Lafiya

Yana isa aka gama komai aka turashi office din PROFESSOR HAKEEM

yana zuwa yayi nocking akace yashiga

Professor Hakeem yanakan kujerar shi yana fama da wasu takardu

Shamsu yashiga yagaisheshi professor Hakeem ya amsa batare da kalleshiba

Yace ta akayi malam

Shamsu yace daman nine sabon secretary din da aka turo office dinka

Professor Hakeem yace OK dafatan zamuyi da gaskiya malam

Shamsu insha Allah sir

Sai alokacin professor Hakeem yadago kai ya kalli ya shamsu

Yace ko zan iya sanin sunan malamin
Yaya shamsu yayi murmushi yace Shamsuddeen

Hakeem yace malam shamsu Allah yatayaka riko za iya tafiya

Shamsu yayi godiya yace nagode sir

Ya wuce abinshi professor Hakeem yacigaba da aikinsa

Can wajen shabiyu da rabi professor Ahmad yashigo office din Hakeem yace ya man muje muyi

lunch kasanfa  bana jure yunwa

Hakeem yayi murmushi yace wai damma ka kusa  shiga daga ciki
Aisha Nada aiki wallahi sai dai ta ringa samaka wani flask

Ahmad yayi dariya yace ai dani dakai  duk jirgi daya yakwàso mu

Nan dai Hakeem ya tattara suka fito tare Hakeem yakalli shamsu dake kan kurarshi yace

Abokina zamufita ga key din office din take care

Shamsu OK adawo Lafiya

Suna zaune a gurin cin abinci Ahmad yace waini wannan Dan gayun ne sakatarenka

Hakeem yace kaima kaji mamaki ko

Da naso namishi tambayoyi sai naga rashin dacewar hakan gwamma nagama fahimtarshi kafin

Naji tarihinsa

Ahmad yace hakan ma yayi
amma mutum very responsible person kaman wannan ace yana sakatare

Shamsu yashiga office din maigidan nashi yaga kudi a kasa
Ya dauka ya ajeye mishi a saman tebur

Bayan su Hakeem sundawo yashiga office din sa
Sai ya kalli inda ya zubar da kudi yaga babusu
Dan dama da gangan yayi hakan Dan ya gwada shamsu ne kawai

Yazauna akan kujerarshi aikuwa idonshi yakai kan kudinshi da shamsu ya ajiye mashi su

Professor Hakeem yayi murmushi akaro na farko
Yaya shamsu yashiga ranshi

Karfe hudu dai dai Hakeem yatashi a office dayafito yaga kujerar da shamsu yake yaga yana waya ne amma yanaganin fitowar Hakeem yawa kubra sallama

Hakeem yayi murmushi yace hala kaida uwargida kuke wayar kuma ka kashe

Yaya shamsu baice komai ba sai murmushi kawai

Hakeem yace natashi kaima zaka iya tafiya

Shamsu yace aisunce wai sai time din tashi yayi zantashi

Hakeem yace no  zan musu magana kaje kawai abinka

Hakeem har yayi gaba ya dawo yace  sunbaka kudi kuwa
Ya shamsu  yace wani kudi kuma nida nafara aiki yau  sir yakarasa yana murmushi

Hakeem yayi murmushi yace yakamata subaka kudin daukar aiki

amma zanbaka aro idan anbaka sai ka dawo mundasu ko

Ya shamsu yayi dariya kabarshi kawai sir kar azo basu baniba

Hakeem yayi murmushi yace idan basu baka na barma

Kuma banason musu yashiga tsakaninmu malam shamsu ka karba kawai karmuyi haka dakai

Shamsu yakarba yace nagode yallabai

Yace karka damu

Sai gobe kayi kokari ka koma gida

Shamsu yasake baki kawai yana kallon Hakeem

Yaduba damin kudin da Hakeem yabashi

Nan dai yayi wa Allah godiya cike da farinciki shamsu ya kulle kofar office din su

Yayi gida

Yana zuwa Husnah ta tareshi da murna oyoyo yaya na sannu da dawowa

Shamsu yayi dariya yace yauwa yar kanwata ina umma

Ummu ta fito daga daki tana daura dankwali tace a a dawuri haka

Yaya shamsu yace wallahi Allah ne ya hadani da shugaba nagari yace karfe hudu ma ina iya tafiya

Umma ta ce alhamdulilla ai haka akeso
Yaya shamsu yace umma ina Abba tace yanzu zaishigo sunje gaisuwar Mara Lafiya shida malam tanko

Kafin tarufe baki ma sai ga Abba yayi sallama yace a a Dan albarka har andawo

Nan suka zauna kan ta Burma yafito da kudin ya ajiye gaban mahaifinsa

Nan yamusu bayanin komai

Abba yayi gyaran murya yace to yanzu idan akazo ba a baka kudin daukan aikin bafa

Ya shamsu yace  nima haka nagani dai
Na nuna yabar kudinsa kawai yace aishi yabani

Umma tace to kaidai duk inda kake ka tabbatar karike gaskiya kazauna da kowa zuciyarka daya

Ya shamsu yace insha Allah
Zankiyaye

Nan dai Abba da umma sukace baza a taba kudinba harsai

anbaka angani koba hakaba yaya shamsu yace hakan ma yayi gaskiya

Husnah tace Abba kawai da yaya shamsu yayi anfani da kudin gurin kai sadakin anty kubra

Koba a bashi tunda yana aiki saiya biyashi a hankali

Abba yayi murmushi yace uwatakenan ke yarinyace har yanzu bakisan duniyaba

Indai aure ne ai zaiyi insha Allah

Suka ce Allah yasa

📖📖📝📝

Bayan kwana biyu ranar alhamis ya shamsu yaje wurin aiki aka kirashi akabashi kudin daukar aiki naira dubu goma shabiyar

Da yadaqo gida yace wa ma haifinsa ambashi yanuna musu

Abba yace alhamdulilla kaga gobe saika mayar mashi da kudinsa

Allah yayi albarka ya shamsu yace ameen Abba

Abba yace yakabar kudin kuma anan
Ya shamsu yace Abba kayi abinda yadace kawai

Abba yace wa umma tadebi kudin ta ajiye agunta

Washagari ya shamsu yasami professor Hakeem a office yamishi bayani yamayar mashi da kudinsa

Hakeem shi har ya manta ma yaba wa ya shamsu kudi

Ba karamin burgeshi ya shamsu yayi ba
Yace
Gashi kasiya wa yara sweet

Ya shamsu yayi dariya yace ai banida aure

Hakeem yakalleshi yace

Malam shamsu idan bazaka damu zanso jin labarinka

Next page

Your comments is needed
Fan's

📖📖📝📝
[05/05, 11:08 AM] UMMU  AFAN 🌹:

🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA  NA UMMU AFAN 🎗

🌹🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹🌹

🌹F.C.T.W.A🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITERS OF THE NATION🌹

🎗DEDICATE THIS PAGE TO UMMU HANIF 🎗

🎗AKWAI  LOKACI🎗

🎗PAGE  46 to 50🎗

PROFESSOR HAKEEM yace ina sauraronka malam shamsu

Ya shamsu yayi murmushi nan yabashi kadan daga cikin  tarin rayauwarsu

Hakeem yace kace kai din dai har yanzu dai gaurone   murkusheshen gaurone

Ya shamsu yayi murmushi yace a nakusa fita a layin gaurayen tunda nasamu abinyi

Hakeem yace hakane

Ya kalli kudin da ya shamsu ya ajiye mashi akan tebur

Yadauko wani rafar ya hada mashi dasu yace

Kadauki wannan kudin kaje kamuku cefane

Sannan kuma ka Isar min da gaisuwata wajen Abba da umma
Da kuma yar kanwarmu

Ya shamsu yace amma ai kudin sunyu yawa yallabai

Hakeem yayi murmushi yace karkadamu

Malam shamsu kana da sha awar cigaba da karatu ne

Shamsu yayi murmushi yace
Zanyi kokari bayan aure na ga nasamu ko degree na samu insha Allah

Hakeem yace Allah ya nuna mana ya shamsu yace nagode Allah yasaka da alkairi

Hakeem yace godiyan yana yawa kuma.banason godiya malam shamsu

Ya shamsu yayi murmushi yace ai ka canci hakan ne yallabai

Nan dai suka Dan taba hira har lokacin tashin Hakeem yayi suka tafi shida Ahmad

Ya shamsu kuwa yana fita yaje kasuwa yamusu cefane sosai har kaji da lemuka  masu sanyi

Yana isa kofar gidansu mai adai daita sahu ya tsaya yabiyashi yafito da ka yansa

Yashiga cikin gidan da sallaman shi

alokacin Husnah tana alolar La asar

Tana ganinshi ta karasa wanke kafarta ta zo takarbeshi tana mishi sannu da zuwa

Yace alolar mekikeyi tace LA asar ya shamsu yace haba Husnah yazaki bari lokacin sallah ya wuce kina da lafiyanki

Kafin tayi magana umma daga kitchen tace ai yau Husnah bataji dadiba ne

Tun da tadawo daga makaranta take kwance  kanta naciwo

Ya shamsu yace ashsha  barin je nasiyo miki magani
Yanzu zandawo

Husnah ta rike rigar ya shamsu tace wallahi naji sauki yaya

Dama abin da ya haddasa min ciwon kan ma

Wani taro akayi a school dinmu kuma nice presenter

Hayaniya ce yasani ciwon kan amma Dana dawo gida umma tabani magani nasha na kwanta yadaina

Ya shamsu yace kinta tabbata
Husnah tadaga kai alamun ta tabbatar

Abba ne yayi sallama yashigo
Da Leda a hannunsa Husnah ta ajiye Wanda ya shamsu yakawo akan taburma tayi saurin karbar na Abba alkamace Abba ya auno Dan Abba akwai son tuwon alkama dashida ya shamsu

Bayan sun zauna ne ya shamsu yace Husnah dauko kayan can kiraba mana

Husnah ta tashi ta dauko

Plate guda uku da tasawa Abba kajin da kuma Irish potato wato dankalin turawa
Ta ajiye mashi maltina Dan tasan zaifi sonshi

Kafin tasawa umma itama maltina tamata

Sai ta hada musu itada ya shamsu ta dauki  lacasera

Ta dauka wa ya shamsu fanta dantasan abinda kowa yakeso

Umma ta ce yau fa shagwaban yatashi Abba yace a din tayi baruwanki ai sunfi kusa yakarasa maganar yana dariya

Husnah tace yauwa Abba fada mata dai

Ya shamsu yayi murmushi Dan yanason yadda suke rayuwarsu cikin son juna acikin gidansu

Suna gamawa Husnah ta tashi tadauko Dan karamin kula  tasaka naman da komai yadda sukasha sai wannan lemu sunkai uku

Tasaka a Leda tace ya shamsu wannan na anty kubra ne idan kaje kace mata inji sweet kanwarta

Umma tace kai wannan soyayya da Husnah takewa kubra

Inba auren nan akayi ba hankalin Husnah bazai kwanta ba ba

Abba yace ai soyayyar Dan uwantane yashafi khadijan

Husnah tace gaskiya Abba kana da ganewa wallahi yadda anty kubra takeson ya shamsu yasa na ke ganin girmanta

Shidai shamsu inbanda murmushi ba abinda yakeyi

Nan yawa mahaifinsa da ummansa bayanin yadda sukayi da maigidansa

Abba yace Allah yasa hakan shine mafi alkairi

Kaga girman alkawariko

To haka akeson mutum aduk inda yake ya rike gaskiya

Ya shamsu yace hanekam
Nan yabawa mahaifin nasa kudin gabadaya yace ya ajiye agunsa

Ya tashi yashiga wanka Wanda Husnah ce takai mai yana fitowa yayi alwala zuwa sallar magriba

Bayan ya dawo daga isha  ne yadauki kayan da Husnah tabashi yakaiwa kubra

Ya fesa turarensa mai Dan arha duk da talaucin su ya shamsu baya rabuwa da turare danshi mutum ne mai tsafta sosai Dan gado sukayi a wajen iyayensu

Saikuma Husnah tace matsa kaban guri akan tsafta kokadan Husnah bata son datti

Yana isa gidansu kubra ta fito da hijabinta dogo

Duk yadda takai taboye abinda aka mata agida kubra takasa sai da yagane

Yace Lafiya naga fuskarki haka kubra

Kubra tayi yake tace bakomai wallahi abune yafada min a idona amma  nacire

Kafin ya shamsu yayi magana wata kanwarta wadda suke uba daya tazo tace wai kizo inji mama kicigaba mata da abinda tasaki

Kubra tace kice inzuwa yarinyar tajuya takoma zuwa cikin gidan

Tausayin kubra Yakama shamsu sosai yace kiyi hakuri kinji watarana sai labari nasan duk akaina kikaganin wulakanci Dan kin ki bada hadin kai

amma namiki alkaqarin komai yazo karshe insha Allah

Yace karbi wannan inji kanwarki tace nakawo miki

Kubra tace Allah sarki Husnah Dan Allah kace mata nagode sosai

Yaciro dubu uku a aljihunsa yace karbi wannan kirike a hanunki

Kubra ta kalleshi ta kalli kudin tace haba sahibina ya daga samun aiki zaka fara barna da kudi kawai kabarshi

Yace ai duk abinda zansamu kina da kaso aciki kikarba kawai kubra idan baki karba ba zaki bata min rai

Cikin sanyin jiki kubra ta karbi kudin
Tace nagode Allah yakara budi yace amin

Maza koma gida kikarasa abinda aka saki karkiyi laifi ko

Tace to sai anjima ko kuma saigobe ba inji ya shamsu

Washa gari dasafe ya shamsu yagama shirin zuwa aiki  bayan sun karya

Yafito yace wa Husnah muje ko

Husnah tace to  yaya suka wa umma sallama

Suna futa kuwa suka yi sa ar  keke napep yaya shamsu yatare musu sukashiga

Suna tafiya suna hira yace inga jakanki tabashi bata kawo komai a ranta ba

Ya shamsu kuwa yafaketa yasaka mata 1000  a ciki dubu daya kenan

Suna zuwa dai dai gate din su Husnah ya shamsu yace wa driver tsaya ta sauka nikuma kayi dani  BUK  Husnah tasauka tana daga wa ya shamsu hanu

Yayi dai dai dannowar motar copper bash

Yaji lokacin datace ya shamsu kanan ya shamsu ne acikin keke napep din nan
Inkuwa shine zanbisa namishi bayanin komai

aikuwa copper bash yayi ta bin yaya shamsu abaya har yasauka a gate din BUK

Bayan ya shamsu yabiya kudin yayi gaba abinsa

Copper bash yayi parking yafito
Yabi bayan ya shamsu
Har yaje yayi signing yazo kafin yaje can kujerashi kofar

PROFESSOR HAKEEM  yazauna

Copper bash yamishi sallama  ya shamsu ya amsa yace  kozan iya taimakonka

Copper bash yace a daman taimakon nazo nema

amma a gurinka ya shamsu

Yadda copper bash yakirashi ya shamsu yasan duk yadda akayi yasanshi ne

Ya shamsu yanuna mishi kujera
Nan copperbash yafada wa yaya shamsu irin son da yake wa kanwar shi

amma taki bashi dama hakan

Ya shamsu yace bazata ta taba amince maka har sai nabata izini

Umarni nabata nima kuma bazan taba amincewaba har sai nayi bincike akanka kafin nan kuma na tabbatar tana sonka na uku kuma zakamin alkawarin barin ta tayi karatu bayan kinyi aure amma wannan zaizone bayan nayi bincike nagar tarka

Copper bash yace wallahi ya shamsu indai akan asali ne bana shakku aje ayi bincike fata na kawai idan kabincika bani da matsala ka amince min nakawo sadakina gidanku shikadai ne zaisa hankalina yakwanta

Ya shamsu yayi murmushi yace karka damu Allah yashige mana gaba

Nan yawa ya shamsu sallama yatafi

*******

HUSNAH zaune kan kujerar class dinsu teacher din dazata shiga musu ta haihu shiyasa suka samu Free time

Meenat tace gaskiya Husnah baki da kirki yanzu kakan dad dina da mummy na ya mutu amma kikasa Neman gidan mu kije kiwa kakata ta aziyya

Husnah tace afuwan aminyi insha Allah ranar asabar zanzo gidanku nawa kakanmu ta aziyya

Meenat tace kai amma danaji wallahi har na matsu asabar tayi

Hajiya ta taganki labarinki kawai takeji agurina

Husnah tace aikuwa zanzo nagaisheta

Tace amin Allah yasa daddy ma yazo sai kigaisheshi

Kinsan tun yadawo kano aiki duk Saturday yake zuwa yaganni

Husnah tace to Allah yakaimu ranar

Suna haka wata junior tashigo tace anty husnah wai kizo inji uncle bash

Husnah tace OK kice ganinan zuwa

Meenat ta kebe baki tace wai meke tsakaninku da copper bash ne

Husnah tace sirrine amma zakiji nan gaba tashi muje kirakani kawai

Meenat ta tashi jiki a sanyaye tabi Husnah zuwa office din uncle bash

Suna shiga suka gaishe da bash ya amsa idonsa akan Husnah

Takaici Yakama meenat

Dan ita ba namijin datakeso irin copper bash
Tayi shishigin amma bata samu karbuwa ba

Ya kalleta yace zaki iya jiranta a kofa magana zamuyi

Meenat cike da bakin ciki ta fito

Copper bash ya kalli Husnah yace munhadu da  ya shamsu

Cikin sauri husnah ta dago kanta da sauri tace meyace maka shikenan nasan yaya zaiyi fishi dani

Copper bash yace karkidamu ba abinda zai miki shima naga alama yana da fahimta
Nan yafada mata yadda sukayi da ya shamsu

Cike da jin dadi Husnah ta tashi tayi hangar waje

Yana kiranta amma taki juyowa saboda kunya

Tana shiga sukacikaro da meenat

Kuka shabe shabe a fuskar meenat

Husnah cikin tashin hankali tace lafiya kuwa meenat cikin rashin sanin mezatace tafara in inna

Tace wallahi bansan menayi wa copper bash ba ya tsani yaganni aguri sai yakoreni

Husnah tace kiyi hakuri zanmishi magana kuma I sha  Allah zaiyi dai dai

Meenat ta share hawayenta tace Husnah na tambayeki meketsakaninku da shi baki fada min ba

Husnah tayi murmushi tabata labarin komai

Meenat tace yanzu kinaso kice min kun Dade kuna soyayya da shi

Husnah tayi murmushi tace a
Amma ni banbashi daman zuwa gidan mu ba

Shine yanzu yake cemin ya wa yayana magana

Meenat tarike kai alamun jiri nason yarda ita

Husnah ta taimaka mata tazauna tace Amina Hakeem anya lafiyarki kalau kuwa

Gaskiya kitashi mu dispensary
Abaki magani

Meenat tace gida ma zantafi tai maka min da phone dina acikin bag

Husnah tabude jakar meenat taga wasu hadaddun wayoyi masu tsadar gaske kuda biyu aciki

Ta kwaso duka tace gasu  meenat ta karbi daya takira driver din ta

Taba wa Husnah wayar ta mayar mata dashi jaka

******

Bayan kwana hudu ankai sadakin yaya shamsu gidansu kubra

Sannan kuma Abba yasai  block da yashi ma aikata sukafara aikin gyaran inda ya shamsu zai zauna acikin gidan ne amma ciki da fall da bayan gida acikinshi

Har Dan karamin kitchen dinta basai ta fito tsakar gida ba

Komai nasu aciki yake

Umma da Husnah sukaje kasuwa suka nemo akwatunansu masu kyau guda uku

Aciki akafara zuba kayan lefe

Wanda yanzu kusan duk asabar sai sunfita kasuwa

Dai dai gwargwado dai aka hada lefen ya shamsu

Aka kai gidansu kubra

Nan da sati biyu za adaura auren

Dubu ashirin ya shamsu yaba wa kubra tayi hidiman biki dashi

*****

Hakeem zaune  kan kujerar yana hada wani muhimman file

Sai Ahmad yashigo yace wai baka gama ba  har yanzu kasan time kuwa

Hakeem yace nagani ai nan da Kaduna dai insha Allah komai dare

Ahmad yace Allah yasa nidai kai nake jira kawai nagama shirina

Hakeem yayi dariya yace bantaba ganin ango merawankai irinka ba Ahmad

Ahmad yayi dariya yace ai gwamma ni kai inkatashi karawa ai bansan dokin dazakayi ba

Hakeem yayi murmushi dayake kara fito da zallan kyanshi

Yace tabbas kuwa lokaci yakusa zuwa inji ajikina nakusa samun choice dina sai dai bansan a inabane

Ahmad yace kai amma fa akwai rigima Dan madam Laila zatayi rikici bakadanba

Hakeem yayi murmushi yace zatawa kanta danzan iya komai akan matata da zan aura Dan itace zabina
Kaga kuwa ta taka a sannu

Ahmad yace wallahi man I like your style  gaskiya zanso Gina gidana kaman yadda kake handling naka

Hakeem yayi murmushi yace banbaka shawarar hakanba
Dan na tabbatar Aisha ba halinsu daya da Laila ba

Kagakuwa ba za amusu hukunci iri dayaba ko

Ahamad yace gaskiya Dan hankalin Aishat nagani yasa har nayi shaawar aurenta

Ya shamsu yashigo ya musu sallama suka amsa suka mika mishi hanu suka gaisa

Ya shamsu yace wa Hakeem gani yallabai

Hakeem yace dama zanfada  maka ne zamu tafi Kaduna

Sai nan da sati daya zamu dawo

Hakeem yadauko invitation card na auren Ahmad

Yabawa ya shamsu yace muna gayya tarka daurin aure

Ya shamsu yayi murmushi yace masha Allah
Allah yabasu zaman Lafiya

Sai dai ranar yazo dai dai danawa auren

Hakeem yakalleshi yace har ansa rana baka fada minba malam shamsu

Dama bakayi niyyar gayya tarmu bakenan kokana ganin inka fada ma bazamu bane

Ya shamsu yayi murmushi kawai yace aikuna kokari ma da aiki
Kuma har ga Allah bani tunanin inna Baku invitation zakuzoba

Saboda matsayinmu badayaba

Hakeem da Ahmad suka kalli juna

Ahmad yace haba malam shamsu karkace haka saikasa muga kaman mu ba mutane bane

Ya shamsu yace to afuwan

Nayi kuskure

Hakeem yace to yanzu dai bazamu samu zuwaba amma muna maka fatan alkairi

Tace ban account number din ka inbada nawa gudumawar asiyawa amarya kaji

Ya shamsu yace wannan  yana daga cikin dalilin dayasa naji fada muku zamanin yanzu kowa yana fama da kanshi

Dan Allah kabarshi karka damu kanka

Hakeem yace karka damu ni nayi niyya kuma kasan bakyau maida hanun kyauta baya

Ya shamsu yace hakane yakaranto wa Hakeem number account din

Shima Ahmad yanaji kuma ya kwashe number.

Hakeem yace zakaji alert Allah yabada zaman Lafiya

Ya shamsu yace ameen nagode

Sukayi sallama har wajen mota

*****

Da daddare suna zaune tsakar gida ya shamsu yace Abba da ina son ba wa manemin auran Husnah dama yaturo iyayensa

Kaga tana gama  makaranta sai aiyi aurenko

Baban yace ai nalura  yaron nan bashir kaman da gaske yakeyi

Umma ta ce sau biyu yana kawo mahaifiyarsa muna gaisawa

Shamsu yace alhamdulillahi gaskiya konina yaba da bashir

Kara shigowar sako yaji a wayarsa yaduba yaga alert ne na dubu Dari biyardaga professor Ahmad

Kafin yayi magana wani alert din yasake fadowa daga boss dinshi a office

Wato professor Hakeem

Shima dai dubu Dari biyar dinne yaturo

Sun hada mishi 1 million NIRA cas su biyu suka bashi

Nan shamsu yakalli mahifinsa yafada musu

Abba yace kai amma wannan uban gida naka Allah yasaka mishi da alkairi
Umma tace ameen wallahi ko a mafarki bamutaba tunanin samun dubu Dari nan kusaba

Ballantana har million daya Allah yasaka musu da alkairi

Kai kuma saika kazauna dasu da zuciya daya

Nan dai ya shamsu yakira Hakeem a waya yace ga Abba na zai muku godiya

Hakeem yace haba shamsu yanzu saboda kyautar da baitaka kara ya karya ba zaka wahalar da Abba wajen gode mana

To gaskiya indai Dan inbari Abba yagode min ne zankashe wayata

Insha Allah idan nadawo zanzo nagaisheshi da ka ina amma banda godiya tsakanin malam shamsu

Ka gaida umma da kanwarmu

Sai da safe
Dif
Hakeem yakashe wayarsa

Dama wayar ya shamsu a handsfree take duk su Abba sunji komai

Abba yace gaskiya duk inda akeneman shugaba nagari wannan yaro ya kai
Allah yarabashi da sharrin duniya  Lafiya

Ameen Ameen gaskiya dai bantabajin mekudi hakaba da Jan talakawa ajikinsa kamar wannan uban gidan naka

Nan dai suka ta tatattaunawa akan yadda za ayi da kudin

Abba da umma dai suka barmai zabi

Ya shamsu yace shikenan Allah yakaimu gobe aga yadda za ayi

Itakuwa Husnah Allah Allah take safiya tayi taje school taba wa aminiyarta labari

Za a ba copper bash daman turowa gidansu

Washagari Husnah da meenat suna zaune a inda suka saba zama

Husnah tabata labarin za a ba copper bash daman turowa gidansu

aikuwa gaban Meenat yatsinke ras

Wani tashin hankali ya ziyarceta
Tarasa meyake mata dadi

aikuwa har aka tashi daga school meenat batadawo dai dai ba

Tana kallo copper bash ya budewa Husnah gaban motarshi zai kaita gida

Dan tunda aka sanshi yaroki alfarmar zai dinga dawo da Husnah gida idan antashi

Da kyar aka yarda mashi Dan saida yahada da mom dinshi

Husnah tana daga wa meenat hanu Ina AMIN ABDUL HAKEEM kam batasan tanayiba

Ta Lula dunitar tunani

**
MEENAT tana zuwa gida tafada cinyar hajiya rukayya kakanta

Tafashe da kuka maitsanani

Hankalin hajiya rukayya yatashi Dan ta dauki soyayyar duniya ta daura akan 'yar jikan nata bakaramin so takewa Amina ba

Nan dai dakyar tasamu meenat tayi magana

Tace hajiya nashiga uku nakusan mutuwa

Wallahi idan ban auri copper bash hajiya zaku iya rasani dan mutuwa zanyi

Nan hajiya rukayya tace kwantar da hankalinki kimin bayanin komai

Nan meenat ta kwashe komai tafada mata

Ba abinda yafi burge Hajiya rukayya a labarin sai jin cewan

Bash Dan hamshakin mai kudine a kano

Tace kwantar da hankalinki kaman yazama naki ma anfama

Aure shida Husnah kuma yazama tarihi

Zanje Kaduna aiko
Zan baki mamaki bash da bakinshi zaice yanasonki

Next page

Your comments is needed fans

Kamar yadda nayi typing metsayi haka nakeson

Comments dinki da tsayi

Wallahi comments mai tsayi yana burgeni
Sosai

Ina yinku masoya AKWAI LOKACI😘😘😘😘😘😘

📝📝📝📖📖
[05/05, 11:08 AM] UMMU AFAN 🌹:
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA NA UMMU AFAN 🎗

🌹🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹🌹

🌹F.C.T.W.A🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITERS OF THE NATION🌹

🎗DEDICATE THIS PAGE TO adda khadija and shamsu ina yinki over sister
Dik ina ganin comment din ki akan novel di na
Wato AKWAI LOKACI💋💋💋💋

Daya bayan daya zakuji sunanku masoya AKWAI LOKACI FANS GROUP 💋💋 keep comments kawai 😘

🎗AKWAI LOKACI🎗

🎗PAGE 51 to 60🎗

Ya shamsu ya yagyara wa iyayensa gida dai dai gwargwado

Har anyi fenti sabo gida sai kamshin sabon fenti yakeyi da sabon siminti

Ya zuba wa umma sabbin kujeru dai dai karfinshi

Sannan shima ya zuba a dakinsu shida kubra

Yasai TV guda biyu dayasa wa iyayensa daya kuma yasa a sashinsa

Sannan kuma yama umman shi dinkuna kala biyar na fitan biki sai yama abbanshi ma kala biyar shima masu kyau shadda da kuma yadi

Umma har da hijab uku da ta kallamansu
Uku

Sai Husnah kuma yamata kusan kala bakwai dai dai karfinsa
Ya hada mata da mayafai guda biyar  da takalman ta hudu

Sai kayan kwalliya da dai sauransu

Yafi kashe wa Husnah kudi acewanshi ita tafi bukatar hakan

Yama kubra ma kayan fitan biki yace kartayi amfani Dana lefenta

Sannan kuma yasa wa abbanshi kaya a shago  Dan dama Abba yana shawa ar sana ar awu na hatsi

*****

Yauce ranar daurin auren  shamsu da amaryarsa khadija
Komai yatafi yadda akeso

ankai amarya dakinta dake cikin gidan  su shamsu

****

an daura auren Ahmad da amaryarsa Aisha
Suna shirin zuwa dinner ne Wanda PROFESSOR HAKEEM  ya hada wa babban abokinsa

Hakeem da Ahmad sunyi shiga iri daya wani hadadden suit suka saka ango yasaka baki nacikin ja

Sai Hakeem kuma yasaka brown colour na cikin sa fari

Duk Wanda ya kalli  PROF HAKEEM sai yasake kallonshi

'Yam mata sai rawankai suke musam man kawayen amarya

Laila ma taci ado cikin wani tsadadden less Wanda tayi order daga  malesia

Tayi  kyau kan nan yasha gashin doki
Fuska kuma yaci bleaching   kana ganinta dai kasan anci duniya

Ango yashiga mota zuwa gurin dinner

Hakeem yabude mishi bayan mota Laila kuma ta babbar kawar amarya kuma ta bude wa amarya dayan gefen tashiga

Hakeem ne zaija motar ahmad yace Man please kamin wata alfarma mana
Hakeem yace ina sauraronka malam ango

Ahmad yace kasan idan muisa wajen babbar kawar Aisha ce zata bude mata kofa tunda kai kadaine a gaban  motar ta shiga muje kawai

Hakeem yayi shiru alamun ya amince kenan

Shine rahma kawar amarya tashige gaban mota tana gaida Hakeem ya amsa a dakile kaman bayaso

Suna isa kuwa bayan Hakeem yayi parking  aikuwa har 'yan gulma sunje sun sanar da Laila cewan  ga Mijinta ya dauko budurwa a gaban mota

ai kuwa tafito kaman wata mahaukaciya dai dai lokacin da rahma kawar amarya take fitowa daga motar Hakeem

aikuwa rahma batayi tsammani ba sai taji mari kau sannan kuma akasa kafa aka kwasheta

aikuwa yazo da tsautsayi rahma tabuga kai sosai take kuwa ta suma

aikuwa cikin tsannanin bacinrai Hakeem yadauki hanu ya zabga wa Laila mari yasake kwasheta da mari

Nan fa mutane aka taru ganin wannan Abu da  Laila ta aikata
Nan da nan 'yan uwan rahma dama suma suna gun sukace basu yarda bayan ansa mata ruwa ta farka

Hakeem yace kinayin abin kika dama ina kyaleki idan zanyi aure kin isa kiha nanine

To barin fada miki daga yau kikasake min dabban ci irin haka wallahi zanyi maganin ki ban wawaiya kawai

Wasu da basusan suwayeba

Wata 'yar dattijuwa ta matso tace haba 'yar nan  Kinsan fa yaran yanzu ba a hanasu auren abinda sukeso koda kuwa iyayensu ne
Ballantana keda gani dai baki haifeshi saidai kizama yarshi aisai hakuri

Tajuya kan Hakeem tace haba d'ana da hankalinka zaka mari yayarka a cikin mutane akan mace

Wasu abin dariya yabasu wasu kunya wasu kuma haushi

Musammam meenat cikin gatsali tafito daga cikin taron

Tacewa matar nan dalla malama kirufemana baki
Wayafada miki  kanintane dazakisa mutane agaba da surutu  to banana ne itakuma mamana ne
Dan haka kikama gabanki bamason muna furci

Wato cikin tsananin bacin rai Hakeem yadanko Amina yayi mota da ita ya wurga ta ta tashi motar sai gida

aikuwa Laila tace shikenan zaikashe min 'yartawa Dan zata kwacewa uwarta 'yanci
Tana ihu tana kokarin shiga mota sai saiga motan police nan sunzo tafiya da ita 'yan uwan rahma kawar amaryace suka dauko 'yansanda aikuwa suka tafi da Laila

Hankalin Ahmad yatashi yace wa Aisha amarya tayi hakuri bari yakira akawo mishi mota subi bayan Hakeem Dan komai zaiya faruwa

Hakeem na isa gidansu yayi sashen sa Meenat ya dauki belt dukanta yasoma

Kuka sosai meenat take tana bashi hakuri

Wayyo Allah daddy kayi hakuri wallahi bazan sakeba yace Ashe baki da mutunci kikalli kaman wannan matar kimata rashin kunya ko

Abinda uwarki da kakanki  suka koya miki ko
To ba agidana ba Dan ubanki

Mummy hafsat ce yashigo da kyar ta karbi meenat agurin uban

Hakeem ya kalli mummy yace mummy Dan Allah bana son yarinyar nan ta koma gurinsu
Kwatata sunbata wa yarinya tarbiyya

Mummy hafsat tace wai meyafarune nan Hakeem yafada wa mummy hafsat komai  harda dabbancin da uwarta tayi  a wajen dinner

Mummy hafsat tayi salati tace yanzu wadan nan mutane bazasu canja haliba gashi harsuna Neman bata mana jika

Kaman daga sama kuwa suka ance sannu masu tarbiyya
Dana nasan ba Wanda yake haddasa fituna saike hafsat

To wallahi anzo gurin da banzan bariba dan me zaudauki hanu yata dukan matarshi acikin bainar jama a

Mummyn Hakeem tace aini abinda Hakeem yayi amin dai dai duk abinda Laila takeyi tasamu daurin gidinkine yaya rukayya

Hajiya rukayya tace wato kekikabashi daman yadauki karuwa a mota ko

Mummyn Hakeem tace ya isa haka yaya rukayya wallahi zanyadda da komai amma banda mummunan kazafi akan Abdul Hakeem

To wai ma da kuke wannan haukan wayace muku Hakeem bazai kara aure ba

ai Karin aure akan Hakeem wajibine Dan wallahi koshi baiyi niyya ba nizansashi aure dolene

aikuwa hajiya rukayya tafashe da kuka tace yanzu hafsat nizaki cewa mahaukata ina matsayin yar mijinki kidubi tsaban idona kice muna hauka

Mummy hafsat tace duk abinda yafaru kokuka janyo
Kuma wannan yarinya da kuka sangarta bazata koma wajenkuba

Zanriketa har Allah yasa tagane gaskiya tadawo hanya bakaman Ku da kuka bata ba

Hajiya rukayya tace wannan kuma baki isaba hafsat kinyi kadan kirabani da jikata

Mummy hafsat tace zancen kikeso

Tana amina fuuuuuu suka bar falon

Hakeem kuwa barin falon yayi zuwa dakinsa

Sukabar hajiya rukayya kaman tafashe dan bakin ciki

Wayar hajiya rukayya tayi kara taduba taga Suby ce kanwar Laila tace kekuma ya akayi

Suby cikin tashin hankali tace mama gamunan a police station ankulle anty Laila

Hajiya rukayya tace wani station din kuke

Nan tafada mata tafita zuwa police station din

Hakeem yana shiga bedroom dinshi wanka yashiga

Kafin yafito yadan kwanta yana tunanin bakin hali irin na Laila da 'yan uwanta

**
alhaji abubakar yana office din shi azaune saboda yayi baki daga India

Sai yaji kiran  yayarshi hajiya rukayya

Yadauka tare da sallama
Hajiya rukayya tafashe da kuka tace duk inda kake kazo gida ba Lafiya

Matarka da 'danka zasukashemin 'yata da jikata

alhaji abuabakar yace subahanalla ganin zuwa yaya kidaina kukan Dan Allah

Ya kashe wayar yadau hanyar gida

Yana zuwa yasamu yayansa hajiya rukayya a kofar gidanshi
Yafito amota da sauri yace mekefaruwa ne haka

Nan dai ta kwashe karya da gaskiya tafada mashi yace yanzu kishiga mota muji police station din ayi belinta
Inyaso sai mudawo gida a yi magana

Hajiya rukayya tashiga mota suka nufi can police station din
Suna isa tun kamin ayi parking suka ga Ahmad da Laila

Ahmad yaga motar daddyn Hakeem sai yakaraso gurin motar yagai da daddy

Daddy yace sunbaka belin kenan
Ahmad yace a amma dakyar suka bayar sai da nasa hanun zata je har gida tabawa yarinyar data sumar hakuri

Daddy yace Allah yarufa asiri kaima kayi kokari Ahmad Allah yabaku masu yimuku

Ahmad yace ameen daddy barin karasa gidan

Daddy yace wa Laila tashiga bayan motar sutafi tabude bayan tashiga

Ta madubi hajiya rukayya tace Dan Allah kalli yadda suka mayar min yarinya saikace wacce bata da gata

Alhaji abubakar dai baice komai har suka isa gida

Duk yatarasu a falo Hakeem na zaune daddy yace banji daddyn abinda yafaruba naji komai

amma ina insan kai Hakeem wace mata kadauko agaban mota nan Hakeem yawa mahaifinsa bayanin

Hajiya rukayya tace karya  kakeyi kana nufin Laila Karya zata maka

Mummyn Hakeem tace to ita Lailar uwarshice dabazata mishi karya ba

Daddyn Hakeem ya ce ban baki iznin maganaba hafsatu kiyi shiru

Mummy hafsat tayi kwafa

Nan dai daddy yayi musu nasiha meshiga jiki

Hajiya rukayya tace sai maganar yarinya sunce wai bazan koma da Amina ba

Daddy ya kalli Hakeem yace yazakayi haka bayan kuma yarinya dasu tasaba

Hakeem yace daddy idan har yarinyar nan zata koma to ta gaggauta fito da miji tana gama secondary school kawai aiyi aure

Dan wannan da irin tarbiyyar dasuka bata nan gaba zata iya fin karfin mutane

Mummy hafsat tace wannan shawarar taka tayi dai dai
Dan bazanso jikata ta acikin wannan rayuwar da ba asan nagaba ba

Hajiya rukayya tace kaga abubakar kashiga tskanina da matarka

Daddy Hakeem yace wa mummy hafsat Dan Allah karkisake cewa komai sai na baki dama

Nan alhaji abubakar yace  zata koma amma gaskiya nima anan naba da goyan bayan tafitar da miji kafin nan da tagama secondary school

Hajiya rukayya tace wannan ba abin muwabane
Abamu nan wani lokaci saurayinta zaizo dakanshi yagaisheku aitana dashi

Alhaji abubakar yace to alhamdullila  Dan Allah komai ya wuce

Ke Laila ba wa mijinki hakuri
aikuwa hajiya rukayya tace ya za ace tabashi hakuri bayan shiyakamata yabata hakuri daya dauki hanu ya tsinka mata mari acikin mutane

Ganin abinda hajiya rukayya takeyi yasa Hakeem barin falon yayi sashinsa

Yana fita suka hadu da Ahmad
Hakeem yace ango

Ahmad yace komaidai yakoma dai dai ko Hakeem yace barin shiga nashirya nazo muwuce

Muje musallami friends dinmu na nesa

Ahmad yace karka damu nagama komai

Hakeem yace yanzu har ka rakasu airport Ahmad yace kwarai

Hakeem yace amayar fa Ahmad yayi murmushi yace ai andade da tafiya da amarya

Dan dazu nakirata harsun huta ma

Yan uwanta ma sun kamo hanyar dawowa

Hakeem yace to ai sai musamu mushirya muwuce muma ko karnayi laifi dayawa agurin Madam Aisha

Ahmad yayi murmushi yace a haba aitasan komai

Idan taga bamuzo ba tasan abinda yatsare mu

Hakeem yace yau zaka shiga dakin amaryar ka

Barima kagani Hakeem yashige sashinsa

Yafada bathroom yayi wanka
Yana gama shiri cikin shadda marun colour ya balain masa kyau kamar danshi akayi shaddar

Yana fesa turare Laila tashigo
Tace daddyn meenat naga kaman tafiya zakayi baka sallamemuba

Hakeem ya watsa mata wani kallo

Yace mekuke bukata tace kayan abinci da na amfanin gida yace kizauna kirubuta duk abinda bukata zansa driver yakawo muku

Daga yau nabar baki daman da kikesamu harkike ganin kaman kinfi  karfina sai yadda kikayi dani ko

cikin tashin Hankali Laila tace Dan Allah karkamin wannan horon kasan nasaba sayan abinda nake bukata da kaina

Hakeem yayi murmushi mugunta yace nawa nakebaki dama

Laila tace dubu Dari uku duk wata

Hakeem yace hakane ko ta ce a hakane

Yace kedawa nabari agidan nan tace nikadai

Yace good yanzu duk wata zanturo miki dubu hamsin

Kekadai dai nasan zasu isheki

Yana gama fadan haka yayi waje da brief case dinshi

Haukane Kane kawai  Laila batayi ba
Amma hankalinsa yatashi sosai nan tadauki gyalanta tayi gurin  mahaifiyarta hajiya rukayya

****
Bayan wata shida  professor Hakeem zaune  kan  kujerar office din shi

Yadauki wayarshi yakira yaya shamsu

Ya shamsu yashigo yace  Barka dai yallabai  sannu da aiki Hakeem yayi murmushi yace yauwa malam shamsu

Yace ga wannan ya shamsu yakarba yace ina zankai yallabai

Hakeem yayi murmushi yace nakane malam shamsu zaka kaiya dubawa kagani

Ya shamsu yabude Aikuwa ya shamsu ya dago ido  yakalli   PROF Hakeem

Yace admission fa nake gani yallabai

Hakeem yace yes nasan kana da burin karatu a rayuwarka

Iyakacin zamana da kai na lura kai mutum ne mai son karatu

So yanzu ga dama nan malam shamsu zaka iya farawa nagama komai har registration da komai sai dai ka kai credentials dinka asa maka a file

Kuma daga Level two zakafara nariga nayi komai

A department of business administration

Ya shamsu baisan lokacin da tashiba yace yallabai gaskiya ba abinda zance da sai dai Allah yabaka abinda kake nema duniya da lahira
Allah ya jikan mahaifanka ya ramaka zuria

Hakeem yace ameen malam shamsu  na gode kwarai da adduarka a gareni

Sai dai ni har yanzu baka taba tambayata wani Abu da yashafi   rayuwata ba malam shamsu koba bukatar sanin daga ina nafito ne

Ya shamsu yayi murmushi yace zanso sanin tarihinka dakuma tarihin nagartarka a rayuwar alumma

Nan professor Hakeem yayi murmushi
Yabashi labarin rayuwarshi kaf bai boye mai komai ba

Ya shamsu yaja numfashi yace yanzu tun kana 20years kayi aure kenan

Hakeem yace kwaraikuwa  ina da 17 year old girl yanzu haka

Da mamaki ya shamsu ya kalleshi yace masha Allah
Gaskiya kai kam duk abinda ake nema a rayuwa Allah yabaka

Hakeem yace zakasan daughter nawa ma ai duk  sati tana zuwa ranar alhamis

Ya shamsu ko wacce kake cewa amina

Hakeem yace yes ita nake nufi

Ya shamsu yayi shiru  yace am sorry sir wallahi  duk azatona  madam dinkace

Hakeem yayi murmushi yace 'yata ne nacikina

Ya shamsu yace masha Allah wallahi gaskiya labarinka ya burgeni

Bude kofar office akayi Prof Ahmad ne yashigo yace

Kace kuna tare da malam shamsu ne Hakeem yace ai tundazu muke hira anan

Ahmad yabawa ya shamsu hanu sukayi gaisa

Ahmad yace wa Hakeem madam fa tagama abincin rana yakamata muje muyi lunch

Hakeem yace gaskiya dai nima yaka mata nasan abinyi

Kaga madam Aisha sai tadinga hutawa ko

Ahmad yace  Aisha ce zagaji wai caf yanzu kasan Allah da zankoma inje cin abinci nikadai sai tambayi ina kake baka biyoni ba
Duk randa kake azumi haka nake fama da ita

Hakeem yace Allah sarki madam tana tausaya wa marayan Allah

Ahmad yayi murmushi yace maraya  a kano ba

Ahmad ya kalli ya shamsu yace malam shamsu gaskiya yau Na kamaka sai munje kaci abincin amarya

Hakeem yace aifa dai kam tunda shi yana mana rowan abincin amaryarsa da kuma ladan da zamu samu wajen gaida su umma da Abba

Ya shamsu yayi murmushi yace bahaka bane banyi tunanin inna gayyaceku zakujeba shiyasa

Hakeem yayi murmushi yace saboda gamu aljanu bama cikin jinsin mutane ko

Ahmad yayi dariya yace zamu baka mamaki sai dai kaganmu agidanka

Ya shamsu yace ina zuba  ido ,nan dai kyar ya shamsu ya yarda suka je dashi cin lunch

Suna kan dining din Ahmad suna cin abinci itakuma Aisha tana kan two sitter

Tace wa Ahmad honey yaushe zaka kaini yawo kasan fa bansan kowaba a kano kuma inason inga gari

Ahmad yace zan hadaki da kawance da madam din malam shamsu kinga  saikije mata itama tazo miki
amma sai malam shamsu ya amince

Ya shamsu yayi dariya yace ina zata iya erea mu  ai sai mu

Hakeem yace kaidai kawai malam shamsu kace bazaka bar madam dinka suyi zumunciba

Ya shamsu yayi murmushi yace shikenan  Allah yashige mana gaba

Sukace amin

Dazasu tafi ne Aisha tace  wa ya shamsu Dan Allah agaisar mata da kawarta kafin suhadu

Ya shamsu yace zataji insha Allah

****

Bayan wata biyu da fara zuwa makarantar shi
Ankawo sadakin Husnah
Harda kayan lefe akwati gomashabiyu cas

Sadaki kuma naira dubu Dari biyu

Yanzu haka ana jiran suyi waec da neco ne kawai asha biki

Shakuwa ce maitsanani da kaunar juna tsakanin copper bash da Husnah

***

Meenat zaune kan carpet dinsu hajiya rukayya tadawo daga tafiyan datayine wajen boka Dan karbowa meenat maganin MALLAKA da zata mallake copper bash yazama nata

Hajiya rukayya tace a abinci zaki zuba mishi idan yaci zai kamu da soyayyarki Wanda ko uwarsa bazai mata Sannan kuma zaiji ya tsani Husnah aduniya

Cikin farincki amina tace kai Allah yabar minke kakus dina

Laila dake gefe tana kallonsu Dan itama jiya tazo

Laila tace hajiya Nifa ba abinda kika karbo min Akan daddyn meenat

Hajiya rukayya tace ai wannan yaro fa asiri bazai kamashi ba sai dai kawai musa a kawar mana dashi
Har lahira kinga masamu dukiya muyi yadda mukeso da shi

Meenat caf daddyn nawa za a kashe wallahi bazaiyi yiwuba
Haka kawai ita mummyn bata San yadda zata karbi kudi a ahanunshi ba sai ankasheshi

Hajiya rukayya tace to ai murasa yadda zamuyi da wannan uban naki ne jikalle

Meenat tace natabbata baza arasa wani hanyar ba kudaiyi tunanin

Husnah zaune a dakin amarya kubra tana asigment dinta

Kubra tace kedai Husnah kinji dadi wallahi wannan irin gashi aikoda shi zaki yaki mijinki balantana ga uwa uba kyau da diri duk

Allah yabaki Husnah tadago manyan idonta ta kalli kubra tayi murmushi

Tace anty kubra kenan sai kace ke

Kubra tayi murmushi tace zakicimin fuska ko ai idan dai kina guri muai saidai muyi shiru

Husnah tace banda zuga fa matar yaya

Husnah ta fashe da dariya ita kadai

Sai kubra tace meyabaki dariya
Husnah tace kawai danku nakeson gani keda yaya wannan irin kyau da kyau ai sai dai kuhaifo mana aljani Dan kyau fa

Kafin Husnah takarasa maganarta kubra ta dauki pilon kujerarta zata kwadawa Husnah

Husnah ta tashi ta gudu dai dai shigowar ya shamsu

Yace lafiya kekuma Husnah tace Lafiya qlw ya shamsu

anty kubra ce ta biyoni

Umma dake kan sallaya a faranda tace o keda kubra dai zanga ranar rabuwanku akwai drama

Ya shamsu yayi murmushi yace sai tabita ai

Umma tayi murmushi tace andawo Dan albarka ya makarantar

Ya shamsu yace alhamdulillah umma bara nayi wanka sai nazo muyi hira umma tace

To banana

Ya shamsu yashiga dakinsa yasami kubra zaune ta tashi tana mishi sannu da da wowa

Yayi murmushi Dan kullum son matanshi karuwa yakeyi saboda yadda take matukar mutunta 'yan uwanshi hakan nasa yana Dada jinta cikin ranshi

Murmushi yasakar mata yace kamu hanunta yace meya hadaki da kanwartaki

Kubra ta yi murmushi tace tsokanata tayi shiyasa tagudu

Wai karmu haifi aljanu Dan kyau fa

Ya shamsu yayi dariya yace ai haka tace
Shiyasa na tambayeta tamin shiru

Washagari da safe bayan  anfito break sai copper bash yakira Husnah office din sa Dan ta serving din abinci Dan baya break shima sai goma

Shiyasa daga gida akekawo mishi

Ba kullum yake kiran Husnah ba Dan idan yakirata bata zuwa Dan kare mutuncin kanta
Ba kullum ana ganinta a office din shi ba

Suna zaune itada meenat wayarta yayi kara ta dauka tace aslammu ailaikum

Yace wa alaikumussalam my love

Husnah tayi murmushi tace inajinka ranka yadade

Yace alfarma nake nema kizo Dan Allah ki serving dina break fast

Husnah takalli meenat tace kice to Dan Allah

Husnah tace shikenan ganin nan zuwa

Husnah takashe wayar ta kalli meenat tace meyasa kikasa na amsa mishi

Meenat tace tace haba kekuwa Dan ya roki alfarmar  yau dai ai sai kiyi mishi

Husnah tace bazaki gane  bane
amma tashi muje kiraka ni dama abinda meenat kesonji

Suna isa office din copper bash

Yace wa amina taje cikin motarahi zataga basket din abinci ta dauko mishi

Aikuwa amina cike da farinciki ta wuce class dinsu ta dauko maganin ta da zata sawa bash

Sai da ta bude flask din ta zuzzuba  dama soyayyan doya da kwai ne

Sai ruwan  tea

Aikuwa ta zuba ta dauka takai mai
Husnah tayi serving dinshi

Yayi dai dai lokacin komarwar su class

Husnah tace zata wuce class yace ita bazataciba
Tace ai yau alhamis suna  tana azumi

Yace yayi kyau  kikula min da kanki kinji ko

Tayi murmushi dimple dinta suka lutsa yace I like your smile

Husnah tace thanks

Ta wuce zuwa class Wanda tuni meenat tarigata

Yagama break dinshi  tsaf

Washagari jumma a

Dama bashir yasaba zuwa duk Jumma a

Husnah zaune tagama shirinta tsaf bashir kawai  take jira

Kubra tace gaskiya dai tunda yasaba kiranki kuma yasaba zuwa yakamata kikarashi kiji kolafiya

Husnah ta yarda da shawarar anty kubra

Takira bashir yakai sau goma amma yaki dauka sai a kiran karshe

Yadauka yace dalla malama me na damuna haka

Kebari nafada miki karkisake kirana daga yau banza Mara mutunci

Na tsaneki Husnah bana son jin sunanki kifita a rayuwata

Sadakina da kayan aurena duk za azo  karba  kafin yafadi wata magana

Husnah ta yanke jiki ta fadi

Ya yi dai dai da shigowar kubra

Aikuwa kubra tayi ihu umma da abba da ya shamsu suka zo

Next page

Your comments is needed fans

Ina dadin comment din Ku fan's😘😘😘😘

Ina alfahari da Ku 👍👍👍

📝📝📝📝📖📖📖
[05/05, 11:08 AM] UMMU  AFAN 🌹:
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA  NA UMMU AFAN 🎗

🌹🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹🌹

🌹F.C.T.W.A🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITERS OF THE NATION🌹

🎗DEDICATE THIS PAGE TO  MOM IMAN &HANIFA
MUCH LOVE TO YOUR COMMENTS SIS
KEEP IT UP🎗

Ina alfahari daku masoya novel din AKWAI LOKACI

daya bayan daya zakuji sunanku ina bin comments dinku sosai

Allah yabar zumunci😘😘😘😘😘😘

🎗AKWAI LOKACI🎗

🎗PAGE 61  to 65🎗

HUSNAH   kan cinyar umma ansamata ruwa ta farfado

Ya shamsu yace Husnah kiyi magana meya haddasa miki wannan suman

Husnah ba baki sai kuka
Abba yace ke kubra kukinsan abinda yafaru

Kubra tace gaskiya dai ba abinda yafaru sai takira bashir
Bansan meyace mata ba  kuma nasan tabbas abinda yasameta yana da alaka da bashir

Kafin suyi wata magana wasu mata sukayi sallama suka shigo

Umma ta sannunku da zuwa suka yauwa

Umma ta ce sannunku da zuwa sukace yauwa Allah yasa nan ne gidan su Husnah ba bata mukayi ba

Ya shamsu ya kallesu yace nan

Suka shiga yiwa gidan kallon wulankanci suna kebe baki

Dayar tace ni wallahi dama banga gamin kifi da kaska ba da za ace wai bashir yarsa gidan dazai nemi matar aure sai gidan matsiyata

Wato kubran ya shamsu wani takaici ya debeta ta tashi
Ta cakumo wuyar wacce tayi maganar

Ta wanke ta da mari zata kara mata ne ya shamsu yariketa

Kubra tace Dan Allah ya shamsu kabari
Nakara mata
Inbanda cin mutunci kishigo har gidan mu kuce zakuci mana zarafi

To wallahi ubanku yayi kadan

Ita wacce aka Mara tace kika mareni to wallahi sai kinyi da nasanin marina

Kuma abinda yakawo muda ma munzo abamu kayan auren mu da sadakinmu

Mai auren yace bayayi mudama bason gidan matsyata irinku mukeba

Cikin tace kune kuwa babban matsiyata wadda basusan darajan nagaba dasuba

Abba yace wa kubra shiga daki

Kubra tabi maganar Abba  tayi dakin

Abba yace wa ya shamsu fito musu da kayansu

Ya shamsu yafito da kayan daya bayan daya

Umma ta ce kuna iya kwashewa kufita mana daga gida ko

Ita wacce aka Mara tace aiko bakuce mufita zamu fita ehe

Ya shamsu yace ke idan kina rashin kunyarki ya tsaya iya kan dai dai ke banda  iyayena

Kwarjinin ya shamsu ya musu suka kasa mishi rashin kunyar

Nan da nan suka fara jidan kayansu suna fita dashi

Ya shamsu yashiga daki yadauko musu sadakinsu yakai musu har gurin mota

Yace gashi sai Ku hada basai wani yasake zuwa mana gida

Suka karba shiru Dan sunkasa magana ma

Ya shamsu yashiga gida yaga yadda Husnah take kuka yace kiyi shiru kidaina kuka kinji yar kanwata

Allah zai miki canji da mafi alkairi

Umma tace gaskiya yaron nan yabani mamaki yanzu memuka mishi da zai mana wannan cin mutunci

Abba yace ai sai agode wa Allah ba akaiga aurenba

Da anyi auren ne ya wulakanta mana yarinya ai bazamu ji dadi ba

Ya shamsu yayi ajiyan zuciya yace shiyasa ba kuwani maikudi ake yarda da soyayyrashi akan talaka ba

Yayi amfani da  talaucin mu ne yasa har ya iya yin abin da yayi

Amma bakomai watarana sai labari

Shiyasa ni kwatata yanzu bazan sake wa Husnah auren mai kudi Ba

Gwamma ta auri dai dai ita sayi arzikin tare zaifi ganin mutuncinta

Umma ta ce wallahi na goyi bayanka
Dari bisa Dari

Abba yace muna namune kuma Allah na nasa Allah yazaba mana abinda yafi alkairi

Sukace amin

Nan akayi ta rarrashin Husnah da kyar tasamu tayi shiru

***

Satin Husnah biyu bata je makarantaba school ba saboda rashin Lafiya datayi

amma yanzu jikin alhamdullila
Dan tana ma shirin zuwa school gobe insha Allah

Washagari Monday da safe Husnah tashirya cikin sabon uniform dinta Wanda ya shamsu yadinka mata

Tayi kyau sosai tasaka read cap dinta da belt dinta na head girl

Bayan ta fito tayi wa umma sallama umma tace Allah miki Ibarka kinje Dan kicire komai aranki

Tace umma namiki alkawari cire damuwa daga raina

Tawuce bangaren ya shamsu
Ta Dan bubbuga kofar ya shamsu  tace ya shamsu nagama mutafi yace OK daman kenake jira

Suka fito tare da kubra tana rataye da jakar mijinta

Ta kalli Husnah tace kai tawan wallahi kinyi kyau sosai

Husnah tayi murmushi tace anty kubra kenan ya Shamsu

Mutafi kasan anty idan tafara sai tasa muyi latti

Kubra tayi murmushi tace to Dan Allah kisayo

Wannan kunun ayar da kike kawo min

Husnah tace karki damu
Zantaho miki dashi
Kubra yauwa kanwata

Nan dai ya shamsu da Husnah suka fita yatare musu  keke napep

Yabata dari biyar tace kai yaya shamsu yamin yawa ai

Ya shamsu yace ai nasan bakya azumi Dan haka kiyi amfani dashi kiyi break karkizauna da yunwa

Husnah tace wallahi umma ce ta hanani yin azumin wai saina warke

Ya shamsu yace ai gaskiyar tane
Gwamma yar kanwata tayi katuwa

Husnah tayi murmushi tace nagode yaya

Ta shige cikin school dinsu

Tana shiga an buga assembly  nan ada sauran prefect din suka tayata
Shirya yara Assembly

Nan dai Husnah ta hau kan stage tafara control din data sabayi

Bayan angama assembly principal ta aika akira mata head girl dinta Husnah

Tace mata nakiraki ne nabaki hakuri akan kinyi rashin Lafiya har natsawon sati biyu school bataje tadubokiba

Husnah tayi murmushi tace mummy ai an wakilta prefect sunje sun dubani

Mummy principal tayi murmushi tace ai duk da haka yakamata a hada da malamai

amma dai muna Neman afuwa
Husnah tace wallahi mummy bakomai aikema  bakya gari da kinje

Nan mummy principal tace bata wani envelope tace ga wannan kikai gida

Husnah tace to mummy

Nan principal tabata daman ta koma class

Husnah nazuwa class taga meenat sai alokacin take zuwa

Husnah tayi murmushi tace ai wallahi aminyi bakida kirki
Banda Lafiya kokije kidubani ko

Amina ta kalleta sama da kasa tace Allah yabaki Lafiya

Abin yaba wa Husnah mamaki
Har zatayi magana sai Ku ma tafasa

Dagana kuma malamin su na
Math's yashigo

Ana cikin musu teaching wata daliba tayi excuse sir copper bash yana kiran anty amina Hakeem

Sir yace amina Hakeem
Meenat tace yes sir

Yace oya tashi kije
Kafin amina ta fita sai da tajiyo taga ko Husnah tana kallonta

Itakuwa Husnah batasan tanayi ba
Dan ita kosunan bashir bata son ji tatsaneshi sosai

Har aka fita break amina batadawo ba

******
Yauce su Husnah suke graduating a school dinsu

Aka kawata hall dinzasu yi taron aciki

Principal bata ba da damar graduating students Susa kayan gidaba wato personal wear's kenan

Shiyasa duk inda kaga SS 3 zaka gansu sunsha guga sunsha kyau

Dan ba hana suyi make up ba

Duk prefect kowacce da hulanta akanta sunjeru a kujera na musamman sai  kuma sauran

graduated students dinsuma suna nan akujera ta musamaman

Husnah ma duk 'yan gidansu sunzo mata Abba ne kawai baisamu zuwaba amma ya shamsu da anty kubra da umma duk sunzo

Amina Hakeem  dakyar tasamu daddynta Hakeem yace zaizo

Ahmad da amaryarsa sai Hakeem sukazo sai mamanta da kuma hajiya rukayya duk sunzo

Hakeem tunda yazauna yake ta fama da wayarsa

Dagowar da Ahmad zaiyi yaga ai anzauna kusadashi
aikuwa dai ya shamsu ne da anty kubra umma kuma tanacan bangaren dattijai mata

Ahmad yace kaga ikon Allah malam shamsu kai ne anan kokuma wa

Ya shamsu yajuyo jin ankira sunanshi
aikuwa yaga  su Ahmad da Hakeem
Hakeem ma jin an ambaci sunan malam shamsu

Yasa yadago mai suka yi murmushi gadayansu

Nan ya shamsu yabasu hanu suka gaisa

Yace wasuka zowa Ahmad yace daughter dinmu ai nan take karatu

Kaifa yace nikuma kanwata ce anan

Kubra tace ina wuninku  Hakeem da Ahmad suka amsa

Ahmad yakalli inda madam dinshi Aisha take  yatashi yaje yarada mata magana akunne aikuwa Aisha ta task da sauri

Tana zuwa ta kama hanun kubra tace alhamdullilahi yau dai nima na hadu da kawata

Kubra ma dayame wayayyiyace tace nima naji dadin haduwata dake

Nan Aisha taja hanun kubra suka koma gurin su daban

Nan kuma ya shamsu da Hakeem da Ahmad suka can gaba wajen special guest

Nan akafara taron da addua

Can principal tafara jawabinta kamaryadda aka saba

Daga can kuma ta ce itada kanta zatakira best student of the year

Wanda duk shekara akeba principal dama tazaba da kanta ta kuma bata kyauta duk karshen shekara haka akeyi

Wani daga cikin teachers dinsu ya tashi yakarbi Mike din hanun principal da list din hanunta

Yafara kiran suna kaman haka

Best student of the year
Kowa ya kasa kunne

ASMAU SULEIMAN SHAMSU

aikuwa duk student aka dauki tafi raf raf raf

Dan daga malamai har student sunsan Husnah ta cancanta sosai

Cikin nutsuwa Husnah ta tashi ta isa gurin principal
Nan principal tace wazata kira ya tayata karba
Husnah tace wa principal  ya shamsu za akiramin

ya shamsu suna zaune duk hankalinsu yakoma kan head girl
Shi ya shamsu baifada musu wacece kanwar tashiba

Sai jisukayi ankira ya shamsu yatashi cike da alfahari da 'yar kanwarshi bata bashi kunya kokadan

Ahmad da Hakeem suka hada ido
Ahmad kaddai itace kanwar tashi

Hakeem yayi murmushi yace ga zahiri amma fa yarinyar taburgeni matuka
Yayi maganar yana kallonsu Husnah

Cike da mamaki Ahmad yakalli abokin nashi

am I dreaming ?
Man what are you saying

Hakeem bai kalleshiba murmushi kawai yayi ya dauke idonshi daga gurin  su Husnah ya mayar da kanshi kan wayarshi

Murmushi Ahmad yayi dai dai lokacin ya shamsu yadawo yazauna

Ahmad yace kanwarkace ya shamsu yayi murmushi yace yar karamar kanwata kenan

Yace masha Allah
Allah ya albarkaci rayuwarta

Ya shamsu da Hakeem suka ce ameen

Daga nan kuma sai akafara ba wa prefect satificate dinsu  ya rage sauran na social prefect da Head girl

Aka kira social prefect AMINA HAKEEM ABUBAKAR

Nan akabata sertificate dinta da kuma gift dinta maman Laila ita tayata karba

Hakeem kallo daya yamusu yacigaba da abinda yakeyi

Can akakira me gayya mai aiki wato head girl

Husnah taje ta karba itada yaya shamsu principal Tamika kyautar aka musu hoto

Duk wani kyauta da akerabawa  Husnah ita takarbi na farko abin yaburge kowa ana karshen

Husna ta tashi zata karba sai kawai tafashe da kuka Dan tasan koba komai yayanta zaiyi alfahari da ita

Principal ta rungumeta tana share mata hawayen

Tace asmau Allah ya albarkaci rayuwarki

Ya shamsu yaji dadin adduar  principal

Yace Ameen hajiya mungode Allah yabar zumunci

Nan fa students sukayi tazuwa suna daukar hoto  da Husnah suna mata fatan alkairi

Masu bata gift nabata kai gaskiya Husnah tayi farin jini sosai har malamai suna tururruwar  hoto da ita

Meenat zaune abin duniya yadameta tana matukar jin bakin ciki   abin da kefaruwa da  Husnah

Laila tace wai ita wannan yarinyar fa saikace aljana komai ta handame ita kadai

Meenat tace kyaleta dama yunwa ne yakawota school din Dan dama 'yar matsiyata ce

Scholarship taci tashigo

Hajiya rukayya dole ai yanzu naji batu

Motar school ce ta kaiwa Husnah gift dinta har gidan

****

PROFESSOR HAKEEM   yana zaune cikin falonshi  kusan sati kenan da graduation dinsu Husnah amma kullum da ita yake kwana da itayake tashi aranshi

Kuma tunda yake a rayuwarshi bai taba saka 'ya mace a rayuwarahi  ba

Kuma a yadda ya fuskanci zuciyarshi takamau son 'yar baby nan

Shida kanshi yake wa kanshi dariya

Ya duba agogo yaga sai yanzu  8:30  nadare tayi
Yaje ya hada Kofi

Yanasha  kadan yana tunanin Husnah

Abinda baisaniba shine Ahmad yadade a bakin kofa yana kallon abokin nashi daya fada shauki

Ahmad yayi gyaran murya hade da sallama

Hakeem  yajiyo suka hada ido da Ahmad

Ahmad yace abokina wai  meyake faruwa ne
Kwana biyu naganka  kaman akwai wani Abu

Hakeem yayi murmushi  tareda kurbar copee yace  shine kabar matarka kazo gulma ko

Ahmad shima dariyar tare da dauko lemu maisanyi a fridge

Yadawo yazauna

Ahmad yace inkarashida gulma kaikaso

amma dai ni bazan bar nan ba sai kafada min

Hakeem yatashi yakoma bayan kujera yace
Ahmad  am  in love

Ahmad yayi dariya yace daman nasani

Duk wannan boye boyen naka duk kallonka nakeyi

amma gaskiya idan har kasamu yarinyar nan kayi  sa a wallahi

Hakeem yace wace  yarinya kenan tunda nidai  ban fada wacce nakeso da bakinaba

Ahmad yayi dariya yace karka rainawa wa kanka hankali mana

Kawanwar shamsu koba hakabane

Hakeem yayi murmushi yace amma ya akayi kagane hakan dawuri

Ahmad yace shekaru talatin muna tare fa dan uwa taya za ayi barangane matsalarka ba

Hakeem yayi murmushi yace hakane amma bazan fada ba sai na musu

Jarabawa daya kaga daga tabbatar gidan danaje Neman iri

Next page
Your comments is needed fans❤❤❤❤❤

Anfara wasa fa fans❤❤❤❤

Sainaji ku
[05/05, 11:08 AM] UMMU  AFAN 🌹:
🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗

BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

🎗HAKKIN MALLAKA  NA UMMU AFAN 🎗

🌹🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹🌹

🌹F.C.T.W.A🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITERS OF THE NATION🌹

🎗DEDICATE THIS PAGE TO sis JIDDER  (BAEWAR  ALLAH)
WANNAN PAGE IN NAKI
SABODA KAUNA DA KIKE  NUNA WA WANNAN
NOVEL NAWA NA
🎗AKWAI LOKACI🎗
Allah yabar zumunci keep it up 😘😘❤️❤️

Masu comment ina sane da Ku kafin na kamla littafin nan duk sai kunji sunanku daya bayan daya so kucigaba da bin ummu afan takuce ❤

🎗️AKWAI LOKACI🎗️

🎗️PAGE  66 to 70🎗️

PROF HAKEEM  zaune kan resting chair dinsa a bakin sweeming fool yana shan iska dan yanzu yafito daga cikin ruwan

Wayarshi ta daukara yana dubawa yaga dalibata wato mummynshi kenan dan sunan dayasa mata kenan

Bayan sungaisa Hakeem yace mummyna albishirinki mummy hafsat tace goro

Yace naga matar aure a kano fa

Cikin tsananin farin ciki mummy hafsat tace alhamdulilla naji dadin wannan albishir

Yaushe zakazo katura mahaifinka gidansu yarinyar

Hakeem yayi murmushi yace daliba kenan ai ban ma taba fada wa yarinyar ba nikadai nake kida kuma nake rawa na

Mummy tace shirme ni harkasani ina murna to idan bazaka iya fada mata nika nuna min gidansu yarin sai naje

Ayau saina zo kano wallahi akanka my son

Hakeem yayi murmushi yace nasani mummy na

Nasan zakifi kowa farinciki shiyasa nafada miki tunkafin na fada wa yarinyar

Sai mummy Kinsan masu soyayyar Allah kadan suke aduniyar nan

Kuma dadin da dawa ma yarinyar danagani din ba masu karfi bane

Kinga idan naje kaitsaye Kuma akayi rashin  sa a saikiga sun soni don kudina badan Allah

Mummy taja numfashi tace hakane son sai dai zuciyata tana bani bazataba son abinda baidace dakaiba

Hakeem yayi murmushi yace Kinsan menakesonyi  mummy tace a a son sai kafada

Yace zan jarabasu nagani zanje  amatsayin  talaka banida komai

Ingani zasu karbeni kokuwa

Mummy tace hakan ma tayi son dina
Kuma ina maka fatan alkairi

Insha Allah zasuci duk wani jarabawar da zakayi musu

Wasunan surukartawa Hakeem yayi murmushi mummy ta sosa mishi inda yake mai kaikayi

Yace ai harma tazama surukarki
Mummy tace aiba surukaba ma 'yata zama son

Hakeem yayi murmushi yace asmau amma anakiranta da HUSNA

kai masha Allah ashema babban suna ne da ita

Insha Allah asmau zata Mata agareka tun kafin naganta naji inasonta

Hakeem yace shiyasa nakeson Ku iyayena kuna matukar daraja abinda nakeso

Allah yabani matar da zata bauta muku da zuciya daya badan kudinku ba ko kudin danku

Mummy hafsat tace aikasamu son zantayaka da addua

****

Washagari  Hakeem Bayan sungama komai ya shamsu yazo musu sallama zai wuce gida dan karfe hudu yake tashi a lectures

Ahmad yace wa ya shamsu yaufa kafanmu kafarka zamuje mugaida Abba da umma

Dan idan muka biye maka bazaka gayyace zuwa samun ladan nan ba

Ya shamsu yayi dariya yace shikenan idan kun shirya muna iya tafiya

Hakeem yace na dauka zaka kawo wani excuse ne ince ai ba umma kai kadaibane muma namune

Ahmad da ya shamsu sukayi dariya

a motar Hakeem akatafi  ya shamsu agaba Ahmad yabaya

Ya shamsu yana nuna wa PROF HAKEEM hanya

******

HUSNAH  ce zaune tsakar gida tagama aikin gidan kenan tas ko ina yadau kamshi

Ita kuma anty kubra tana kitchen tana hada abincin dare Wanda sudama kafin biyar sungama komai sun zuba a kula

Kuma aikin sukayi Husnah da kubra yau idan kece da aikin gida to dayar kuma saitayi abinci

Yau Husnah ce da aikin gida

Tagama komai da wuri tana wa anty kubra dariya tana kitchen dan yau ya shamsu yace ayi tuwon semovita miyar kubewa danya
Har kudin danyar kifi yabayar

Anty kubra tace zanrama ai Allah yasa ran girkinki Abba yace sakwara yakeso

Husnah tayi murmushi tace kai ai danagane kuskurena kuwa

Umma datake jinsu tace tun tuni kinjuye ruwa Yakama kishiga kiyi kisamu kifito kije min aika ko

Husnah tace to umma
Umma ta kalli kubra tace sannu kinji kubra Allah dai yamaku albarka yabaku masu yimuku kuma

Kubra acikin zuciyarta ta amsa da amin dan tana jin kunyar umma idan tace Allah yabasu masuyi musu

Husnah tafito daga wanka tayi dakinsu tashafa mai tadauko powder tashafa sai kwalli sai tasa lips glow alebenta

Tabude akwatin kayan ta tafara zaban wadda zata saka

aikuwa idon ta yakai kan wani material pink da kuma ratsin baki ajiki Wanda ya shamsu yamata a bikin shi

Tunda tasa a biki batasake sawaba

Sai tadauko shi tasaka dinki duguwa Riga ce
Daga sama ya dameta sosai dan Husnah fa akwai kayan aiki

Shiyasa umma bata cika barinta fita da gyaleba saidai hijabi dan Allah yamata kira

Husnah takalli kanta a madubi itakanta tasan tayi kyau sosai

Sai kuma tasan dakyar umma zata bari tasaka gyalen material din

Itakuma yau mayafi takeson yafawa

tace barin gwada dai tagyara gashinta tadaure da ribbon fari
Kafin tayafa gyalenta dan   bata saka dankwaliba
Kota saka dankwalima abanza

Dan bayazama akanta sabonda tsantsin gashinta

Tadauko turarenta tafesa kafin tadauki Jakarta na suwaga pink da takalminshi duk pink tasaka
Kai masha Allah da wannan kyakkyawar hallita

Tafito tace umma nafito
Umma ta kalli 'yartata tace au da wannan gyalen zakifita

Husnah tace Allah sarki umma na gyalen kayan nefa

Kuma kinga kayan ai yana da fadi sosai
Kafin umma tayi magana anty kubra taleko tace umma dan Allah kibarta wallahi tayi kyau kuma kinga ai kayan yana da fadi

Umma ta ce wato bakinku daya ko to shikenan kije Allah yakiyaye hanya

Husnah tace to umma baki min bayaninba umma tace kinci gidanku yau kika saba karbomin zuman ne

Husnah tayi murmushi dimple dinta tsuka lotsa sosai
Tace to ummana afuwan nadauka bakaman na kullum bane

Tayi waje sukace mata adawo Lafiya

adai dai  kofar gidansu ya shamsu yanuna wa Hakeem yayi parking

Suka fito atare Ahmad yace kashiga saikamana iso

Ya shamsu yace to shikenan yaya cikin gidan alokacin umma ce kadai a tsakar gida kubra ta fito mata da taburma
Dan anna suke hirar Daren su gadaya

Ya shamsu yayi sallama umma tace a a ubana har andawo yace a umma yagidan nan dai yagaida umma kafin yace umma daman su ogana na office ne sukazo gaisheku

Umma ta ce shine kabarsu a waje kuma sushigo ciki dan Allah haba waje

Ya shamsu yaje ya musu iso zuwa cikin gidan

Umma ta ce kashiga dasu daki Ahmad yace a umma mu kusa da ummanmu zamu zauna basai munshiga dakiba

Umma taji dadin har ranta tace to shikenan 'ya'yan ummu kuzauna nan suka kwashi gaisuwa agurin umma ta amsa cike da farin ciki
Nan kuma ta musu godiyar hidimar dasukeyi da su

Hakeem yace haba umma ai mu da shamsu Yanzu munzama 'yankuma bagodiya tsakaninmu ai yiwa Kaine

Umma ta ce hakane kam Allah yake mutum da mutum
Kodai Allah yasaka muku da aljanna

Umma ta ce wa shamsu ubana aisai kayi maza kaje nan shagon mati ka karbo musu lemu mai sanyi da ruwa

Hakeem yace haba dai umma mufa ba bakibane

Komai ummanmu tabamu cizamuyi
Ba umma ba harta ya shamsu yaji dadin wannan kara da Hakeem da Ahmed suke musu

Sallmar HUSNAH  ce yasa Hakeem daga ido yakalli hanyar waje aikuwa suka hada ido cikin ido
Husnah tayi saurin dauke idonta    dan dama akasi aka samu ta kalleshi

HAKEEM yasamu Kansa cikin wani yanayi Wanda yakasa  fassarashi  ba Ashe ganin da yayi mata a school ma tafi haka

Husnah ta durkusa har kasa tagaishe da su Hakeem Ahmad ne karfin amsawa shikam ogan ba baki
Yakasa komai ne

Ba Wanda ya kula da canzawarshi sai Ahmad

Ahmad murmushi yayi shikadai

Kubra tafito tagaishesu

Ahmad yace ai kawarki basan zamuzo ba dakinganta

Kubra tace dan allah yakawo mata Aisha Dan zaman da sukayi a gurin graduate dinsu Husnah

sun saba sosai

Ahmad yace ya mata alkawari ran sabar zai kawo Aisha tamata wuni daga nan tagaida umma

Umma ta ce Allah yakawo ta Lafiya umma na maraba da ita

Husnah da kubra suka kawo musu abinci a kula da biyu suka ajiye
Husnah tadauko plate guda biyu da serving spoon duk ta ajiye musu

Sai ta dauki jug ta kawo musu ruwa  maisanyi na randar umma  ta kawo musu da cups biyu

Umma ta ce maza hada musu zobo  Husnah
Husnah tace to umma ai na dafa tunda dazu hadawa kawai zanyi saidai ba kankara

Ya shamsu yace hada barin karbo kankara

Ya shamsu yafita  jimawa kadan sai ga shida kankara yakawo yaba wa husnah

Hadaddan zobo ta hada Wanda yasha kayam kamshi da cocumba

Tasa musu a jug shima takai musu kafin ta wuce dakin anty kubra umma tace bara nashiga kuci abincin Ku

Ya shamsu yace bissimillarku kuci abinci

Hakeem yayi murmushi yace aiko baka fada ba

Ahmad yayi murmushi dan yasan dalilinsa na fadar hakan

Hakeem yayi serving kanshi

Tuwo daya yasaka sai sai yasa miyar baiga ruwan wanke hanuba sai

Yace yaya shamsu ruwan wanke hanu dan bana cin tuwo da cokali

Ya shamsu yayi dariya yace amma yallabai kaso barkwanci ninekuma yayan
Hakeem yayi murmushi baice komai ba

Ya shamsu yakira Husnah takawo ruwan wanke hanun

Takawo ta ajiye  gaban ya shamsu shikuma ya mikawa Hakeem gabansa

Hakeem sosai yaci tuwon dai Bayan ya cinye Leda daya sai ya kara Ahmad nema yarage kadan

Ya shamsu yace haba yallabai dan Allah kacinye wallahi umma zataji dadi

Hakeem yace rabudashi ya shamsu tsoron madam Aisha yakeyi kartatsareshi sai ya cinye abinta yakasa Bayan yacinye na gidan umma

Duk suka kwashe da dariya
Hakeem yatsiyayi zobon da Husnah ta hada musu yasha

Aikuwa yaji kunnenshi kaman zai yanke dan dadi
Kodan ya hadu da soyayyane oho

Kafin yayi magana Abba yashigo dattijon arziki

Duk suka mike tsaye sai da Abba yazauna suka zauna suka kwashi gaisuwa

Ya shamsu yagabatar dasu

Abba yace a manya baki ne damu agidan Ashe
Nan shima yashiga musu godiyar hidimansu akansu

Sun dan taba hira kafin Abba yashiga daki yabarsu nan da ya shamsu

Hakeem yace Gaskiya ya shamsu wannan zobon asamin awani Abu natafi dashi zansha zuwa dare

Ahmad yace narigaka azuci karigani a baki dan kasan duk inda nasha abinda yamin dadi sai narage wa madam

Hakeem yayi murmushi yace kai man kafadi gaskiya

Ya shamsu dai dariya yakira Husnah yace tasamo jugs guda biyu  ta zubo zobo tace to

Hakeem tabita da kallo  komai na yarinyar yamishi Dari bisa Dari
Tana da duk wasu qualities din dayake bukata ga mace

Husnah ta zuba takawo ta ajiye
Ta yigaba abinta

Sai da akakira magrib suka yi sallama da su umma da Abba da anty kubra

Husnah tana kan sallaya idan tayi magrib bata ta shi sai tayi isha

Hakeem yaso yasake ganin Husnah

Amma taki fitowa

Ahmad ya ajiye bandir din kudi 'yan dubu dubu yace a ba wa kanwarsu tasai kayan kwalliya

Ya shamsu yace dan Allah karmuyi haka kudauki kudinku

Ahmad yace ai nariga na ajiye kuma ma aibakai muka ba ba kanwarmu muka ma kyauta

Da kyar ya shamsu yabar kudin nan

Suna cikin mota Hakeem ya karya kwana zuwa baibi hanyar gida ba

Ahmad yace man yana zaka kaimu kuma Hakeem yayi murmushi yace sa ido kawai kayi kallo man

Ahmad yace OK baringa ikon Allah to

Hakeem yayi parking adai dai gurin wani malamin almajirai  suka sauka

Malam na ganin HAKEEM yataso yazo sannu da Zuwa professor  Hakeem yayi murmushi suka gaisa da malam Garba

Malam Garba yace mukarasa daga taburma nan suka karasa

Hakeem yace malam bawani Abu yakawoni ba illa Neman wata alfarma

Malam Garba yace alfarma kuma alhaji da kanka
Hakeem yace a malam

Aure nake nema malam

Amma kasan rayuwa ta baci yanzu sai aureka badan anasonkaba sai dai don abinda kakedashi

Malam yace hakane

Hakeem yaja dogon numfashi
Ya kalli Ahmed da ya kagu yaji dalilin abokin nashi nazuwa nan

Hakeem yace malam zanje Neman aure da sunan talaka talakan ma futuk Mara iyaye

Koda anzo Neman tarihina guringa za azo dan
Kai zanfada a matsayin malamin danayi karatu agurin shi

Kai kuma inason kanuna tun ina karami aka kawo maka ni

Wannan kadai nakeson kamin malam

Malam Garba yayi murmushi yace gaskiya alhaji kana da tunani mai kyau Allah ya tabbatar da alkairi

Hakeem da Ahmad suka ce amin malam

Nan suka wa malam sallama Hakeem yadauko bandir din kudi yaba malam yace gashi a rabawa yara sadaka

Ya ba malam wani kuma yace Gashi wannan nashine

Malam Garba yayi ta musu addua

Acikin mota Ahmad yace amma meyasa makayi wannan tunanin haka Hakeem

Ahmad yace kana nufin bazasu ganeka ba wai kome

Hakeem yayi murmushi yace duk zan shirya wa hakan

Ahmad yace Allah yasa amma dai yakamata duk wani abinda zakayi wallahi kayi sauri kafin

wani yariga ka

Hakeem yayi murmushi yace inaji ajikina wannan yarinyar rabonace

Ahmad yace to tunda kana da tabbacin haka
Meye na gwada ta kuma

Hakeem yace inason nasan mena aura ne kuma rayuwata zanbata kaga kuwa ina bukatar bincike sosai

Ahmad yace sai prof komai naka daban ne wallahi gaskiya bazan boye maka ba I like your life style Bros
Keep it up

Hakeem yayi dariya yace baka jiya abokina

Ahmad yace ai bazangaji

Komai naka is so special

****
Bayan sati uku Hakeem yayi order na fuska daga India

Yau yakesaran za akawo mishi

Hakeem ya zaune wani abokin
Wayar shi tadau kara yana sai yaga number din Wanda  yaba sautun siyo mishi fuska

Yadaga wayar yace badai  har kun isoba
Doctor isah yace gani ma acikin school dinku

Hakeem yace what's a surprise
Ganin zuwa

Hakeem yafita yaje yashigo da doctor isah

Nan Bayan sungaisa doctor isah

Yafito mishi da sakonsa

Hakeem yakarba yace masha Allah kuma gaskiya kayi yadda nace

Doctor isha yace to ai  kasan aikan manya irinku  ba kasafai akacika muku shirme ba

Hakeem yace zakafara kaima ko

Doctor isha yayi murmushi yace  ansamu ragi sosai yallbai dan Rabin yakai dubu Dari da hamsin

Hakeem yace OK zaka iya barinshi a wajenka  yazama naka doctor

Doctor yace a yi haka yallabai
Hakeem yace karka damu ai kamin komai

***

Da daddare Hakeem ya fesa wanka yadauki jallabiyya yasaka yadauko fuskarsa yasaka  kafin yadauki carbi yarike a hanu

Yadauko wayar Nokia da yasa akasayo mishi second hand wacce duk tasha dauri da roba

Ya kalli kanshi a madubi shida kanshi yaba kanshi dariya

Yadauki kudi yan hamsin da kuma 'yan goma yasaka a aljihunshi

Ya kulle gidanshi yafita zuwa gidan Ahmad yayi sallama
Maigadin yace sannu malam daga ina haka kuma gurin wakazo

Yace inason kamin sallama da maigidan ne

Bayan Ahmad yafito ne yaga mutum ustaz har da gemunshi

Yace assalmu alaikum

Hakeem ya amsa mishi cikin canjawar murya

Hakeem dai yakasa danne dariyar shi yacire fuskan

Ahmad wazaigani Hakeem ne

Cike da mamaki Ahmad yace amma ka shammaceni

A ina kasamu masks nasan dakyar akesamu a Nigeria

Hakeem yace daga India aka kawo min
Kaga kai ma danake tunanin zaka ganeni baka ganeniba

Bana tunanin shamsu da mutan gidansu zasu ganeni

Dan haka ni wuce daga yau zafara basu exam's din su

Hakeem ya mayar da fuskarshi yagyara da kyau yadda baza a ganeba
Yayi bakin titi yatari kekenapep zuwa anguwar su Husnah

Next page

Tofa  fans za afara wasa fa

Your comments is needed

Ina alfahari da masoya novel na🎗 AKWAI LOKACI🎗

📖📖📖📝📝
[05/05, 11:08 AM] UMMU  AFAN 🌹: 🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗
🎗🎗
🎗
BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

Story & written
By
The  special writer

UMMU AFAN

🖊️🖊️🖊️🖊️🖊️🖊️📚

🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹

🌹🌹 (F.C.T.W.A)🌹🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITER'S OF THE NATION🌹

🎗️I DEDICATE THIS PAGE TO YOU  sister surayya auwal ina matukar jin dadin comments din ki amma Dan Allah sister kikara yawan comments din ki ina alfahari da Ku da da comments din ku🎗️❤️❤️❤️❤️❤️

🎗️AKWAI LOKACI 🎗️

🎗️PAGE  86 to 90🎗️

HUSNAH  zaune tana gyaran farcenta  Umma tace auta nikam ya kukayi da Alhaji ne naga jiya yazo

Husnah ta bata fuska tace wallahi Umma guduwa nayi dakin anty kubra na buya Dan wallahi Umma nibana sonshi

Umma tayi salati tasanar da ubangiji
Tace aidaman zaran hijabin dakikayi kaman kinje
Bazuwa kikayi ba

To ma wai meyasa bakya sonshi meyamiki husnah karki zamo me saka alkairi da sharri mana

Tunda Allah baiyi aurenki da shi abdullahinba sai ki ba
Wannan dama kodan halinsa na kirki badan abin hanun shiba

Anty kubra tace wallahi Umma kullum sai namata wannan nasihar amma kamar anshuka dusa

Husnah tace wallahi ni kwatata bana jin zan iya son wani bayan ustaz ne

Kuma bana son na aureshi nakasa yimashi biyayya Umma na Dan Allah kufahimceni

Umma tace ai shi so ahankali yake shiga
Kyawawan halaiyar wannan yaro kadai zaisa kifara sonshi azuciyarki

Dan yana da duk wani nagarta atare dashi

Kafin Husnah ta yi magana  ya shamsu yayi sallama yashigo yazauna

Yana gaida umma kubra ta tashi tace sannu dazuwa tayi hanyar fridge tadauko mishi ruwa maisanyi

Takawo mishi

Ya dauka yasha  kafin yakalli umma yace mekuke ta tattaunawa ne ummana

Umma tayi murmushi tace wallahi wannan shasharce muke taba baki saikace wata uwarmu
Sai waina mu takeyi

Ya shamsu ya kalli Husnah yace wai meyake damun kine husnah

Ustaz yariga yatafi bazai dawoba
Wallahi husnah da ace zaidawo lokacin da akeshirin daurin auranki da Abdul Hakeem za afasa a daura dashi

Sai dai kash ba a mutuwa adawo

Sai dai ina miki albishir dacewan Allah yamiki sakayya da mafificin alkairi

Mun dade muna Neman hanyar da zamu sakawa wadan nan mutane

Sai gashi Allah yakawo tunda yasawa yallbai kaunar ki aransa

Maizai hana kitayamu maida alkairi da alkairi husnah

Abdul Hakeem yamana komai a rayuwa kuma duk abubawan da yayi mana na tabbatar Dan Allah yayisu

Kaman yadda  kema zamu bashi dan Allah badan abin hanun shiba

Husnah tace shikenan yayana
Namaka alkwarin bazan baka kunya ba
Na amince da shi
Amma wallahi danku Dan wallahi yaya bana sonshi

Ya shamsu yayi murmushi yace Abu mafi mahim manci dai shine ki amince

Husnah ta turo bakin shagwabar tace wato bakadamu dani bako yaya na

Ya shamsu yayi dariya yace caf waya fada miki yar kanwata
Yace ai nafi jidake

Dan idan kikayi aure ma fa tare zamu tafi

Husnah tayi murmushi tace ai wallahi yaya da dagaske kake da naji dadi sosai

Amma nasan kana fada be kawai
Amma nifa kullum sai nazo gidan nan

Umma tace kwarai kuwa daga ke har yayan naki zan ga me hankali   acikin Ku

Anty kubra tace gaskiya kam umma
Nima naga alama tana dariya

Ya shamsu yace dawa kikeyi yadauki pillow na gefensa ya wurga mata ta tashi
Tagudu yabita shima

Umma tayi murmushi Dan yadda Dan ta guda yake zaune lafiya da matarshi bata taba ganin wani abun ki agurin kubra

Husnah tace umma Dan Allah yau kimana danbun  tsaki da kanki
Kinga yau nice da girki

Umma tayi murmushi tace naki wayon sai girkin 'yata azo zanyi

aikuwa husnah tayi murmushi duk kugama  badaini ba wato sai ran girkin anty kubra zakiyi ko Shikenan  nasan mezanyi muku a gidan kuma dole kuci

Umma tayi dariya tace kinga kuwa kyayi aiki har dare kenan

Husnah tayi murmushi ta tashi tace Abba yakusan da wowa

Barin yi kitchen

Tana shiga kitchen din tafara tunanin abinda zata daura

Taduba store dinsu taga suna da doya

Tadauki guda biyu tafere shi tas ta wanke
Ta rarraba  shi kanana
Tazuba tunkuya takawo gishiri tasa dai dai misali

Kafin tadebo albasa attaruhu da tattasai dakuma tomatoes amma  kwaya hudu tasa tomatoes din bata bukatar tumatir dayawa

Nan ta wanke komai tas
Tafara  greating dinsu a greater ba a blender ba

Dan bata bukatar suyi laushi

Nan tasoya su da mangyada saidataga tayi  soyu sannan tadauko yankakkakun kayan namanta kanana dake cikin fridge tafashashshe
Tazuba tadauko gyararran kifinta Wanda tariga tacire kayar tas shima tazuba tacigaba da juyawa

Kafin tadauko maggi tazuba dai su curry da thyme da dai sauransu

Tahada tacigaba da soyawa haba ai nan da nan gida ya hau kamshin girkin husnah

Sai da ta tabbatar ya soyu kafin tarage gas din kadan

Tadebo kwai (eggs) guda  biyar
Tafasa  su a kwano daban tasaka magi guda daya takada

Kafin tadauko tana zubawa kadan kadan tana gaurawa har tagama tacigaba da juyawa

Gaskiya ko itada datayi miyar yakayatar da ita balantana Wanda saidai yagani kawai saici

Nan ta sauke tasama Abba a kulansa kafin tasa ma umma ma anata kulan

Ta ajiye a gefe

Tadauko nasu ya shamsu da anty kubra tasamusu  dama tumsafe tayi kunun ayarta Wanda yasha madara tasaka a fridge  yayi balin sanyi kuwa

Ta dauka nasu yaya shamsu tayi da shi part dinsu
Taje tana ta sallama taji shiru

Can saiga anty kubra tafito da gudu daga bedroom dinsu kanta ba Dan kwali ga gashinta duk an hargitsa

Ga rigarta zif din agaba yake kana ganin kasan akwai magana Dan anfara Jan zif din amma baikai kasaba

Kubra bata San ma da mutum a falonba ganin husnah kawai tayi tasake  baki tana kallonta

Kubra ganin kallon yayi tace ke malama lafiya kuwa

Husnah tayi murmushi tace a a bakomai gani nayi kinfi to kamar wacce  tayi dambe da zaki

Takarasa maganar tana dariya

Kubra tasan metake nufi
Itama tayi murmushi tace kema kwana nawane zakije fada da zakin

aikuwa husnah tabarai ta turo bakin tace zakifara ko anty kubra
Ta ajiye musu abincin tace gashi idan kungama  soyayyar kwaci

aikuwa tana fadar haka tagudu

Kubra tayi murmushi kawai kafin ta koma ciki

Husnah wanka tafada tana fitowa tayi sallar La  asar dinta  kafin taje gaban dressing mirro dinta tafara shafa mai abinta tanagama shafa maidin tadauko body spray tafesa kafin dauko wani

doguwar rigar English wear tasaka

Ta dauki gashinta daure da ribom baki kasancewar kayanta marun colour ne

Yana da bakin dankwali tadaura tayi daurin tauban
Tasaka jambaki shima marun colour  gaskiya ba karya duk Wanda ya kalli husnah sai yaso yasake kallo

Kayan dama dayane  daga cikin kayan da mummy hafsat takawo mata ne

Ta fito tasami Abba da umma sungama cin abincinsu

Abba yayi murmushi yace autar Abba gaskiya abincin yayi dadi wallahi
Waya koya miki ne autar ummanta

Umma tayi murmushi aini wani girkin ma fa kirkiran abinta takeyi kuma saikaga yayi dadi

Husnah tayi murmushi tace aini a school dinmu Abba food &nutrition naza ba akan  agriculture

Abba yace kai amma auta ta kinyi dabara

Umma ce takatse musu zancen nasu

Tace anya kuwa kinci abinci Dan nasan halinki sarai idan ba aganki ba saiki kai har goma na dare bakici komai ba

Abba yace wai har yanzu rashin   cin abincinta yanan
Umma tace sai abin da yakaru

Idan tagadama wataran dakanta zata dafa indomie

Ya shamsu ne yashigo falon yagaida iyayen nasa

Ganin fitowar ya shamsu yasa husnah zuwa gurin kubra

Wayar ya Shamsu yayi kara yana yaga yallabai kamar yadda ya saving wayar

Yadauka  bayan sungaisa prof yakecewa gani acikin gidanku

Ya shamsu yace haba yallabai  kaman wani bako kashigo mana

Hakeem yayi murmushi  yace ai gurin matata nazo katurota Dan Allah yakashe wayar yana dariya

Ya shamsu yafada wasu Abba Hakeem ne yazo

Abba yace ya zai tsaya a waje kuma  kaje kashiga da shi falonku  tunda yau  surkunta yakeji damu

Umma tayi murmushi tace ina ruwan Abdul Hakeem yaron kirki wallahi

Ya shamsu yaje suka shigo tare da Hakeem harkasa Prof yatsuguna yagaida su umma

Kafin ya shamsu yace mune daga ciki tana can  ma

Suna sallama dai dai lokacin husnah take gwadawa kubra rawan ittiki

aikuwa Hakeem idonsa  kyam akanta ya shamsu yace to dancer of the year

Anty kubra tayi dariya tace sannu dazuwa tana wa Hakeem cike da kulawa ya amsa tareda tambayarta gida

Nan ta tashi tayi falon su umma Husnah zata bita ya shamsu ke dawo nan baki iya gaisuwa bako

Cike da jinkuyar Prof tun ranar daya ganta half nacked bata kaunar su hada ido

Tadawo tazauna gefen  ya shamsu kai a kasa

Ya shamsu yace to yallabai saika fito

professor Hakeem  yace  Weldon ya shamsu

Ya shamsu yayi murmushi yafita

Hakeem yamaida kallonshi kan husnah wacce take ta wasada da  yatsunta daya sha Jan lalle

Batayi tsam Mani ba kawai taganshi agabanta

Zama yayi kasan shima yana fuskantarta

 kasa dagowa tayi saboda kunyarshi gashi itadai bawani sonshi take ba

Yace tunda nibaza a gaisheniba  nibarin gaisheda my wife

Dafatan kin wuni lafiya kasa amsawa tayi

Yace koki amsa gaisuwata konasa hanu na dago da fuskarki

aikuwa bashiri tadago tace cikin shagwabbiyar murya tace kayi  hakuri karka tabani ina wuni

Professor Hakeem yayi matukar kaduwa jin wanann murya  na husnah

Gawani masifaffan kyau tamishi

Kayan data sa ajikinta kaman Dan ita akayisu

Prof jiyayi kaman ya rungumeta a kirjinsa kozai zamu saukin sha'awar data taso mishi  lokaci daya

Husnah ganin hanun Prof kawai tayi yadanki hanunta

Cikin tashin hankali husnah tabi hanunshi da kallo

Yace baby kinsan damuwata wallahi kece ina matukar son kasacewa  dake amatsayin mata

amma haryanzu  bansan matsayina ba agurinki

Husnah tace zanfada maka amman saika sake  min hanu

Hakeem yayi murmushi yace shike nan inajinki

Husnah tafara magana tace na'amince zan aurekà  amma bana jin zaka sàmi soyayyata Dan nariga nagama soyayya a rayuwatà Dan ni kwata kwatà soyayya bai karbeniba

Kar sàinafara  sonka kaima narasàka

Takarasa maganar da kuka mecin rai

Hakeem jiyayi kukan har cikin ranshi  yadauko hand kacif a aljihunsa fari Sol yasha kamshi yamika mata

aikuwa ganin hankacif din nan saiyada ta girgiza

Ta karba dasauri tace Dan Allah yaya a ina kasamu wannan hand kacif din

Hakeem yace nawane kokina sone cikin sauri tadaga kai tace Dan Allah kabarmin wallahi irin Wanda ya muallim yake amfani dashine

Koranar da zamu rabuma  shine a hanunshi

Takarasa maganar hawaye mai tsanani  Hakeem yace  banason kukan nan kigoge fuska kimin magana Wanda yamutu ai yamutu

Husnah tayi  murmushin data kumatunta lotsawa sosai

Tace aikuwa sai dai kayi hakuri Dan har abada bazan daina tunaninshi ba saboda yatafi da zuciyata  gabadaya

Hakeem yaji matukar jintausayinta kaman yarungumeta ya rarrasheta

Husnah tacigaba da bashi labarin soyayyarta
Akan bashir da abinda yayi mata bayan tadauki zuciyarta tabashi lokaci kawai akejira ayi biki amma yafasa
Kuma yakoma suna soyayya da babbar kawarta

Sannan takarabashi labarin masoyin asali ya muallim

Hakeem yace nikuma na godewa Allah nakuma godewa saurayinki dayace yafasa

Dan da befasaba danayi asarar  zukekiyar yarinya kamarki

Kinga kuwa nidan gatan Allah
Akaro nabiyu yasake kama hanun Husnah  yace please baby kiyarda dani

Yakura mata ido tace naji  amince amma kasake min hanu Dan Allah bakyau fa

Hakeem yace nasani baby shiyasa nakeson abanike a matsayin mata  saboda banason nacigaba da sabawa Allah taba jikinki batareda aure ba
Because I can't control my self in front of baby

Husnah ta tabbatar dagaske yakeyi
Tayi murmushi  bara maka ruwa da lemu

Yaji dadi har ranshi data nuna kulawar ta agareshi

Murmushi kawai yayi tare da 'daga  mata gira ta tashi zata je sai kuma taga idonshi akanta

Ta juyo a shagwabe please yaya kajuya kadaina kallona inbasokake nafadiba

Maganar yaba Hakeem dariya yace jeki na rufe idon

Da gudu kuwa tafita yabi bayanta da kallo

Sai yatuna da ranar dayazo amatsayin ustaz

Zataje dauko masa kudi wai sai yarufe idonsa

Murmushi  kawai yayi shikadai
Tare da zaro wayarsa daga aljihunsa

Sallama tayi da tire a hanunta dauke da abinci  ta ajiye gabansa

Hakeem yaganta cikin wata jibgegen hijabi abin yaso  bashi dariya ma
Kar dai ace tagane  abinda yake kallo
Sai yayi murmushi kawai

Husnah tace ga abinci  yaya
Hakeem yace nakoshi

Husnah takalleshi tace saboda me

Hakeem yace saikin fada  dalilin ki nasaka min hijabi daga shiganki dauko min ruwa

Husnah tayi murmushi kawai
Tace  sanyi nakeji tafada tareda boye kanta  cikin hibinta

Hakeem yace  baby
husnah tadago batareda ta amsa ba

Yace cire hijabin nan kizo   ki serving dina

Husnah ta  marairai ce kaman zatayi kuka tace Dan Allah kayi hakuri yaya wallahi kunyarka nakeji

Prof ya tsareta  da maya tattun idonshi masu kwarjini

Yace OK kinfison  acire miki da kauna ko

Husnah tayi saurin girgiza kai

Yace OK do as I said  cikin sanyin jiki husnah tacire hijabin ta ajiye kan kujera tasauko kasa ta Samishi abinci

Prof ya gyara zama yafara cin abincin tareda tsareta da ido

Duk kallonshi yasa ta takura

Yace batayi tsanmani ba taka spoon din a hanyar bakinta
Tadago ido takalleshi ya daga mata gira

Tace azumi nake yi

Yau Wednesday dama ana azumin nafila

Husnah tace wallahi Nina koshi cikina ma kaman zafashe

Yace tunda yayi niyar bata tabude baki kawai yasamata

Bata da zabi haka tabude   Dan karamin bakinta yasaka mata

Yanayin yadda take cin abincin nata ma kawai abin kallone

Yatsaya kawai yana kallon ikon Allah

Yace bude bakin nagani
Tayi saurin cewa  na am da karfi

Tace inazuwa umma nakirana ta tashi tagudu abinta

Hakeem murmushi yayi kawai yagama cin abincinsa yafita yashamsu yace har zaka gudu

Hakeem yace a nayi bakine
Shine zanje nagansu

Ya shamsu yarakashi har gurin mota

Prof yakira megadi yabashi manyan lodoji yashiga dasu gida

Ya shamsu yace yallabai  Dan Allah karage kashe mata kudi haka sunyi yawa karka manta fa yarinyace Husnah har yanzu bata gama sanin kantaba

Prof yayi murmushi yace karkadamu itama ai hakkinace so konawa zankashe mata basuyi yawaba

Karka damu ya shamsu
Nagode da kulawarka
Yashige mota yayi gaba
Yabar ya shamsu da tunanin irin karamcin na PROFESSOR HAKEEM

****
Meenat sun wuce honey moon itada agonta bashir a inda zasu zaga kasashe sama da biyar

Shiyasa ma suke saran sai nan da 5 months zasu dawo Nigeria

Dadddyn Hakeem da shi dawasu amin tattun abokansa sukaje nemawa ABDUL HAKEEM ABUBAKAR SHUAIB

Auran  ASMAU SULAIMAN SHAMSU

Sun bada sadakin husnah da zinare Wanda akalla zai kai  million daya  da  rabi

Abba da ya shamsu suka suka kikarba

Daddyn Hakeem yanuna rashin jindadin shi

Sai su Abba suka karba tare da wa abin albarka

Nan daddyn Hakeem yace yana Neman alfarmar asaka auran nan da two Weeks

Next page

Your comments is needed Fan's

Ina alfahari daku masoyana ❤❤❤❤❤❤

📝📝📝📝📝📝📝📝📖📖📖📖📖📖📖📖
[05/05, 11:08 AM] UMMU  AFAN 🌹: 🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗
🎗🎗
🎗
BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

Story & written
By
The  special writer

UMMU AFAN

🖊🖊🖊🖊🖊🖊📚

🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹

🌹🌹 (F.C.T.W.A)🌹🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITER'S OF THE NATION🌹

🎗I DEDICATE THIS PAGE TO YOU  SIS NERFEESERT  A MUSA

INA MATUKAR JIN DADIN YADDA KIKE  COMMENTS DINKI DAFATAN ZAKI CI GABA DA SUBURBUDO COMMENTS
KEEP IT UP 😘😘😘🎗

🎗️AKWAI LOKACI🎗️

🎗️PAGE 91 to 95🎗️

PROF zaune cikin falonshi na gidansu yanawa da Ahmad madam Laila tazo tazauna kusa da shi fuska a kode

Tace ina da magana fa baban meenat

Hakeem yakalleta da nutsuwa yace ina sauraronki maman meenat

Laila tadago kanta ta kalleshi Dan taga kaman yau akwai abin arziki

Sai tadauko ko kwalliyar da tayi ne ta burgeshi

aikuwa sai tasake wani shagwabe fuska wai ita zatayi shagwaba

Abin yaso ba Prof dariya amma sai ya make

Tace daman inason wasu kudine Dan Allah

Hakeem yayi murmushi tare da kurban copee dinshi

Yace kaman nawa kike bukata uwargida rangida idan bake bagida

aikuwa kanta yasake fashewa

Tayi dariya tace kuma daga ni bawata nice amarya nice uwargida

Saboda dariya Hakeem har kwarewa yayi
Ya ajiye coffee din yana murmushi Wanda yake karawa kyakkyawar fuskarshi kyau

Yace Allah ko tace sosai

Yace nawa kike bukata kenan

Tace million biyu Hakeem ya kalleta yace sun isheki

Laila tankalleshi da mamaki

Sai dai kuma tabasar tace a idan zansamu kari ma aizankarba

Yace OK yatashi yaje dakinsa yadauko cheque yarubuta naira million biyar

Yabata aikuwa madam laila data karba taga abinda keciki

Kusan suman zaune tayi agun

Sosai takasa control din kanta

A take ta dau waya takira hajiya rukayya tafada mata kudin da hakeem yabata

Tsaban batan basira irin nasu daga uwa har 'yar suka hau murna

Ta ma mance agaban Prof take da mamaki Hakeem yake kallonta

Kuma godiya haka ta tashi zata fita

Hakeem yace baki jiba zokizauna

Baki tambayeni kudin menene ba

Laila tace aina sani tunda Nina tambayeka kuma ka nunka min fin abinda na tambayeka

Hakeem yace OK  wannan kudi kiyi amfani dasu ne naki

Dan nan da two weeks za a daura min aure

Kinga saiki sai abinda kike bukata ko

wani wawan ihu tafashe dashi
Tacire Dan kwali ta yar tace cikin tsananin tashin hankali tace wallahi Abdul baka isa ka  cimin mutunci ba kayi kadan

Kuma wallahi banga 'yar iskar data isa nayi kishi da ita

Wani wawan kallo Hakeem wa watsa mata

Yadawo PROFESSOR ABDUL HAKEEM  dinsa data sani yace karkisake kiran matata da 'yar iska if not zan baki mamaki

aikuwa Laila ta tafa hanu tace auwa harma tazama matar taka to wallahi Baku isaba

Kodayake kaima ba yinkanka bane duk abinda kakeyi saka akeyi

aikuwa tawuce fuuuuuuuuuuu tayi hanyar part din mummy hafsat

Hakeem daya kai cup din coffee baki ganin tafita ya ajiye coffee din

Yace tashin hankali badai matar nan gurin mummy na zata ba

aikuwa yatashi yazare belt din jikinsa yayi part din mummy hafsat

Mummy tana zaune tana waya da hajiyar Ahmad suna shirya yadda zasu tsara komai kafin bikin ganin Laila tashigo a fusace yasa mummy hafsat tace zankiraki hajiya

Laila ta tsaya agaban mummy hafsat tana  girgiza jiki

Mummy hafsat tace ke lafiyar ki kuwa zakizo kitsaya kina girgiza

Laila tace burin ki yacika sai dai ina son kisani wallahi  ba aisa akawo min wata 'yar iska gidaba

Nidaman nadade dasanin bakya kaunata kuma wallahi ba yadda kika iya dani

Mummy sake baki kawai tayi tana kallonta

Zata sake wata maganar taji belt ta kota ina ajikinta

Hakeem ne sosai yake sauke mata belt din nan ajiki

Mummy hafsat tashiga tsakani tace barta haka son
Yace mummy kibarni na babballata hartana da gost dazata sameki tana miki rashin kunya  Who is she by the way

To bari kiji bazan dauki raini ba ballanta na ki ma  mummy na wacce bani da kaman su aduniya

Kekinsan zamana dake ma ai darajarsu kike ci Dan ubanki

To kije nasakeki kuma yanzu zaki bar gidan nan nonsense ""

Ya kalli mummyn shi yace mummy Dan Allah kiyafemin wallahi nayi da nasanin hada zuria da hajiya rukayya

Bantaba tunanin zan ajiye matar da zata iya miki abinda Laila tamiki yanzu ba

Mummy tace kayya son kayi sauri da baka saketa ba
aiko wace mata da irin nata kishin idan mijinta yazo mata da zancen Karin aure

amma ni baka min komai ba hasali ma kanuna min kai d'ane Allah yamaka albarka

Tajuya ta kalli Laila dake kurma ihu tana kuka kaman ranta zai fita

Mummy tace kekuma tunda rayuwa da kika zaba wa kanki kenan aishikenan

Mummy ta wuce abinta Hakeem shima komawa sashinsa yayi nan da Laila ta dauko waya tafashe da kuka hajiya rukayya ta rude tace ke lafiya kike kuka waya mutu

Laila tafada mata abinda kefaruwa
aikuwa itama hajiya rukayyar kusan haukar tayi

Tace ba inda zakije ganin nan zuwa kadunan shidin  banza share hawayanki
Kekadaice a gidan mijinki

Kwantar da hankalinki ganin ta howa

Alhaji abubakar daddyn Hakeem yana hanyar dawowa daga office
Hajiya rukayya takira wayarshi tana kuka

Daddyn Hakeem yayi tafada mishi abinda abinda kefaruwa

Daddyn Hakeem yace Abu baiyi kyau ba ammanshima yanzu zaikoma gidan

Tace itama gatanan a hanyar zuwa yace Allah yakawoki lafiya

Ya kashe wayar yacigaba da tukinsa

Hajiya rukayya nazuwa sai da tabi tacan gidansu ta taho da uwarta itama wato hajiya suwaiba sukazo tare

Laila na zaune tana jiran hajiya rukayya suby kanwarta tuntuni tazo suke zaman jimami tare

Karasowar kowa da kowa aka hadu a falon daddyn Hakeem

Tunda daga kan hajiya suwaiba mummy hafsat hajiya rukayya Laila suby da kuma uban gayya ABDUL HAKEEM suna zaune gaba dayansu

Daddyn Hakeem yafara gaida hajiya suwaiba tunda itace uwa agaresu bakidaya

Kafin yagaida yayarsa hajiya rukayya

Daga nan kuma yabukaci yasan abinda kefaruwa

Hajiya rukayya tafara magana cike da zafin zuciya

Tace bantaba tunanin abinda wannan yaro zaimana bakenan ya suna zamansu lafiya da matarsa
Za azuga shi yayi aure wannan ma ai Neman tashin hankali ne

Kuma abin batsaya nan ba sai su hadu shida uwarshi sun mata duka

Sannan kuma tabashi umarnin ya saketa saboda bakin hali da akasha a nono

Ran Hakeem tafarfasa yake saboda bakaken maganganun da akejifar uwarsa dasu

Hajiya suwaiba tayi salati tasanar da ubangiji tace yanzu duk wannan abubuwan dake faruwa shine ba asanar daniba

Ta kalli Hakeem tace yanzu kai Ashe har yanzu baka daukemu da mutunciba
Kokana ganin Dan bani na haifi ubanka ba

To bari kaji idan bani da iko da kai inadashi da ubanka kuma ai ubanka yana da iko dakai ko

To wannan aure bazakayi shiba
Kuma maganar saki babushi dole yarinya ta zauna gidan ka

Daddyn Hakeem da tun da hajiya suwaiba tafara magana baice komaiba

Yayi gyaran murya yace  to hajiya naji duk hukuncin dakika yanke

Maganar Saki tabbas zai maida matarsa kobakomai saboda darajar 'yar da ke tsakaninsu

Maganar fasa aure kuma babushi

Ba fashi

Idan bazaki matanba alokacin dakika zo da bukatar hada su aure sai da Abba na Allah yajikan rai yafada cewan duk lokacin dayazo da bukatar kara aure bawanda ya isa ya hanashi

Sannan kuma koda SON bashida sha awar kara wallahi sai namishi da kaina
Saboda kugirbi abinda kuka shuka

Hajiya rukayya da Hajiya suwaiba suka kalli juna

Daddyn Hakeem yaciga dacewa
Narayu cikin maraici tunda natashi bansan dadin uwaba sai na uba ga kuma gallazar matar uba wato ke Hajiya suwaiba narayu a hanunki cikin kunci da gallazawa

Kuma.abinda bakisaniba shine kice silar mutuwar mahaifiyata amina bayan ta haifeni kukamata jifa da ciwo da haka har Allah yadau  abinsa

Kinsan a ina naji kamaku nayi kuna zancen keda Hajiya larai kishiyar ki

Nayi kuka kaman raina zaifita
Dana ji wannan magana daga bakinki

Kunsani maraicin dole kuma kuka kasa rikeni tsakaninku da Allah

Ba irin abinda bakuyiba ganin namutu amma Allah yace saina rayu a duniya

Alokacin da Allah yabani haihuwar ABDUL HAKEEM nadade ina mishi adduar Allah yarabashi da sharrinku

Dan nasan yanzu hankalinku zai komo kan 'Dana
Kullum cikin mishi addua a ruwa nake inabashi yasha
Wanda nasan ko mahaifiyarshi batasan niyya na ba

Saikuma kwatsam kukazo da gudirin aurawa Hakeem Laila alokacin shekarunsa basu wuce ashirinba  kuka dage sai anyi  na amince ne saboda wani dalili

Dan koda din ma abbana bai aminceba inzaku iya tunawa

Saboda haka babu Wanda ya isa ya hanshi aure

Idan kunga 'yarku bazata zauna da kishiya you are free to live with her

Hajiya rukayya da jike sharkaf da zufa
Zatayi magana daddyn Hakeem yadaga mata hanu ba abinda zakice yaya rukayya

Hajiya suwaiba ta sauka har kasa tace Dan Allah abubakar kayafe min wallahi duk sharrin shaidan ne hakan bazai kara faruwaba

Daddyn Hakeem yace haba Hajiya ai duk da abinda kika min bazaisa nadaina ganin ki a matsayin uwaba
Dan haka kitashi daga tsuguna min

Hajiya suwaiba tace nagode Allah yamaka albarka kaida zuriarka

Hajiya rukayya ma tana kuka taba wa daddyn Hakeem hakuri daddy dayake shiba meruko bane ya yafemata

Hakeem ya kalli mahaifin nasa yaga daddy na goge kwalla
Bakomai yasa daddy kukaba sai rashin imani irin nasu

Idan ya tuna sune sillar rabashida mahaifiyarshi da ko kamannin ta baisaniba saiyaji wani kunci
Daddy kasa jurewa yayi yatashi yashige bedroom dinsa

Abdul Hakeem yabi bayansa mummy hafsat ma tashi tayi tabisu

Hajiya rukayya tabuga tsaki aikin banza wallahi wannan kukan danayi bazai tagi banzaba

Hajiya suwaiba tace towayafada miki dama tubar gaskiyace

ai kawai ganinayi asirinmu yatonu shiyasa na bullo musu tanan

Laila cikin kuka tace yanzu dai kuna gani Hakeem zaikawo wata dasunan mata

Suby kanwar Laila ta ce ai wallahi duk wacce tayi gigin shigowa gidan ki anty Laila wallahi taja wakanta balain duniya Dan wallahi sai mun nakasa rayuwarta

Hajiya rukayya tace ai zama bai kamamuba

Ke Hajiya bari musa driver yamaidake gida

Gobe zamuyi nijar saboda ke Laila yau kije kibashi hakuri

Kinuna kinyi ladamar abinda kika aikata har dai yasamu yabarki gobe mutafi

Laila tace shikenan hajiyarmu Allah yabar mana.ke kina kokari ganin farin cikinmu

Nan sukatashi kowa yakama gabansa

Laila ta koma part dinsu tazauna tana tunanin abubuwan da suka faru

Wanda sana diyarshi allura ta tono garma

****

Laila sundawo daga nijar yanzu tana zaune ne zaman jiran amarya Dan tafara aiwatar da niyarta

Hakeem kuwa sake tsarin gidannasu yabayar akeyi badare ba rana
aiki ake zabgawa

Zama yayi yaga gaskiya a yanzu yakamata dadinsa yadaina fita office
Shiyakamata yayi komai su su huta

Kuma bashida da sha'awar raba gida da mahaifansa

Yayi shawarar dawowa A B U Zaria sunfi kusa da nan

Zaisamu daman da dazaije ya kula da harkokin kasuwancin daddynsa

Ahmad ma yace shima kawai kadunan zaidawo yacigaba da rike company daddynsa
Shiya sama yasa ma aikata gyaran gidanshi na Kaduna

Sunyi parking gabadaya zuwa Kaduna Aisha matar Ahmad ta tare a sabon gidanta dake Kaduna

Hakeem ankam mala komai ainda aka fitar wa da kowa dinshi

Part din Hakeem yana tsakiyarsu

A babban folon PROF zai iya shiga part din kowacce falon nashi guda biyu akwai a sama Wanda idan ka haura sama falon PROF shima daga gefe kuma wasu maka makan bedroom dinshi guda biyune

Kai gaskiya dai naira tayi kuka a gidan Prof

Gabakidayansu yasakewa was furniture's har daiyayensa

Komai yazuba wa Husnah Wanda uba yake wa 'yarsa Prof ya dau nauyin komai

Bakin ciki kamar zai kashe Laila amma ba yadda ta iya dole tanuna bakomai saboda tasamu ta cimma burin ta akan amaryarsa

Mummy hafsat gobe zasu daga zuwa Dubai itada mummyn Ahmad

Hado kayan lefe

*******

Biki ya rage saura kwana hudu Hakeem ne cikin motarshi yana zaune agefen mai zaman banza

Yayinda Ahmad kuma yake driving zasu kano gidan su husnah

Ahmad yace kai prof gaskiya kacanja wallahi gaskiya Allah yawa husnah albarka data saita mana kai

Dafa magana wahala yakebaka
amman yanzu sai a zauna dakai asha hira musam man ma na husnah

Hakeem yayi murmushi yace kaikuma dadina dakai sa ido wallahi

Ahmad yace aidole ne asamaka ido yadda yarinya karama tacanja ka

Hakeem dai murmushi yayi yace bazaka kanebane abokina bakasan yadda nakejin babyn a raina bane ko

Ana kiran la asar suna shiga gidansu husnah ya shamsu yataresuda murna yace kaga manyan kannena

Ahmad yayi murmushi yace fada dakyau ya shamsu girma fa Allah yabaka

Hakeem yace kana mamakine yaya shamsu

Ya shamsu yayi dariya yace waneni da mamaki Dan na zama yayan manyan maza

Daga shiya shamsun dayayi maganar harsu Ahmad da Hakeem sai da sukadara

Ya shamsu yace bissimilla mushiga daga ciki

Hakeem yace mudai fara gabatar da sallah tukun

Nan suka wuce masallacin unguwar

Husnah zaune itada anty kubra

Anty kubra tace Dan Allah husnah kisanar da kawayenki
Maganar bikinki

Husnah ta yatsina fuska tace nifa bazanyi taroba ma

Nibana mason hayaniya wallahi

Kuma da kika damu bagakiba dake da anty Aisha kusai kuzama kawayena

Kubra tarike baki tace lalle husnah wuyanki ya isa yanka
Nice ma zan zama kawarki ko

Husnah tace to Baku kuka dage saina aureshi ba

Anty kubra tayi murmushi tace aini dadina da gobe saurin zuwa
Kaman yaune zakizo kinacemin anty kubra
Wallahi inason mijina

Husnah tayi murmushi tace humm anty kenan nifa nafada miki auren biyayya kawai zanyi amma ba wai danso ba

ai nagama soyayya

Anty kubra tace shikenan  tunda haka  kikace akwai ranar maida martani

Anty jumai wacce aka dauko tunda Sudan saboda gyaran amarya tunda akasa bikin washagari ummu tayi Sudan dama can ita mutuniyar cance

Anty jumai tadubi husnah tace tashi muje kishiga wankar tunda
Hadin yayi awa biyu da shafawa

Husnah tace anty wai Dan Allah yaushe za adaina min wannan shafe shafen nan da shaye shayen nan

Anty jumai tayi dariya tace sai randa kikabar gidan

Kuma kuji dakyau dawasu zaki taki tafi

aikuwa Husnah ta turo baki ta tashi taje ta shiga wanka

Tana kansaka kaya taji muryar su yayanta da PROF suna gaisawa da umma a falo

Tayi niyar kwalliya tafasa  Dan mutumin nan yabata tsoro ranar

Riga da skirt tasaka nawani tsadaddan net tayi kyau bakadanba

Powda kawai tashafa sai man baki

Tana kan maida kayanta cikin durowa anty kubra tashigo tace amarya ango nakira yana falonmu  husnah ta turo baki tace anty kinfara ko

Zanrama wallahi nasan abinda zanmiki kema

Kubra tace ya hakuri 'yar kanwata nadaina

Dan nasan ki sarai wallahi

Husnah tayi murmushi tace a to dole abani hakuri dai

Tadauki mayafin kayan tayafa

Kubra tace kai husnah kedai komai baki baiwane

Wallahi kinwani canja ne fa gabadaya
Kinciko tako ta ina

Jin abinda anty kubra tace yasa husnah tunani tabbas ko itakanta tasan komai nata yacanja

Kuma acikin sati biyun nan da akafara mata gyaran jiki ne

To gaskiya bazata  tasa gyaleba

Ta ajiye gyalen tadauki jibgegen jijabinta

Anty kubra tace haba Dan Allah mijinkine fa yazo zakije masa da wannan katon hijabin

ai gwamma dai kidau ki mayafin dakikayi niyar sawa

Kinga zaisake shiga hanu kafin nan da kwana hudun nan

Husnah tace aikuwa kinja ma wallahi rayuwar hijabin zanyi agidansa

Ta wuce anty kubra tayi falon

Tashiga da sallama ya amsa mata tamkar wani balarabe

Kamshin sa yacika falon

Husnah tanemi kasa tazauna

PROF yakureta da kallo wani kyau yaga tamishi
Kaman yau yafara ganinta

Husnah tagaisheshi bai amsa ba jin bai amsa ba yasa tadago suka hada ido yakafeta da idonshi

Kasan yasauko yazauna yana fuskantarta yace haka ake tarbar miji baby

Tayi shiru batace komaiba yace babay magana nake fa

Husnah cikin shagwabarta Wanda ita bada niyya tayi shiba tace menama kuma

Yace nafarko nace kidaina samin hijabi idan zakizo gurina bakida mayafaine

Tace tokai meyasa bakason insa hijabin

Hakeem very good question
Nafarko inason hijabi amma a muhallin daya dace asaka kaman kiganni da wani ko abokaina da kuma sauransu

amma banda dagani saike kisaka
Bakisan nazo naganki Dan nasamu nutsuwabane ?

Husnah tayi shiru tana wasada da zobenta

Murmushi Prof yayi Yakama hanunta tana kokarin janye hanunta prof yacire  zoben hanunta Kafin yasaketa

aikuwa Husnah ta kalleshi  a tsorace tace Dan Allah kayi hakuri kabani zobenan

Yace meyasa zan baki tace nima bani akayi

Yace wakenan tayi rau da ido kaman zatayi kuka

Tace masoyina ya muallim

Yace zan baki amman saikinbi maganana kicire wannan jijabin
Dan ba anan yakamata kisaba

Husnah tace Dan Allah yaya kayi hakuri kabarni da hijabina nariga nasaba

Hakeem yace OK yasaka zoben a aljihunsa

Yace nawa kike bukata game da events din ki

Husnah takalleshi tace nima bana bukatar komai

Ya kalleta da mamaki yace saboda me tace bakomai wallahi ni duk wani Abu dayashafi bidia bana kaunarsa

Dan Allah yaya daman inason na roki alfarmar  events din dakukasa akatin nan wallahi banaso Dan Allah kabarshi kawai

Hakeem yace duk abindakikace haka za ayi amma bashi ne
Duk randa kika haifamin baby  zan baki mamaki duk abinda ba ayi a bikin nan ba saina yishi

Husnah tayi shiru can tace tokabani zoben yashare zancen

Yafito da kudi dubu Dari shida ya aje mata yace gasu nasan zaki bukaci kudi banason kitambayi ya shamsu ko Abba

Duk abinda kike bukata let me know OK

Ya cigaba da kallonta kawai kaman yasami TV

Husnah tace maganar zoben
Yace sakinyi abinda nace miki
Husnah tace nayarda amma saidai nakoma na dauko mayafina

Baice komaiba sai binta dayayi da kallo

Shigowar husnah Hakeem kusan suman zaune yayi Dan baitaba tunanin abinda idonshi zaiganiba kenan

Da sauri yace baby go and wear your hijab please

Husnah takoma da sauri
Tana shiga dakinta fashe da dariya
Dan bakaramin dariya yabata ba

Hakeem dafe kai yayi take hankalinsa ya tashi

Nan yafara tambayar kansa
Meyasa sai akan yarinyar  nan yake jin feelings haka

Maiyasa komai nata is so special to me

Da kyar yaja kafarsa yafita zuwa gurinsu Ahmad da ya shamsu

Ahmad yace muwuce ko  PROF yace

Hakeem yace muje muma su umma sallama

*******

Laila takira meenat tafada mata duk abinda kefaruwa

aikuwa meenat kaman tayi tsuntsuwa tazo Nigeria

Tace kiyi abinki mummy babu matar data isa kiyi kishi da ita wallahi

Idan mukazo  koni ko 'yar iskar da tayi kasadar auran daddyna

Suna gama waya da Mummynta Laila

Tadubi Bashir tace   kaji kuwa mekefaruwa agidanmu

Bash yace saikin fada

Takwashe komai tafada mishi

Tsaki bash yayi yatashi

Yabar gun

Next page

Your comments is needed fan's

Love u all

📚📚📚📚📚📚📝📝📝📝📖📖📝📖
[05/05, 8:53 PM] UMMU  AFAN 🌹: 🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗
🎗🎗
🎗

BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

Story & written
By
The special writer

UMMU AFAN

🖊🖊🖊🖊🖊🖊📚

🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹

🌹🌹 (F.C.T.W.A)🌹🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITER'S OF THE NATION🌹

🎗I DEDICATE THIS PAGE TO YOU Hauwa'u idris ( maman daddy )
Allah yabar zumunci inajin dadin comment din ki Allah yabar kauna keep it up😘😘😘😘😘🎗

🎗AKWAI lokaci🎗

🎗PAGE 101to105🎗

PROF  yashigo direct dakin amaryar ya wuce sai yaji kofa gam

Kuma gashi bashida spire key
Duk guda hudun suna hade da juna

Ya koma dakinsa yayi wanka
Ya koma kan bed dinsa yadauki waya
Yasoma dialing din number husnah   yayita ringing

Husnah bata daga wayar ba

Prof yayi mirmushi Wanda shikadai yasan abinda yasashi murmushi

Ya rufe ido Dan bacci amma bacci yace baisan zancenba

Yadauki wayarshi kawai yakira Ahmad

Saida yakira Ahmad sau biyu kafin ya dauka

Ahmad yace kai ango yadai kira da wannan lokacin

Hakeem yace kai dai bari wallahi man
Wallahi yarinyar nan ta kulle min kofa

aikafin yakai karshe Ahmed yafashe da dariya sosai yayi dariyarshi

Kafin yace amma wallahi husnah ta burgeni
Sosai

Hakeem yace Dan iska dariya zaka min ko

Ahmad yace aikaine abokina duk kabi ka tsorata masu yarinya aidole ta kulle kofarta
Dan batasan mezaifaruba idan akabarku Ku biyu

Hakeem yayi murmushi yace duk tagama buyanta badai ta shigo hanu ba

Zanbata mamaki zata shigo hanu ai

Ahmad yace wallahi dai kabi yarinyar mutane a hankali
Bafa babbar mace bace

Dan nasan kasaba da manyan mata

Yayi dariya yakashe wayar shi

Hakeem cikin murmushi yabi wayar da kallo

Yace zanrama ne

Kafin yakoma amma bacci fa yaki Sam
Daya rufe ido zaiga husnah alokacin da yake kissing dinta

Sai yayi murmushi ya rungume pillow kawai bacci yayi awun gaba dashi

Laila duk abinda kefaruwa tana lebe tana gani aikuwa ganin Hakeem ya burda kofa yaji akulle duk ta gani

Har wayan dasukayi da Ahmad taji aikuwa cikin farinciki ta koma part dinta ta sanar da su hajiyarta da kanwarta suby

Dan basu komaba ita suby auran nata ya mutu shiyasa zata zauna gurin Laila

aikuwa cikin farinciki hajiya rukayya tace aikin banza Ashe ma duk abinda suke yarinya bata so

Suby tace a a karku manta dama boka yace zai sa gaba a tsakaninsu

Watakila aikin ne boka ne yafara aikitakanta

Inbahakaba wazaiki yaya Hakeem a matsayin miji

Hajiyarsu tace tabbas maganarki hakatake

Kunga ganiba gwamma da muka sake mishi kudi gashi anfara aganin cigaba

Laila dai da farin ciki ta kwanta abinta zuciyarta fati kal

Karfe hudu dai dai na asuba Husnah tafarka cikin nannauyar baccin da ya dauketa

Tashi tayi tashiga bathroom alwala tayi kafin tayi nafilfilunta kamar yarda tasaba ana kiran sallar

asuba tayi sallarta tayi adduointa da karatun alkur'ani

Kafin tacire kayan jikinta Dan jiya bata samu daman cire kayan ba saboda gajiya

Tashiga wanka kafin tafito
Spray kawai da shuwa tashafa sleeping dress tasaka duguwar riga abinta tafada gado abinta

Sosai taji dadin baccinta Hakeem bayan yadawo daga sallar asuba yasake tana dakin husnah shiru bata budeba

Direct dakinshi ya wuce dakinsa
Shima baccin yakoma

Karfe bakwai da rabi dai dai mai aikin mummy ta buga kofa

Suby kanwar Laila ita tabude kofar

Taga me aikin mummyn Hakeem ce

Tace sannu suby ta yatsina baki yadai ina zaki da basket din abinci haka

Tace hajiya ce ta aikeni nakawo ma amarya abin karyawa

Suby ta kebe baki tace to aikuma basu tashiba amma kawo saina na mika mata

Tabata abincin

Suby ta karba tashige dashi part dinsu gurin su Laila da hajiya rukayya

Laila cikin murna tace yauwa suby dauko maganin a side drawer kikawo

Aikuwa haka suka barbade komai da maganin nan

Farfesuf na kayan ciki sai kunun gyada da kosai

Kai kuma farfesun ganda Wanda yasha kayan hadi sosai

Haka suka bikomai suka badeshi tas

Hajiyq rukayya tace maza ke suby tashi kikaimata

Laila tace abarta ta kai Dan tanason ganin amaryar

Hajiya rukayya tace a a idan kika kai dakanki za azargi wani Abu

Zakiganta ai mudai burinmu kawai tabar gidan

Suby tace wallahi nimafa basanin amaryar nayi bama dan haushi

Husnah cikin bacci taji ana buga mata kofa ta tashi  tayi hanyar falonta

Tayi kofa tabude sukayi ido hudu da suby
Suby sai tadauka kaman gezo idonta suke mata wannan irin zukekiyar yarinyar kuma daga ina

Husnah ta ce sannu suby  tace ina antyntaki

Husnah ta yatsina fuska  tace antyna kuma

Suby tace ina nufin amaya
Husnah tayi murmushi tace OK ai tashiga wanka

Tana ganin suby tasauke ajiyar zuciya

Husnah ta kibata hanya kuma
Suby tace ga shi inji hajiyar yaya Hakeem akawo mata

Husnah tace OK angode barin kaimata
Suby ta mika mata basket din husnah tarufe kofarta

Murmushi husnah tayi ta ajiye basket din ta ajiye kan dining kafin ta koma kan bed  koma bacci

Sai karfe goma dai dai ta tashi
Ta gyara bedroom dinta da falonta ta badeshi da kamshi

Ko ina yadau kamshi  kafin tashiga bathroom tayi wanka tafito ta shirya cikin wani tsadaddar super Holland  dark blue sai adon pink ajikinsa

Yadda dinkin yazauna ajikinta shizaifi Baku sha'awa sosai das yamata  dinkin ma kawai a in kallone
Matsalarta daya  bata son dankwali ta tace gashinta takama da ribbon pink

Kafin ta murza daurin Dan kwalinta abin wuyanta ma pink ne

Gaskiya husnah tayi kyau matuka

Tadauki ta kalminta plate shoe tasaka

Har ta zauna zatafara break fast saikuma taga rashin dacewar hakan

Bata je tagaida mummy ba

Gyalenta tadauka maishegen kyau tayafa

Pink colour

Tafita tayi hanyar kofarta  tasaka key ta kulle

Bayan ta fita

Dama dole saitabi ta main falonsu gabadaya  tana fitowa kuwa taga mutan gidan gaba dayansu a falo

To itabasaninsu tayi ba
Ganin harda manya yasa husnah ta durkusa tana gaida su hajiya rukayya da kuma Laila

Laila ta watsa mata harara
Wai ita hakimar bata fitowa ne saike

Hajiya rukayya tace inazata fito ansamu duniya
An auri mekudi an asirceshi

Suby ta kalli husnah tace 'yar buzuwa kotafiya za ayi ne

Husnah ta kalleta tace inje ina ai munsamu gida nida antyna
Dan nadawo kenan gwamma muma muzauna muci arzikin Dan da alama bamu kadai bane 'yan cin arzikin

Husnah tana gama yada musu magana tayi waje abinta

Har suby zata bita hajiya rukayya tace a a kyaleta kar ajimu tun yanzu mana

Laila race lalle ma Dan talaka be iya samun wuriba
Wannan zakewa haka harda dauko 'yar riko
To wallahi wannan yarinyar kamar aljana bazata tazauna  min agida wallahi

Kalli yadda take tafiya kamar wata 'yar sarki

Hajiya rukayya tace  aibakisan halin talakabakenan idan yasami guri

Kuma ke Laila da kike cewa bazata zauna ba yayar tata ma ba zaman zatayi balle ita 'yar cin arziki

Nan dai suka muna funcinsu

Husnah tayi sallma a falon mumy shiru  ba kowa

Ta nemi guri tazauna a tafkeken falon su mummy

Mummy ta sauko daga sama bata lura ba harzata shige kitchen
Husnah tayi saurin sauka  kasa tace mummy ina kwana

Mummy hafsat tajuyo tayi tazali da surukar tata

Tace a a husnah ai ban lura bama meyasa kika zauna nan baki haura saman ba saikace bakuwa

Husnah tace bakomai mummy nan ma yayi

Mummy hafsat tace a a nan gidanku ne ko ina zakishiga
Kina da damar hakan kinjiko

Ya bakunta husnah tayi murmushi kawai batace komai ba

Mummy tace kinci abinci ko husnah tace yanzu zanje nayi

Kafin mummy tayi magana Abdul Hakeem yayi sallama yashigo wata tsadaddiyar shadda   milk colour sai wata hadaddiyar hula da ya murza akansa Wanda yasake fito da kyakkawar fuskarshi mai kewaye da kwantacen saje dayakarawa fuskar tashi kyau

Gaskiya PROF Fa kyakkawar mutumne bankarya

Yashigo idonsa yakai kan Husnah dake zaune kan kafet

Wani farinciki yaji sosai
Ya kalli mummy

Yace mummy na antashi lafiya

Mummy tace lafiya kalau son maza kuwuce dining kawai kuyi break idan kungama kukirani zanje nayi salar walha

Hakeem yace angama dalibata
Mummynsa tayi murmushi tace a a tun yaushe daliba ta canja malami ai

Hakeem yace amma tunda yanzu nadawo gida
Sai kisake sayan form agurina Husna da mummy sukayi murmushi

Mummy tace kaga idan nabiye maka sai lokaci ya wuce banyi sallar ba

Ta kalli husnah tace 'yata tashi kije dining kinji  kikarya abinki kinji

Ina zuwa yanzu

Mummy tayi sama tabarsu anan

Hakeem yakure wa husnah ido yace wana kama
Husnah ta saukar dakai kasa
Hakeem shima zamayayi  shima tabayanta yakamota yasakalo Kansa tagefen  wuyarta hanunshi  yakai cikin rigarta ta yashafo cikinta

Yace bakice abinciba baby jicikinki fa kaman zai hade da baya

Itadai husnah wani  iri takeji tabatan dayakeyi

Yace tashi muje nabaki abinci banason musu

Cikin shagwaba husnah tace ni anan zanci ba a dining ba

Prof yace angama baby dakanshi yatashi  yakawo musu komai plate daya yazuba musu

Yace oya bude bakin bayan yadauko kofin kunun gyada tace dakaina zan sha kabari kawai

Yace bason musu fa
Badan tasoba tabude baki yabata
Nan yabata farfesun ma   kosai da duk wani abin dake gun saida yashiga cikin husnah tace mishi ta koshi yaki

Yace daman ya shamsu yamishi bayanin bata cin abinci

Cikin shagwaba husnah tace wallahi inaci kuma nakoshi sai da yaga tana shirin  dawo Dana cikin nata yabarta haka kafin shima yafara cin abincin

Bayan yagama ne yasa hanu zai dauke tiren abincin husnah targashi yace yadai yakureta da ido
Tace kabarshi kawai zankai

Bai hanataba husnah tadauka tayi hanyar datake tunanin nan ne kitchen din

Tana zuwa ta ajiye a sink din wanke wanke  ta wanke tas duk wani abin da za a wanke saida ta wanke

Shikuma prof be biyo sa wuba saboda yana waya ne

Mummy tasauko daga sama  tagashi shikadai  ne a falon
Tace a a asmaun

Hakeem yayi sallama dawani abokinshi yace tashiga kitchen
Kai kwanuka

Mummy taleka kitchen dintaga ko ina  tsaf an goge

Mummy tace kai haba husnah da kanki Aida kinbarima yanzu mai wankewar zatazo yau tayi ranar dawowa ma

Husnah tace bakomai mummy

Mummy tace maza jeki huta kafin nafito
Husnah tayi murmushi tace
a a mummy meza adaura  Dan naga kaman abinci kikeson daurawa

Mummy tace a haba dai daga zuwa harkifara shiga kitchen a a jeki huta
Idan kunyi sati saikifara dafa abincinki

Husnah tace mummy kigafarceni amma banzan taba zama inga kina shiga kitchen

Yakamata kema kihuta Dan Allah

Tunda na taso agidan mu Nina ke abinci  umma ta na hutar da ita  saboda haka Dan Allah mummy kibari na ringa miki abinci kihuta kema kisan kinada yarinya a yanzu

Cike da mamakin kalaman husnah mummy tace lalle husnah kin haifu Allah ya wa iyayenki albarka dasuka miki tarbiya maikyau

Nagode da kika daukeni matsayin uwa
Allah yabaku zaman lafiya keda mijinki yazaunar daku lafiya kinjiko

Husnah kai akasa tayi shiru

Mummy tace na'amince zaki rinkawa mummy abinci amma fa mummy ma tayi alkawarin satayi sati kina cin abincin mummy kinjiko

Saboda haka kibar mummy tacika  alkawarin ta

Husnah tayi murmushi kawai kafin tayi magana

Hakeem yayi gyaran murya mummy da husnah suka kalleshi

Mummy tace wato labe kake mana ko

Hakeem yayi murmushi yakaraso cikin kitchen din

Yakama hanun mummy yace haba mummy please kibar yarinki tasamu ladarki

Allah ne ya amsa adduarki yakawo mana husnah cikin rayuwar mu

Kinji mummyna

Mummy hafsat tayi murmushi tace shikenan tunda kunmin yawa Allah yayi albarka

amma bayanzu za adaura abinciba sai yamma idan anyi la'asar
Yanzu muje kawai muyi hirar mu

Mummy taja hanun husnah wacce tunda Hakeem yashigo takasa magana

Ranar dai a sashin mummy husnah ta wuni sai da ka kira isha tabar dakin mummy ganin Hakeem da daddy sunfita sallah

Mummy tace yau husnah Allah yatashemu ki huta gajiya ko

Ita mummy a tunaninta husnah zata je tashirya ne kafin mijinta yasameta

Husnah kuwa tashiga falon taga Laila da suby a zaune

Ta wuce abinta batareda ta kalli kowa ba

aikuwa suby tace ke zonan

Kojuyowa husnah batayi bare ma tasan da ita sukeyi

Ke 'yar talakwa bakiji menace bane husnah tayi banza dasu kafin suby ta karaso husnah tashige ta banko kofarta tasaka key

Direct wanka tafara kafin tayi sallah tayi karatun ta data saba

Suby tace anty anya kuwa ba wannan aljanar  yarinyar bane kishiyarki kuwa

aikuwa jitayi Laila ta zabga mata mari

Suby tace mena miki anty Laila

Cikin tashin hankali Laila  tace damme zaki min wannan mugun fatan

Taya za ayi yaje ya auro 'yar cikinsa

Bama hakaba idan yakasance wannan yarinyar ce ai yayi abinkuya
Nikuma nashiga uku taya zafara kishi da wannan yarinyar

Suby tace aiko dai koki kokiso itace
Dan agabanki tasa mukulli ta bude sashinta kuma dazu Dana kai mata abincin ma ita nagani kawai raina mana hankali take

Laila ta daura hanu akai tace nashiga uku ni Laila wannan ai inaganin ko meenat ma ai tagir meta
Lalle Hakeem yacuceni

Yanzu sakayya da zaimin kenan ya auro 'yar cikina inyi kishi da aita ina Sam bazaiyuba wallahi

Suby tace wallahi idan kika bari aljanar yarinyar tazauna agidan nan

Zikidawo jaka wallahi Dan abinda kike samu bazaki samu ba

Yarinya kaman ita tayi kanta Dan kyau tahada komai da d'anamiji yake bukata

Laila tace ya isa haka suby zakisa zuciyata tafashe kibarni naji da Abu daya Dan Allah

Hakeem yashigo falon da sallama Laila ta taso sannu da zuwa baban meenat

Hakeem yace yauwa yashige bedroom dinshi  Dan karya taba kofar husnah yaji akulle agabasu su fahimci wani Abu

Laila tabishi har yafito Daga wanka yana  yashirya ya kwanta

Laila taga bashida niyar kulata yasata ce baban meenat har yanzu fa bansan kanwartawaba

Sai kanwarta muke ta gani tana shige da fice

Hakeem yayi murmushi Dan ta tabo inda yake mishi kaikayi

Yace kanwa kuma ai bata da kanwa itadai wacce kikagani din itace amaryata

aikuwa Laila ta tashi tace amma wallahi kaji kunya Hakeem yanzu da girman  ka da darajarka zaka auro 'yar cikinka wannan ma ai zubda mutuncin Kaine da zubar wa  'yarka  da mutunci

Prof baki kawai yasake kallon ta
Yayi murmushi yace kinyi  sake maman meenat da kika auri mijin asmau saboda yanzu nasan nima namijine  kuma na auri dai dai Dani kije aduba miki nidake bamu taba dacewa ba kuma bazamu daceba

Meenat da Allah yabani na karba kuma inason 'yata
Idan tazo ruwantane taso matata ruwantane takita

amma zanfada miki wannan Kalmar mummy da daddyne kawai bazan iya rabuwa dasu ba saboda husnah

Amma bayansu zan sabama kowa akan matata so get out of my room

Cikin tashin hankali Laila tafito Daga bedroom din Hakeem

Kuka sosai taci suby nabata hankuri

****

Bayan sati uku Hakeem ya Dade da komawa aikinsa gashi aikin yamishi yawa ga kullum tunanin husnah ne da sha'warta acikin ranshi

Ba inda yake samun ganinta sai a part din umma Dan Anna take wuninta

Tana fita sallar isha zata gudu

Hakeem zaune kan kujerar office dinsa Ahmad kuma yana cike wani file's

Ahmad yace yauwa kagani ko yana nuna wa Hakeem abinda yacike
amma hankalinsa baya taredashi

Ahmad yace wai meke faruwane Prof
Hakeem yayi murmushi wallahi baby ce take bani ciwonkai

Taki bari na rabeta Sam wallahi
Bana ganinta idan ba a gurin mummy ba

Ahmad yace zanbaka shawara idankabi yau din nan kadaina damuwa

Hakeem yabada hankalinsa sosai

Ahmad yace bakace agurin mummy take wuniba prof yace a

Ahmad yace sallar ishar dazakaje yau kabari kawai kamuku jam'i

Kana shiga kacewa mummya da daddy da ciwon kai kadawo

Idan kaga zata tashi saikace jirani mutafi tare agaban mummy nasan bazatayi musu ba

Hakeem yace kuma wallahi sai dai kuma yau laila ce da kwana

Ahmad yace saikayi hakuri yau da gobe ai duk dayane yayi dariya

Hakeem yace a a baduk dayabane wallahi kai bakasan halin danake cikibane shiyasa

Ahmad yace kai haba mai mata biyu fa amma kana fadin haka ai saika kabani tsoro nakasa kara tabiyu

Hakeem ya harareshi

Husnah falonta suna waya da ummanta da ya shamsu da anty kubra

Bayan sunagama wayarne ta dauko mayafinta zata koma banngaren mummy

Sai taji Laila tana waya amma bata San dawa take ba

Laila tace dadin abinma fa yarinyar baso shi take kullum a dakinta take kwana
amma wannan aikin bokane yace bazai taba bari harya kusanceta ba

Yanzu fa kusan sati uku kenan amma suna wasan buya bata ma bari  yaganta

Shikuma na mamajo kina gani shi kisan yana cikin damuwa

Can ta matse mishi kinga  haka malam zaicire mishi sonta aranshi kwatata

Dan nima yace karnabari ya kusanceni har sai yarinyar tabar gidan

Kinga kuwa ai yana cikin matsala dannima bana zuwa bedroom dinsa harsai ranar da wannan aljanar yarinyar tabar gidan

Nan dai sukayi sallama da kawartata

Ta kalli suby tace insha Allah saura kiris yarinyar nan tabar gidan nan

Daga nan kuma sai mufara shirin yadda zamuyi mukasheshi idanba haka ba wallahi wata zaisake hangowa

Suby tace wallahi da dai yafikam
Dan wallahi nima inason naga munfara fantamawa fa anty

Laila tace kidai yishirunki kawai saura kiris

Husnah toshe baki tayi sai kuma wani jiri data ji yana dibanta dakyar tasamu takai kanta kan kujerarta

Tace innalillahi qainnairraihirraju'un  nashiga uku meya musu  suke son kasheshi

Gaskiya bazantabari kuyi nasara da yardar Allah

Kuma mijina zaisamu abinda yakeso insha Allah

Allah yakaimu gobe nashiga ukuna ni husnah wani irin zunubi na daukarwa kaina

Tabbas yaya Hakeem bai can canci wannan sakaiyar daga garaniba kayafemin Dan Allah duk da banasonka nayi alkawarin faranta maka kamar yadda kake faranta mana nida iyayena

Duk wannan maganar da husnah take yi tanayinsane itakadai

Hmmmmmmmm

Next page

Your comment is needed fan's. Love u all

Duk wacce bantaba bata page ba

Tayi comments mezafi next page natane 😘😘

📝📝📝📖📖📖
[05/05, 8:53 PM] UMMU  AFAN 🌹: 🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗🎗
🎗🎗🎗
🎗🎗
🎗
BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

Story & written
By
The  special writer

UMMU AFAN

🖊️🖊️🖊️🖊️🖊️🖊️📚

🌹FIRST CLASS TECHNOLOGIES WRITERS ASSOCIATION🌹

🌹🌹 (F.C.T.W.A)🌹🌹

🌹HOME OF QUALITIES AND TRUSTED WRITER'S OF THE NATION🌹

🎗️I DEDICATE THIS PAGE TO YOU BINTA ADAM (MAMAN IMAM) 🎗️COMMENTS DINKI YANA SANI SANI CEWA NIMA WATACE SO PLS KEEP IT UP
INA ALFAHARI DAKE 👏😘👍❤️

🎗️AKWAI LOKACI🎗️

🎗️PAGE 96 to 100🎗️

YAU take asabar daurin auren prof da husna

Wanda za adaura karfe uku na rana saboda bakin da zasuzo daga kasashen waje saudiya da sauransu
Duk Wanda baisamu yakaraso tun juma'a ba saboda wani uzirin

Shine aka daga daurin auren

Kuma a yaune ake kai  za akai lefe gidansu husna anasu aladarkenan

Mummy hafsat ce zaune cikin kawayenta matan mayan mutane
Da kuma 'yan uwa da abokan arziki

Kowa taganta yasan tana cikin farin ciki Mara misaltuwa

Ana ta kallon lefen Hakeem Wanda za akaima husnah anata yabawa

Mummyn Ahmad tace kafin atafi kai lefen yakamata akira uwargida tazo taga kaya ko

Mummy hafsat tace to akirasu mana
Dai dai lokacin Aisha matar Ahmad tashigo da daukar wayarta data saka caji Dan tunda aka fara hidam bikin nan agidan mummy take kwana

Mummy hafsat tace yauwa 'yar albarka mazaje kicewa su Laila suzo zuga kaya

Aisha tace to mummy tayi part din Hakeem  tashiga part din Laila

anan ta tarar da suby kanwar Laila da hajiya rukayya da hajiya suwaiba da ita Lailar kanta

Sai kuma kawayenta

Aisha ta gaishesu  bawanda ya kalleta  suby kanwar Laila ce tace dalla malama meyakawoki nan

Aisha tace to bani nakar zomom ba nima rataya akabani

Hajiya rukayya zatayi magana Laila tace yishiru kawai hajiya bake yakamata kimayar mataba

Suby tace kema anty bake yakamata kibata amsa ba nice dai dai da zamaninta

Aisha dadina da jaki duk yadda akayi da shi saiyaci kara

To nima bazuwan kaina nayiba mummy ce tace kuje kukaga kaya Dan za a wuce da shi

Tajuya tayi waje abinta
aikuwa Laila ta mulmulo zagi tabita da shi

Hajiya rukayya ta yi saurin rufe bakin Laila tace ai banso kukayi sainsa ba

Kunga idan muka ki zuwa ganin kayan zasuyi tunanin har yanzu akwai Abu akasa

Kunga kuwa ida suka gano mu ai akwai matsala

Dan haka ke Laila kidaure mutashi muje kinuna bakomai azuciyarki

Suby tace kuma fa hakane hajiya gaskiya kin iya taku mai kyau

Hajiya rukayya tayi murmushi tace kutsaya sanya yara

Nan sukayi part din mummy aikuwa ganin irin mutanen da suke cikin makeken falon daddy suncika shi dam

Duk wani dakuna na gidan suna cike da 'yanwan da kawaye dakuma makota

Wani katon bakiciki ya lullubesu su hajiya rukayya

amma Sai suka make

Hajiyar Ahmad tace sannu Ku da shigowa hajiya rukayya tayi taken dole

Idon Laila yakai kan wasu maka makan tsadaddun akwatuna tagani tsakiyar falon akalla zasu kai goma sha takwas

Nan Mummy hafsat tace kumatso kuga kayan mana nan suka shiga kallon aljan nar duniya duk akayan bakaramin zani

Karami aciki shine 25 thousand

Banda sarkoki masu tsadar gaske ga takalma da jakankuna suma awani jibgegen katon jaka aka narko su

Jakar kanshi abin kallone

Mummy Ahmad tashiga musu bayani kayan tace wannan shabiyun dakuka gani gefe shine Wanda ango yayi wannan kuma Wanda hajiya tayi ne

Hajiya rukayya da Laila suka hada ido

Tsaban bakin ciki sunkasa magana ma Dan haushi duk yadda sukayi kar agane su sunkasa

Mummy hafsat murmushi kawai takeyi tace wa hajiyar Ahmad Yakama ta kukai kayan nan lokaci karyawuce

Hajiyar Ahmad da wasu daga cikin kan nan mummy hafsat saiwata kawar mummy

Suka tafi kano kai kaya kuma suzasu dauko amarya

Laila kuka take sosai bayan sunkoma sashin su
Hajiya rukayya tace lalle hafsat tacika Mara mutunci kuma zan nuna mata nice gaba da ita aduniyar ma

Zata kwashi kashinta a hunu

Suby cikin bakin ciki tace ai ba ita kadai bace munafukar

Kinga dukiyar da ya kashe a lefen

Hajiya rukayya tace nashi shabiyu na hajiyar itama ta wa maryar shida

Kuma wallahi duk kayan ba na nan kasar

Suby tace wai wannan amaryar ma 'yar gidan uban waye ita da har suke rawar jiki akanta

Hajiya rukayya tace talakawa ne futuk  Dan a yadda nasa aka min bincikema gidan dasuke ciki shiya saya musu

Laila ta ce nashiga uku hajiya yaushe rabon Hakeem yabaki ko naira Dari ne
amma shine har da siyawa sirakanshi gida

gaskiya saina kashe yarinyar nan

Hajiya rukayya tace kedai  kidaure kawai musamu bukatar mu ta biya

Tana cin abincin nan fa shikenan

Taya zata ci abinci saikin nuna mata bakomai azuciyarki

Laila tace kodan burina yacika ma zanyi kokarin ganin komai ba komai bane

Suby tace wai fa harda mother's nigh mummyn Hakeem tahada

Hajiya rukayya tace munafuka ba kinsan dama tace Sai zaisake aure zatayi biki

*****
Umma da mutanenta suka hadu suna ta karbar bakin 'yan kawo lefe su hajiyar Ahmad kenan

Sosai sunji dadin karbar da aka yi musu daki guda  aka ware musu ga kayan ciye ciye nan burjik Sai Wanda suka zaba

Husnah kuwa tana nan zaune kan gadonta cikin wata kwalliya ta musamman Wanda aka dauko mai make up

Husnah tayi kyau shar da ita
Cikin wata rantsatstsiyar less
Golden colour ga sarkarta mai tsada shima

Anty kubra ce zaune gefenta da Aisha matar Ahmad Dan itama tabiyo masu kawo kaya

Aisha tace gaskiya Laila zatayi hauka idan taga husnah ce kishiyarta

Kubra tace kaman yaya

Aisha tace to ai banbanci  tsakaninsu a bayyane take

Wallahi kubra koni danake mace bana gajiya da kallon wannan tsadaddiyar amaryarmun

anty kubra tayi dariya tace gaskiya dai kam Husnah mace ce wallahi

Wani lokacin sainaji dama husnah bamai mata ta aura ba saboda gaskiya dayar zata iya cutuwa

Aisha tayi murmushi tace hakane kam Sai kuma Allah yasa itadin dai rabom ce

Husnah dai batace musu komaiba tana ta shashshekar kuka ne ma tunda dataga dai tabbas auran za amata

Wayar husnah tadau kara  ta tsinke bata daga ba

Aisha tasa hanu tadauki kiran
Tayi sallama Hakeem yace wacece Aisha tayi dariya tace ango kasha kamshi wato ma harkagane ba ita tadau wayarba
To Aisha ce

Hakeem yayi murmushi madam dakanta kenan yace ina babyn

Aisha tace gaskiya baccima take saboda ciwon kai
Yace what meyasa bata fada minma

Ganin nan zuwa
Aisha tace haba dai cikin matan zaka shigo yace mata ko iyaye da 'yanuwa

Naki wasane Ku kulamin da ita kafin nazo
Aisha tace Dan Allah kabari a daura saikazo kaga mutane sun ragu

Hakeem yayi murmushi yace kanki akeji

Ya kashe wayarshi

PROF yakalli Ahmad dasuke cikin tarin abokansu larabawa da turawa dama dai 'yan kasar baki daya

Yace zanje inazuwa yanzu Ahmad yace zakafara ko

Gaskiya ba Inda zakaje Sai andaura auran nan my sallami kowa

Hakeem yace kafahimceni wallahi ko na zauana bazaku gane kainaba
Idanba naje nadubo babyna naba

Ahmad yace aidai idan kayi hakuri gidanka za akaita yau ko

Duk yadda Hakeem yakai ga son zuwa gurin babynsa Ahmad yahana

Haka ya hakura kawai amma zuciyar nawurin amaryarsa

3 : pm dai dai aka daura auran PROFESSOR ABDUL HAKEEM ABUBAKAR SHUAIB DA AMARYSA

ASMAU SULAIMAN SHAMSUDEEN

Wanda yasamu hallartar duban jama'a suka shaida daurin auran

Ana gama daurin aure ango yafara gaisawa da mutane Wanda suke mushi fatan alkairi

Sosai yake tajida jama'a kansa yayi zafi sosai
Su daddy ma sun wuce Kaduna shida abokansa da kuma daddyn Ahmad

Da kyar Hakeem yasaci idon Ahmad yayi gidansu
Husnah

Yana zuwa gidan yakira wayar Aisha matar Ahmad

Yace please Aisha yaza ayi naganta

Aisha tace barin zo saikashiga ta falon kubra

amma fa Sai dai kashiga ciki Dan bacci take

Hakeem yace OK ganin nan zuwa

Yafita yashiga har dakin husnah anty kubra ta mishi sannu dazuwa suka gaisa kafin tafita itama

Ya kalli gefen da husna ke kwance

Hakeem yace baby meyasa baki fada min kanki naciwo ba

Tayi shiru yace OK bazakiyi maganaba dama zoben ki na kawo miki

Yana fadar haka Husnah tamike tace ina yake Dan Allah

Tashin datayi dasauri Hakeem yazuba wa kyakkyawa fuskarta ido
Shifa gani yake kulum karawa yarinyar nan kyau akeyi

Sosai tamishi kyau

Yace kinaso tace a Dan kabani

Hakeem yaci fuska yace  zoki karba

aikuwa husnah bata kawo comai a rantaba ta tashi taje gaban prof Dan dama ta kunce daurin da akayi mata gyalen ne kawai akan lallausar gashinkanta daya sha gyara  Sai kamshi yake fitarwa
Gata ita kanta wani kanshi take fitarwa na musamman

Tana zuwa kusa da Hakeem tamika hanu yabata bakin lallen da aka zana mata da ja Wanda yasha stone mai kyalli

Hanun nata yabida kallo
Husnah batayi tsammaniba   kawai tajita ajikin mutum ya rungumeta tsam ajikinshi  kaman zaimaida ita ciki

Tabude baki zatayi magana ya hada bakinsu guri daya

Tayi ta kokarin ta kwace kanta kar ashigo asamesu haka amma takasa
Dan  Prof namjin gaske ne

aikuwa bai kyaletaba Sai da yaji wayarsa tana kara  yanasaketa

Husnah tadurkushe agurin datake

Hakeem Ahmad yagani yake kiransa
Yadaga yace wai ya akayi  kuma Man

Ahmad yace wai Dan Allah ina kayi

Hakeem yayi wani murmushi kaman Ahmad nakallonshi
Yace ganinan ina tare da matata

Ahmad  kai amma wallahi baka da kyau yanzu Sai da kaje zaka samusu yarinya agabako

Anya kuwa prof zakabari sukawo maka itakuwa

Hakeem yafashe da dariya yace gaskiya dai daza a mun adalci da anbani matana munwuce

Ahmad yace lalle angon karshen zamani

To Dan Allah yafito su shek zasu koma kuma suna son kuyi sallama

Hakeem yace OK gani nan zuwa amma fa kan katse min hanzari wallahi

Ahmad yayi dariya yace to sabonshiga

Suka kashe wayar gabadayansu

Husnah kuwa tunda ta durkushe agaban prof takasa tashi

Tayi tayi ta tashi Amman takasa saboda bakon alamarin da prof yazo mata da shi

Jikinta bari yake sosai Dan wani tsoron prof nema yakamata

Shima durkushewa yayi gabanta yakamo hanunta yazura mata zobenta

Kafin kuma yadago habanta suka hada ido Husnah tasaukar da nata kasa

Hakeem yace I love you baby
Kikula min da kanji kinji ko

Bata dai bashi amsa ba saboda kunyarsa datakeji

Ya manna mata kiss a goshi
Ya tashi zai bude kofar kenan husnah tayi cewa Dan tsaya Dan Allah batareda ta kalleshiba tayi maganar

Cikin mamaki Prof yajuyo yazuba mata ido ta tashi tadauko hankacif tabashi  batare da tayi magana ba

Tanuna mishi madubinta

Bai ce komaiba yakarasa gaban dressing mirror dinta

aikuwa jambaki yagani duk lebensa da kumatunsa

Murmushi yayi Wanda yakara wa husnah tsoron shi

Ya goge kafin yajuyo yakamota yace meyasa bakya son  nafita ahaka
Kowa yasan daga wurin matata nafito kobahaka bane

Kuma ma wannan dadewar danayi agunki kowa yasan hakan saiya faru

Husnah tadago fuskarta ta kalleshi kaman zatayi kuka
Tace yanzu harsu umma ma sun San hakan

Hakeem yayi murmushi yace duk Wanda ke cikin gidan nan Sai yayi zaton haka
Toke meye na damuwa mijinkine fa

Husnah tace nashiga ukuna Dan Allah kafita karsu shigo

Hakeem yace inzan kwana anan bamai shigowa kowa yasan ina ganawa da matata ne

Husnah kuka ya gangaro mata
Tace wayyo Allah na Hakeem yace matso kusa da ita shima zaman yayi bakin gadon hawayenta tas saida goge mata su da harshensa

Yace bana son nasake ganin kuka a wannan kyakkyawar fuskar

Ya tashi ya wuce yabarta da kunya
Dan idan duk ansan meya mata ai tashiga uku da wani idon zan kallesu ni husnah

Ganin fitan Prof yasa su anty kubra suka shigo dakin

Anty kubra ta kalli husnah data kasa hada ido dasu

Kubra tace har yafita kenan tanafada tana dariya
Husnah tasaukar da kai kaman munafuka

Aisha tace kai anty kubra wannan sa ido haka

Anty kubra tayi dariya kitashi yanzu za ashigo asake miki make up saboda yanzu za awuce dake

aikuwa husnah ido yayi rau rau jin za a wuce da ita

Anty jumai mai gyaran amarya tazo tadauki husnah suka wuce zuwa bedroom din umma anan za amata kwalliyar tafiya gidan angon

Aisha ta kalli kubraa tayi dariya tace wallahi na tausaya wa Husnah Dan daga ganin yadda Prof yake bare bare akanta basauki

Anty kubra tace ai wallahi naga alama
Sai dai muce Allah raba lafiya Dan nan da wata Tara suna zamu je Kaduna

Kuma gaskiya husnah tayi dacen miji Allah yacika wa yayanta burinshi

Kullum acikin addua yake Allah yabawa husnah mijin da zai kaunaceta tsakaninshi da Allah

Aisha tace aikuwa dai addu'arshi taci
Dan professor Hakeem badaga nan ba wallahi

Bayan angama gyara amarya tafito tayi shar daita

Anty jumai ta kamota zuwa falonsu anan umma takara  mata fada sosai tareda mata gargadi takula da ibada addua

Umma saidatayi kukan rabuwa da 'yatata guda daya
Abinda yasake ba husnah kuka kenan ma

Sosai sukayi kuka da kyar aka rabasu

Ya shamsu shiya rakata har mota

Kafin yamata rada a kunne
Saiga husnah tana murmushi da haka su hajiyar Ahmad suka shiga mota tadaga zuwa Kaduna

ankai amarya bangaren mummy hafsat aka ajiyeta sai dare za amikata sashenta

Karfe takwas  na dare akafara mother's night sosai Mummy hafsat tayi  barin kudi Dan bakaramin kudi  daddyn Hakeem da Hakeem dinkansa suka kashe mata ba

Anci ansha ansa albarka
Washagri kuma walima aka yi namaza daban na mata daban

Inda aka gayyato manyan malamai nakasa  dama kasashen ketare

Karfe Tara na dare aka mika husnah sashin uwargida

Da kyar ta danne zuciyarta duk da bata ga fuskar amaryarba saboda tana cikin lullubi

Mummy hafsat dakanta taraka husnah zuwa part din ta darakiyarsu anty kubra da Aisha matar Ahmad

Sai datasa husnah tayi addua sannan kuma tashiga  dakinta da kafar dama

Har bedroom dinta akaita  mummy tazaunar da ita bakin gado

Kafin nan tace wasu anty kubra sutayata hira

Mummy tamusu Sai dasafe tafita zuwa part din ta

*****

MEENAT  zaune abi duniya yadameta
Wai yau ake auran babana dawata 'yar iskar

Gashi kwatata bata gane kan bash
Abinda yakemata duk ya daina shi bazai yi hira da ita

Sai takama tarasa meke shirin faruwa da itane

Mummy bash takasa gane kan yaronta tunda aka yi auran

Dan ita dama ba ason ranta yafasa auran husnah ba

Kawarta ce tabata shawarar tsayawa da addua Allah ya karkato mata da kan danta lafiya

Sadaka gidan marayu gajiyayyu bainda bata kai sadaka

Ga azumi datake

Cikin ikon Allah kuwa addua tasoma karbuwa

Dan jiya wuni bashir yayi waya da 'yan uwansa

Meenat takalli bashir tace uncle yashe zamu zamu koma gidane tunda  har gashi mun wuce lokacin damuka tsara

Bash yace Sai lokacin danaga dama zata sake magana ya daga mata yace ya isa bana son surutu shasha kawai wuce kibani guri

Da gudu meenat tayi bedroom tafara kuka tace nashiga ukuna kar dai bash yadaina sona

Abinda zai burgeku daya ne Ahmad da ya shamsu sune suka rako Hakeem dakin amarya

Ya shamsu yayi addua kafin kuma yamike tsam ya kalli kubra madam muwuce ko

Ta tashi Aisha ganin Ahmad yatashi suka fito atare Hakeem yarakosu har gate

Husnah tana ganin fitansu ta tashi tasawa kofarta key a kofarta
Tayi bedroom dinta ma tasa key

Next page

Your comments is needed Fan's

Much love to your comments😘👏🎗👍

📝📝📝📖📖📖